# KWATANTA JIGO DA ZUBI DA TSARIN WAQOQIN BELLO MUHAMMADU AJI MAI KARAMA DA NA SANI ABUBAKAR HOTORO

**DAGA**

**UMAR FAROUK YAHAYA**

**SPS/15/MHA/00014**

**KUNDIN BINCIKE WANDA AKA GABATAR DOMIN CIKASA WATA QA'IDA TA NEMAN DIGIRI NA BIYU A FANNIN ADABIN HAUSA (M.A. HAUSA) A SASHEN KOYAR DA HARSUNAN NIJERIYA JAMI'AR BAYERO, KANO**

**2021**

## Shafin Tabbatarwa

Na tabbatar da cewa wannan binciken da na gabatar mai suna “Kwatanta Jigo da Zubi da Tsarin Waqoqin Bello Muhammadu Aji Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro” ni ne na rubuta shi da kaina, bisa jagorancin Farfesa Isa Mukhtar. A iya sanina ba a gabatar da wannan bincike a wani wuri ba, kuma babu niyar sake gabatar da shi a wani wuri domin neman shaidar kammala wani karatu a nan gaba.

______________________________

**UMAR FAROUK YAHAYA**

**SPS/15/MHA/00014**

**Shafin Shaidawa**

Na shaida cewa wannan bincike da Umar Farouk Yahaya SPS/15/MHA/00014, ya gabatar, an gudanar da shi ne bisa jagorancina.

Farfesa Isa Mukhtar

Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya

Jami'ar Bayero, Kano

Jagoran Duba Aiki

Dr. Ibrahim Garba Satatima

Shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya,

Jami'ar Bayero, Kano

## Shafin Amincewa

Wannan kundin bincike ya samu dubawa da tantancewa tare da amincewar waxannan malamai.

______________________________

Farfesa Isa Mukhtar
Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya
Jami'ar Bayero, Kano
Jagoran Duba Aiki

______________________________

Dr. Jibril Shu'aibu Adamu
Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya
Jami'ar Bayero, Kano
Mai Duba Aiki na Ciki

______________________________

Farfesa Magaji Tsoho Yakawada
Sashen Koyar da Harsuna da Al'adun Afirka,
Jami'ar Amadu Bello, Zariya
Mai Duba Aiki na Waje

______________________________

Dr. Ibrahim Garba Satatima
Shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya,
Jami'ar Bayero, Kano

## Sadaukarwa

Na sadaukar da wannan aiki ga iyayena Malam Yahaya Inuwa da Malama Ruqayya Yahaya, Allah ya saka musu da gidan Aljanna mafificiya.

## QUNSHIYA

Shafin Tabbatarwa……………………………………………... ……ii
Shafin Shaidawa ……………………………………………...……iii
Shafin Amincewa ……………………………………………... ……iv
Sadaukarwa ………………………………………………......……..v
Qunshiya ………………………………………………..…………vi
Godiya ……………………………………………………............ix
Gabatarwa ………………………………………………...............xvi
Abstract ………………………………………………….....…...xx
Tsakure …………………………………………………………xxi

**BABI NA XAYA**
**SHARAR FAGE**

1.1 Gabatarwa ……………………………………..…………….1
1.2 Dalilin Gudanar da Bincike ……………………..……………..1
1.3 Manufar Bincike. …………………...…………………..……...2
1.4 Hasashen Bincike ………………...……...............................2
1.5 Tambayoyin Bincike……………………...……………...….3
1.6 Iyakar Bincike …………………………..…………………...3
1.7. Gudummuwar Bincike…………………………………………3
1.8 Tarihin Bello Muhammad Aji Mai Karama ………..……………4
1.9 Tarihin Sani Abubakar Hotoro…...………………..…………...…7

**BABI NA BIYU:**
**BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA**

2.1 Gabatarwa……………………………………...……......10
2.2 Ma'anar Jigo……………………………………...……......10
2.2.1 Furucin Gundarin Jigo/ Qwayar Jigo………………..………10
2.2.2 Jigo a Gajarce……………………………………..……10
2.2.3 Warwarar Jigo da Shimfixarsa…………………………………11
2.3 Ma'anar Zubi da Tsari………………………..……………....11
2.3.1 Zubi da Tsari na Gaba Xaya…………………………………....11
2.3.2 Zubi da Tsari na Cikin Baitoci…………………………………11
2.3.3 Karin Waqa/ Aruli……….…………………………………….12
2.3.4 Gangara..…..……………………………………………..…12
2.3.4.1 Gangara ta Gaba………………………………………...13
2.3.4.2 Gangara ta Baya………………………………………...13
2.3.4.3 Gangarata Tsakiya……………………………………....13
2.3.5 Savi-zarce ……………………………………………...…13

2.3.5.1 Savi-zarce na Gaba …...………………………………...….14
2.3.5.2 Savi-zarce na Tsakiya……………………………………..14
2.3.5.3 Savi-zarce na Baya……………………………………...…14
2.4 Ma'anar Kwatantawa………………….......................….15
2.5 Kundayen Bincike da Bugaggun Littatafai da Kuma Mujallu da Sauran Takardu…………………………………………………..15

**BABI NA UKU**
**RA'I DA HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE**

3.1 Gabatarwa……………………………………………………..29
3.2 Ra'in da aka Xora Binciken a kai..……………………….…….. 29
3.3 Hanyoyin Tattara Bayanai …………………………………....31
3.3.1 Tattaunawa da Marubuta da Masu Alaqa da su…...…………..31
3.3.2 Tattaro Wasu Waqoqin Marubutan……………...…………31
3.3.3 Karanta Waqoqin Marubutan……………………...………..32
3.3.4 Ganawa da Masana a Fannin Adabin Hausa…………….….32
3.3.5 Ziyara…..…………………………………...……....... 32

**BABI NA HUXU**
**KWATANTA WAQOQIN BELLO MUHAMMAD AJI MAI KARAMA DA SANI ABUBAKAR HOTORO**

4.1 Gabatarwa..…………………………………………………….34
4.2.1 Jigo ……...……………………………………………………..34
4.2.2 Jigon Yabo…..………………………………………………..34
4.2.3 Jigon Nasiha……...…………………………………………….43
4.2.4 Jigon Gargaxi…...……………………………………………..49
4.2. Jigo a Gajarce..…………….……………………..…...…….54
4.2.6 Warwarar Jigo da Shimfidarsa…...…………………...……….59
4.3 Zubi da Tsari na Gaba Xaya..……………………….....……64
4.3.1 Zubi da Tsari na Cikin Baitoci…...…………………………....68
4.3.2 Gangara …...…………………………………...…………72
4.3.2.1 Gangara ta Gaba……………………………………………...…73
4.3.2.2 Gangara ta Baya…………………………………...………….78
4.3.2.3 Gangara ta Tsakiya……………………………………………...81
4.4.1 Savi-zarce.……………………………………………………84
4.4.1.1 Savi-zarce na Gaba ………………………………………….... 86
4.4.1.2 Savi-zarce na Tsakiya……………………………………..88
4.4.1.3 Savi-zarce na Baya……………………………………………..89
4.5 Jirkinta Faxar Sakamako……………………………….…….... 91
4.6 Kari/Aruli…….…………………………………………...…93

**BABI NA BIYAR**
**KAMMALAWA**

5.1 Gabatarwa…..……………...…...………………..…..…...….96
5.2 Taqaitawa ……………...………………………...………….96
5.3 Sakamakon Bincike………..………………..…………..…...……98
5.4 Matsalolin…………………………………………..…..………99
5.5 Shawarwari ……………………………………….....…….99

Manazarta…………..…………………………….……………...101
Mutanen da ak yi Hira da su…………………………………….…..109
Rataye Xaya:
Sumfurin jerin Tambayoyi…..…………….……………………..110
Rataye Biyu:
Wasu Waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama.........................112
Rataye Uku:
Wasu Waqoqin Sani Abubakar Hotoro…………………………..…137

## Godiya

Yabo da godiya sun tabbata ga Allah maxaukakin Sarki, tsira da aminci su qara tabbata ga shugabanmu jagoranmu abin faharinmu Annabi Muhammadu,Sallalahu Alaihi Wasallam, tare da alayensa da sahabbansa da kuma duk wanda suka tsaya a kan gaskiya har zuwa ranar gobe qiyama.

Da farko ina miqa godiya ga malamina kuma jagoran gabatar da wannan aiki wanda ya yi xawainiya da ni wajen duba wannan aiki, shi ne, Farfesa Isa Mukhtar, bisa yadda ya yi haquri da ni, safe da yamma, wajen duba wannan aiki ba tare da gajiya ba. Allah ya saka masa da mafificin alheri, ya biya masa buqatunsa duniya da lahira.

Sannan ina miqa godiya ta ga jagoran duba aiki na ciki, wato Dr. Jibril Shu'aibu Adamu saboda samun damar sake bitar wannan aiki gaba xayansa, tare da daxa inganta shi da fito da wasu gyare-gyare da shawarwari. Allah ya saka masa da alheri.

Sannan ina qara godiya ga jagoran duba aiki na waje Farfesa Magaji Tsoho Yakawada, saboda sake bitar wannan aiki da fito da muhimman gyare-gyare waxanda suka qara inganta aikin. Malam ina godiya, Allah ya saka da alheri, ya albarkaci zuriya, Allah ya qara lafiya.

Haka kuma ina miqa godiyata, musamman ga Shugaban Sashen Koyar da Harsunan Nijerya, Dr. Ibrahim Garba Satatima.Sannan kuma ina miqa godiya ta ga marubutan da na yi nazarin waqoqinsu Alhaji Bello Muhammadu Aji MaiKarama Giginyu da Sani Abubakar Hotoro. Allah ya qara musu basira da baiwa da hazaqa, ya sa su gama da duniya lafiya.

Har ila yau, ina gode wa dukkan malaman Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya, musamman na wannan makaranta mai albarka wato, Jami'ar Bayero, Kano, waxanda suka haxa da: Emertus Farfesa Abdulqadir Xangambo da Farfesa

Sa'idu Muhammad Gusau da Farfesa Ahmad Bello da Farfesa Usman Usaini Fagge da Farfesa Aliyu Mu'azu da Farfesa Yakubu Magaji Azare da Dr. Ahmad Magaji da Dr. Aminu Lawal Auta da Dr. Muhammad Tahar Adamu (Baba Impossible) da Dr. Murtala Garba Yakasaida Dr. Umma Ado Abbas da Dr. Umma Aminu Inuwa da Dr. Halima Abdulqadir Xangambo da Dr. Maryam Mansur Yola da Dr. Anas Sa'idu Muhammad da Dr. Jibril Shu'aibu Adamu da Dr. Muhammadu Ammani da Dr. Muhammad Sulaiman Abdullahi da Dr. Nura Lawal da Marigayi Farfesa Mu'azu Sani Zariya (Allah ya jiqansa, ya yi masa rahama) da kuma Marigayi Dr Habibu Sani Vabura (Allah ya jiqansa, ya yi masa rahama) da sauran dukkanin ma'aikatan wannan Sashe. Na gode, Allah ya saka musu da alhairansa duniya da lahira.

Sannan ina qara miqa godiyata ga Dr. Muhammad Tahir Rabi'u da Dr. Sulaiman Adamu Sarvi, na Sashen Koyar da Harsuna da Al'adun Afirka, Jami'ar Amadu Bello, Zariya saboda gudummuwar da suka ba ni.

Godiya mai yawa ga dukkanin abokan karatuna waxanda muka yi ta faxi-tashi tun daga kan waxanda muka yi karatu a matakin firamare har zuwa wannan lokaci da nake ciki musamman Xahiru Hussaini Sankalawa da Hassan Muhammad da Musa Abubakar Kurawa da Jamila Sa'id Muhammad da Hussaini Isa Muhammad daAisha Aminu Yahaya da Qamariyya Abdullahi Adam da Ali Wada da Jabir Barau da Faharuddeen Habibu Isa da Ali Muhammad Ali da Garba Yusif da Ali Musa da kuma Lawan Sani Daura da Salisu Rabe da Salisu Yusif da Mahmuda A. Baba da Nura Musa da Ibrahim Ghali da Shafi'u Adamu Tazame da kuma Ziya'u Muhamma da sauransu, bisa gudummawa da shawarwari da addu'o'i da na samu daga gare su a yayin gudanar da wannan bincike. Allah ya saka masu da alherinsa.

Sannan ina miqa godiyata ga malamaina da kuma da abokan aikina na Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano kamar irinsu: Dr. Kabiru

Gwarzo, Mataimakin Shugaban Qwalejin,da (Sub Dean) Mal Sani Magaji Abubakar da Dr. Mahe Isa Ahmad, Shugaban Sashen Koyar da Hausa, da Dr. Bilkisu Yusuf Hassan da Malam Nura Baba da Malam Magaji Ahmad Gaya da Dr. Umar Yahaya da Malam Garba Yakubu da Malam Babangida Magaji Isa da Malama Maryam Habu Hausawa da Malama Halima Isma'il, da sauran malaman Sashen da Tsangaya da kuma Qwaleji gaba xaya.Sannan ina gode wa matata da kuma 'ya'yana dukkansu, Allah ya saka musu da alheri.

Daga qarshe ina miqa godiya ga duk waxanda ban faxi sunayensu ba kamar 'yan'uwana, ba manta wa na yi da su ba, dukkaninsu Allah ya saka musu da mafificin alheri, ya haxa fuskokinmu baki xaya ranar gobe qiyama.

## Gabatarwa

Wannan bincike ne da ya shafi nazarin rubutacciyar waqa, inda aka duba rubutattun waqoqin marubuta guda biyu. An gudanar da binciken ne a kan jigo da zubi da tsari. Saboda ganin irin tasirin da jigo da zubi da tsari suke da shi a cikin waqoqin, wanda za a iya cewa kusan su ne abubuwan da suke da tasiri a wajen fahimtar saqon marubuci.

Haka kuma hanyoyi ne na fahimtar yadda marubuci yake amfani da qwarewa da yadda yake saqa tunaninsa da kuma isar da saqonsa ga al'umma. Binciken ya yi nazarin rubutattun waqoqi na Bello Muhammad Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro, don ganin an fito da irin basirarsu da kuma hazaqa da suke nuna wa a wajen rubuta waqoqi.

Dalilin da ya sa aka zavi a yi wannan nazari, shi ne an fahimci cewa waxannan marubuta suna da waqoqi da suka gabatar waxanda za su qara bunqasa harshen Hausa. Sannan suna da waqoqin da suke da jigon faxakarwa da na yabo da kuma na nasiha da sauransu.

Allah ya yi musu fikira ta saka abubuwa a cikin waqoqinsu, kamartsari mai sauqin fahimta da amfani da amsa - amo marar karyewa, sannan da amfani da wani salo na saka sunayensu duk a cikin waqoqinsu. Wannan ya sa aka ga ya dace a yi amfani da waqoqinsu don nazartarsu.

Don haka, kamar yadda aka saba tsara kowane kundi na bincike, shi ma wannan an karkasa shi zuwa babi-babi har guda biyar. A babi na xaya an yi sharar fage da suka haxa da dalilan bincike da manufar bincike da iyakar bincike da gudummawar bincike da kuma taqaitaccen tarihin marubutan.

A babi na biyu ne aka kawo irin ayyukan da aka yi bita waxanda suke da makusanciyar alaqa da wannan bincike, tun daga ma'anar kalmomi da aka yi amfani da su wajen yin nazarin. Haka kuma an dubi kundayen digiri na xaya zuwa na uku (1-3) da bugaggun littattafai da muqalu da sauran takardu na ilimi, don qara

ba da haske da kuma sanin abubuwan da aka yi ba, da waxanda ba a yi, da sanin yaya yakamata a gudanar da wannan binciken.

Babi na uku shi ne ya bayyana ra'i da hanyoyin da aka bi wajen gudanar da binciken waxanda suka haxa da tattaunawa da kuma ganawa da ziyartar xakunan karatu domin yin bitar ayyukan magabatada tattaunawa da masana da manazarta.

A babi na huxu ne aka yi nazarin jigo a waqoqin Bello Muhammadu Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro, inda aka duba abubuwan da suka haxa da jigo da furucin gundarin jigo da jigo a gajarce da kuma warwarar jigo. Haka kuma an duba zubi da tsari na waqoqin, waxanda suka haxa da zubi da tsari na gaba xaya da zubi da tsarin cikin baitoci da yawan baitoci da xango a waqa da karin waqa da amsa-amo da kuma gangara da savi-zarce. Har ila yau an yi kwatanci ta hanyar duba waqoqinsu, don duba yadda suke nuna qwarewa da fasaha cikin waqoqin, musammam a wajen fito da abin da ya shafi jigo da zubi da tsari.

Babi na biyar shi ne ya haxa da sakamakon bincike da shawarwari da kuma kammalawa. A qarshe an kawo manazarta, da mutanen da aka yi hira da su, an kuma kawo samfurin tambayoyin da aka yi a wajen samo bayanai. Haka kuma an kawo ratayen wasu waqoqin Bello Muhamamdu Aji Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro da aka yi nazari a cikinsu.

**Abstract**

This thesis, titled "Comparative Analysis of the Theme and structure of Selected Poems of Bello Muhammadu Aji Mai Karama and Sani Abubakar Hotoro", adopted Xangambo's (2007) model of comparison, and Brandes, G. (1997) Comparative Theory which underscores the combined study of similar literary works which stresses the points of connection between literary products of two or more cultures. The study presented the biographies of the poets and then compares their poetic works. The paper also discovered the styles and techniques that the poets employ in expressing their messages to audience. In the course of the comparative analysis, similarities and differences between the poets in terms of thematic focus and stylistic creativity are highlighted. The study discovers that the poets differ in their speech and rhyme; Mai Karama cites Qur'anic verses in their Arabic form but Sani cites in verses Hausa Language. It is also observed that the poets mention their street/district names in their poems. This work is opportune to be the first in this area. Finally, the poems are attached to this study as appendices.

# Tsakure

Wannan bincike mai suna "Kwatanta Jigo da Zubi da Tsari Waqoqin Bello Muhammadu Aji Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro" ya qunshi nazari a kan rubutacciyar waqa, sannan an yiamfani da ra'in Xangambo (2007), sannan Nazarin ya yi amfani da ra'in Brandes, G. (1997) Kwatanta Adabi wanda ake amfani da shi wajen kwatanta adabin al'ummomi waxanda ake ganin suna da wata dangantaka ko kuma wasu kamanni a wasu vangarori na adabi ko al'adu domin a tabbatar da alaqarsu. haka kuma an kawo tarihin marubuta. Sannan a cikin aikin an kwatanta waqoqin waxannan marubuta an gano hanyoyi da dabarun da marubutan suke amfani da fasahohin su wajen isar da saqonnisu ga jama'a, a kuma binciken an kwatanta jigo da zubi da tsarin waqoqinsu an fito da inda suka sami kamanci da kuma bambanci. Inda aka gano marubutan sun sha bamban wajen furucin gundarin jigo da kuma zubin da suke bi, Mai Karama yana amfani da ayoyi cikin Harshen Larabci, amma Sani sai dai ya kawo aya cikin harshen Hausa, haka kuma an lura da wani zubi wajen bayyana sunayen ko unguwanninsu a cikin waqoqinda kuma sauran abubuwa da binciken ya gano. Sannan bincike ya samu nasarar taskace wasu waqoqin waxannan marubuta inda ba a samu wasu manazarta da suka yi haka ba, kafin wannan. Daga qarshe kuma an kammala aikin tare da kawo rataye na waqoqin.

# BABI NA XAYA
# SHARAR FAGE

## 1.1 Gabatarwa

Wannan babi ya yi bayani ne a kan dalilan bincike da manufar bincike da gudummawar bincike da tambayoyin bincike da iyakar bincike da hasashen bincike, sai kuma tarihin Bello Muhammad Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro.

## 1.2 Dalilin Gudanar da Bincike

Dukkan wani abu da ake gudanarwa a rayuwa yana da dalili ko dalilai da suke sawa ake gudanar da shi. Akwai dalilai da dama da suka sa gudanar da wannan bincike, kamar haka:

1. Bello Muhammadu Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro marubuta waqoqi ne da suka shahara a wannan lokaci, amma duk da haka nazari guda xaya aka samu kawai a kan Bello Mai Karama wanda Yahaya, (2014) ya gabatar, a kan amfani da ayoyin*Alqur'ani* a wasu waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama. Wannan dalili shi ya ba da damar a kwatanta jigo da zubi da tsarin waqoqin waxannan marubuta guda biyu, domin ganin an yi amfani da fasaharsu a matsayinsu na marubuta waqoqi, da kuma irin gudumawar da suke bayarwa don qara bunqasa wannan fage na nazarí, musamman a vangaren da ya shafi adabi.

2. Sha’awar da nake da ita ta karanta waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro sai na ga akwai buqatar a kwatanta jigo da zubi da tsari na waxannan marubuta, domin qarfin guiwa ga masu sauraro da kuma masu son yin nazarí a nan gaba musamman na kwatanci da bambance-bambancen da ke tsakaninsu.

## 1.3 Manufar Bincike

Muhimmiyar manufar wannan bincike ita ce yin nazarin jigo da zubi da tsarin waqoqin Bello Muhammadu Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro da nufin gano wuraren da aka sami kamanci ko kuma bambanci.Saboda waqoqin za su qara havaka fanin adabi, da kuma qara sanya sha’awa ga masu nazarí.

Haka kuma wata manufar ita ce ta kara fito da aikace-aikacena fili,ta hanyar adana waqoqinsu don gudun vacewa.

## 1.4 Hasashen Bincike

Babu shakka, kafin a shiga cikin aikin gadan-gadan ya kamata a kalli irin abubuwan da mai bincike yakan iya hange ko tsinkaye na abin da yake tsammanin samu yayin kammala bincikensa. Don haka, a wannan nazari ana hasashen samun sakamako kamar haka:

1. Fito da tarihin Bello Muhammad Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro
2. Kwatanta waqoqin marubutan guda biyu, har a samo bambanci da kamanci da ke tsakaninsu ta fuskar jigo da kuma zubi da tsari.

## 1.5 Tambayoyin Bincike

Daga cikin tambayoyin da wannan bincike yake neman amsa akwai:

1. Su waye waxannan marubuta?
2. Yaushe suka fara waqa?
3. Shin jigon wani marubuci zai iya zama iri xaya da na wani marubucin?
3. Za a iya kwatanta jigo da zubi da tsari a waqoqin marubuta guda biyu?

## 1.6Iyakar Bincike

Wannan bincikeya taqaita ne a kan kwatanta jigo da zubi da tsari, domin nazartar waqoqin zai taimaka wajen bunqasa adabi da samar da wasu waqoqin don adana su tare da taskacesu daga qalubalen zamani.Anyi amfani da waqoqin marubutan guda goma sha takwas (18) domin fito da jigo da kuma zubi da tsarinsu.

## 1.7 Gudummuwar Bincike

Daga cikin gudummawar wannan bincike akwai:

1. Adana ayyukan waxannan marubuta.
2. Qara havaka fagen rubutattun waqoqi, da wasu daga cikin waqoqinsu, ta hanyar nazartar jigo da kuma zubi da tsarinsu.
3. Zama jagora a nan gaba ga masu bincike a wannan fanni na nazarin jigo da zubi da tsari.

### 1.8 Tarihin Bello Muhammad Mai Karama

Asalin sunan marubucin shi ne Bello xan Muhammadu Aji Ahmad xan Abubakar xan Abdullahi[1]. Vangaren mahaifiyarsa kuma Bello xan Habiba 'yar Isyaku. An haife shi a shekarar 1972 ranar Juma'a, bayan tsohuwar tasha, qaramar hukumar Mubi a cikin Jihar Adamawa. Bello ya rasa mahaifinsa tun yana xan shekara goma 10. Haka yasasai mahaifiyarsa ta dawo da shi Kano wajen 'yan'uwanta.

Marubucin ya yi makarantun addini da na zamani. Tun yana xan shekara uku zuwa shekara huxu ake zuwa da shi makarantar allo ta Malam Bala Babarbare a garin Mubi, to amma bayan sun dawo Kano an sashi a wata makarantar Islamiyya mai suna *Miftahu Ibadat Wildan*[2] a Unguwar Giginyu, layin Baba Sharu inda ya sami iliminsa na *Alqur'ani* da na littatafan ilimi da dama. A wannan makarantar ya sami damar haddace wani abu daga cikin *Alkur'ani* mai girma qarqashin jagoranci marigayi Malam Lawal Muhammad Giginyu. Dalilin samun laqabin Mai Karama shi neya kasance watan Maulidi ya kama, sai aka ba shi qasida ya karanta. Bayan ya gama karantawa ne,sai marigayi Aqilu Aliyu[3] ya ce "lalle wannan yaro shi ne mai karama". Daga nan ne ya samu sunan. A vangaren ilimi zamani kuwa, marubucin ya fara makarantar firamare ta *Race Course Special*da ke kan titin

---

[1]Marubucin ya bayyana haka ne a gidansa da ke Unguwar Giginyu. Ranar 22/10/2017, da misalin qarfe 5:17 na Yamma.

[2] Islamiyya ce ta koyar da addinin Muslumci, wacce Malam Lawan Muhammad ya kafa a shekarar 1985, a Unguwar Giginyu

[3] Marubucin waqoqi ne, an haife shi a Jega ta qasar Gwandu.

Ahmad Bello, da ke, unguwar Turawa a Nassarawa[4] (Nasarawa G.R.A) Kano, a shekarar 1985.

Bayan nan ya yi makarantar sakandire ta G.S.S. Tarauni, a shekarar 1991 zuwa 1997, wannan vangaren ilimin zamani kenan.

Babbar sana'ar marubucin ita ce aikin kafinta, yana da shago a unguwar Giginyu, layin Baba Sharu a kofar gidansa.

Waqar da ya fara ta farko ita ce *Na so Manzanka*, a shekarar 1992, inda ya fara karantata a makarantar*Miftahu Ibadat Wildan*. Mai Karama ya kasance xaya daga cikin marubuta, wanda ya riqe shugabanci da kuma zama xanwasu qungiyoyi da suke Qaramar Hukumar Nassarawa[5] inda ya zama shugaban *Majalisar Sha'irai*[6] ta Nassarawa wacce take Karamar Hukumar Nassarawa, sannan kuma xan*Gidauniyar Tallafin Sha'irai*[7]da Qungiyar*Rasulullah Akram*[8] da Qungiyar *Haxa kan Madihan Nassarawa*[9]. Haka kuma Shugaban *Shabbabu Rasulullah* Giginyu[10], kuma xaya daga cikin waxanda suka kafa Qungiyar *Kawakibu* ita ma a Unguwar Giginyu, kuma shi ne Shugaban *Lajnatul Islam*[11]ta jihar Kano.Waxannan su ne kaxan daga cikin qungiyoyin da Mai Karama ya yi. Sannan marubucin yanzu

---

[4] Unguwa ce da take cikin birnin Kano, wacce Turawa suka zauna a cikinta.
[5] Xaya daga cikin qananan hukumomin da suke cikin birnin Kano.
[6] Qungiya ce da aka kafata a shekarar 2010, domin haxa kan marubuta waqoqi na Nassarawa ta kudu.
[7] Qungiya ce da take tallafawa marubuta waqoqi, idan an yi musu haihuwa ko biki, an kafa ta a shekarar 2012.
[8] Wannan qungiya an kafa ta a Unguwar Giginyu, wacce ta haxa marubuta waqoqin na Unguwar, an kafa ta a shekarar 2006
[9]Ita ce qungiyar da ta haxa marubutan da suke cikin qaramar hukumar Nassarawa, an kafa ta a 2003.
[10]Ita wannan qungiyar ta dade an kafa ta a 1989, sannan Bello Muhammad Aji shi ne Shugabanta.
[11] Qungiya ce ta qasa, amma a reshen ta na jihar Kano Bello Muhammad Aji shi ne Shugabanta, an kafa ta a shekarar 2015.

duk yana cikin waxannan qungiyoyi ban da Qungiyar *Haxa kan Madihan Nassarawa*ita ya barta.

Marubucin ya rubuta waqoqi da dama waxanda shi kansa bai san yawan su ba. Saboda haka, waqoqin da za a duba suma marubucin ya yi su ne a lokuta da dama. Marubucin ya yi waqoqi da dama kaxan daga cikinsu su ne:

1. Cetonsa (1993)

2. *Khatimul Ambiya'i* (1995)

3. Cikar Buri (1997)

4. Girman Kai (1999)

5. Ranar Murna (2004)

6. *Ramadaniyya* (2005)

7. Sha Rubutu (2009)

8. Shika-shikan Musulunci (2010)

9. Gane Gaskiya (2012)

10. Koyar da Ibada (2013)

11. *Wasilah* (2014)

Waxannan su ne kaxan daga cikin waqoqin marubucin kuma daga cikinsu za a xauki guda tara. Don a nazarce su, musamman ta yin amfani da fasahar marubucin da fasahar da ke cikin su, don fito da jigo da yadda yake zubi mai jan hankalin mai sauraro. A qarshen wannan binciken ana sa ran za a sami fito, da jigo

da kuma zubi da tsarin marubucin ta amfani da nazarin da aka yi a cikin waqoqinsa. Mai Karama yana da halifofi, waxanda shi ya naxa su, wato: Mubarak Idris Alqadiri (Halifa) da kuma Yahaya Isa, waxanda su ne suke yin waqoqin da yake yi wani lokaci.

### 1.9 Tarihin Sani Abubakar Hotoro

Sani Abubakar shi ne asalin sunansa, mahaifinsa Abubakar xan Haruna, mahaifiyarsa ita ce Habiba ‘yar Isma’il.[12]An haifi Sani Abubakar, a ranar 02/10/1975, a Unguwar Tarauni. Ya yi karatun allo a makarantar Malam Abdullahi Kawon mai Gari, da makarantar Malam Musa Bagobiri. Ya yi makarantar Islamiyya mai suna*Nurul Islam*[13], a layin gidan Wanzamai. Ya fara karatun zamani a makarantar firamare ta Kawo, inda ya gama a shekarar 1990. Ya ci gaba da makarantar sakandire ta Tarauniinda ya gama a shekarar 1996. Daga nankuma ya samu damar shiga makarantar Kwalejin Kimiyya da ke Kano, inda ya yi Difiloma a Vangaren Harkokin Kuxi *Financial Accounting,* ya kuma sami takardar shaidar karatu a kan Na’ura mai qwaqwalwa a Hamdam da ke Kwanar Sabo Tarauni a Kano.

Sani ya yi aikin kamfani a Dakata a kamfanin Kwano a shekarar 2004 zuwa 2006. Sai ya koma wani kamfani mai suna *HIYCO* da ke kan titin Haxeja, a inda ya zauna a sashen saye da sayarwa na kamfanin ya kuma riqe Shugaban Sashen tun

[12]Wannan bayanin ya fito daga bakin marubucin a unguwar Hotoron Walawai, 07/10/2017, da qarfe 2:30 na rana.

[13] Makarantar Islamiya ce da take cikin Unguwar Kawon Kudu, a qaramar Hukumar Nassarawa.

daga 2006 zuwa 2012. Yanzu kuma yana koyarwa a Makarantar *Lady Birds* a vangaren Firamare a Unguwar Tarauni.Yana da mata biyu da ‘ya’ya goma sha xaya (11). Har yanzu kuma yana karatu a wajen Malam Aliyu mai Asasu, Limamin Masallacin Juma’ar Unguwar Walawai, da Malam Abubakar wato Malam Babba da kuma Shaikh Sharif Sunusi Unguwa Uku.

A vangaren waqoqi kuma,marubucin ya fara karanta waqoqi ne tun a makarantun Islamiyya, inda daga baya suka kafa Qungiyar Marubuta Waqoqi 1998. Daga ciki waxanda suka kafa qungiyar akwai Salisu Zoro Hotoro da Malam Bashir Yalo da kuma Jamilu mai Salati Farawa, da sauransu. Daga nan, sai ya kafa qungiya mai suna*Hadratul Madahu Nabiyi* (Hallarar Yabon Annabi (S.A.W.) qarqashin jagoranci malaman Ta’asisul, sai wasu qungiyoyin a Kawo da Giginyu, da qungiyar *Madihan Nassarawa,* sai kuma *Majalisar Sha’iran Nassarawa*, inda ya zama Mataimakin Shugaba.Waqar da ya fara yi ita ce mai suna “Qaunar xan Amina” a shekarar 1991, sannan yana da rubututattun waqoqi aqalla 200.Kaxan daga cikinsu su ne kamar haka:

1. Sayyada Faxima (1994)

2. *Ummul Nabiyi* (S.A.W.)(1996)

3. Muradin Zuciya (2001)

4. *Rabbi* Qara Aminci(2002)

5. Neman Ilimi (2006)

6. Sayyada Khadija (2007)

7. Mai Cikar Xaukaka (2008)

8. Abul Faxima (2011)

9. *Khulafa'urrashiduna*(2014)

10. Ta'aziyar Malam Nasiru Kabara/ Rufa'i Ibrahim Ayagi (2013)

11. Sallah (2014)

12. Sayyadi Abubakar (R.A)(2016)

13. Matsayin Malamai (2017)

Waxanan su ne kaxan daga cikin waqoqin marubucin kuma daga cikinsu za a xauki guda tara (9) don aiwatar da wannan nazarin na fito da jigo da kuma zubi da tsarin su. Ta haka ne za a qara fahimtar waqoqinsa da kuma fasaharsa wajen isar da saqonsa ga al'umma. Shi ma Sani akwai wanda yake yin waqoqinsa shi ne Malam Sunusi Muhammad da Abdullahi Abulkarim da sauransu.A qarshen wannan binciken ana sa ran za a sami duk abubuwan da aka ce za a samu cikin kamar yadda yake isar da saqonsa da kuma yadda yake zuba baitocinsa a cikin waqoqinsa.

# BABI NA BIYU

# BITAR AYYUKAN DA SUKA GABATA

## 2.1 Gabatarwa

A cikin wannan babi an yi waiwaye ne a kan ayyuka da aka gabatar masu alaqa da wannan nazari waxanda suka haxa da bayanin kalmomin da aka yi amfani da su wajen yin nazarin daga masana da manazarta daban-daban. Sai kuma bitar kundayen bincike da bugaggun littattafai da kuma maqalu da sauran takardun ilimi.

## 2.2 Ma’anar Jigo

Xangambo (2007:14) ya bayyana jigo da cewa, “Shi ne saqo, ko manufa ko abin da waqa ta kunsa, wato abin da take magana a kai”

Jigo shi ne irin saqon, da marubuci ya ke son sadarwa ga jama’a. Kuma duk wani salo da tsari ko wata dabara da marubuci zai yi amfani da su, zai yi hakan ne da nufin isar da saqon nasa ga jama’a (Sarvi. 2007:69).

### 2.2.1 Furucin Gundarin Jigo/ Qwayar Jigo

A nan za a buqaci mutum ya fahimci manufar soqon na gaba xaya da mawallafin ke qoqarin isarwa ga jama’a, wato abin da yake nusarwa wanda kuma saboda shi ne ya wallafa waqar (Xangambo, 2007:14).

### 2.2.2 Jigo a Gajarce

Xangambo (2007:17) ya bayyana cewa, “A nan za a bi waqa a taqaice baiti bayan baiti ana taqaita abin da mawaqi yake faxa. Za a yi haka ne ba tare da sharhi, bayyana ra’ayi ko wani dogon bayani ba ”.

### 2.2.3 Warwarar Jigo da Shimfixarsa

A nan za a yi sharhi ne kan jigo gaba xayansa. Za a duba shi dangane da jawaban jigo, da kuma abin da waqar ta faxa a taqaice. To amma muhimmin abin shi ne za a duba lungu-lungu na waqar dangane da jigo tare da qarin bayani daga dukkanin abin da za a iya danganta waqar da shi (Xangambo, 2007:18).

### 2.3 Ma'anar Zubi da Tsari

Zubi da tsarin waqa hanya ce ta shimfixa waqa baki xayanta dangane da layuka da baitoci da amsa amo da kuma jerantuwar tunanin marubuci wajen kaiwa ga manufarsa da sauransu (Xangambo,2007:14).

### 2.3.1 Zubi da Tsari na Gaba Xaya

A nan za a duba a ga cewa shin marubucin yana jeranta tunaninsa ko kuwa yana kwan-gaba-kwan baya, ko yana maimaita batutuwa, ko ya sassarqa su yadda sai an sha wuya a sake shisshirya su idan an zo karkasa waqar wajen taqaita ta (Xangambo, 2007:19).

### 2.3.2 Zubi da Tsarin na Cikin Baitoci

Xangambo (2007:19-20) ya bayyana cewa "A nan kuma ana duba dangantakar xango a cikin baiti da kuma cewa ko baitoci sun qunshi jumlatatun manufofi a bisa kansu ko kuma sun dogara da juna don cikar ma'ana. Wato za a duba savi-zarce da gangara.

### 2.3.3 Karin Waqa/Aruli

Mukhtar (2005:7) yana ganin "Kalmar Aruli an aro ta ne daga kalmar Larabci, wato "Arud". Aruli yana magana ne a kan karin waqa"

Xangambo (2007 20-21) kuwa cewa ya yi "Bahari shi aka fassara da Hausa zuwa kari. Aruli ko nazarin karin waqa".

Bello da Sheshe (2013:20) sun bayyana ma'anar Aruli da cewa "Wanzuwar qafafuwa masu bibiyar juna cikin tsari a baitin waqa ko da baitin mai layi nawa ne. Kuma qafa xaya tana iya maimaita kanta a baiti ko baitocin waqa domin ba da karin waqa. A nan za mu kira irin waxannan qafafuwa 'Maimaitau'. Haka kuma qafafuwa biyu mabambanta na iya haxuwa a baiti ko baitocin waqa domin ba da karin waqar. Za mu iya kiran waxannan qafafuwa 'gwamau'.

### 2.3.4 Gangara

Gangara tana aukuwa ne cikin baiti inda za a faro wata magana a cikin wani xango, ba za a qare ta ba sai a xango na gaba (Xangambo, 2007:51).

> Sarvi (2007:110 - 111) Yana ganin :
>
> Gangara na nufin dangantaka tsakanin layi da layi a cikin baiti xaya. Abin nufi a nan shi ne, mawaqi zai fara magana a wani layi, amma ba zai qare ta ba, ko in ce, ba za ta cika ba sai a layi ko layuka na gaba na cikin baitin…..

#### 2.3.4.1 Gangara ta Gaba

Sarvi (2007:111) ya nuna cewa "Gangara ta gaba mawaqi ne zai fara wata magana a wani xango amma ba zai qare ta ba sai a xango ko xangwaye na gaba na baiti. A irin wannnan hali, jimla/maganar farko ta dogara ne ga maganar da ke biye wadda kuma take cin gashin kanta".

#### 2.3.4.2 Gangara ta Baya

Mawaqi zai yi wata cikakkiyar magana a xango na farko (inda aka fara maganar) sannan kuma ya gina mai/masu dogaro da ita a xango ko xangaye na gaba ta dogara ne kacokan a kan fahimtar xango na baya (Sarvi, 2007 :115).

#### 2.3.4.3 Gangarata Tsakiya

Kamar yadda Sarvi (2007:116-117) ya bayyana cewa, " Wannan yanayi ne da layuka biyu ko fiye da biyu ke dogara da juna. Wajen samar da ma'ana cikin baiti. Abin nufi a nan shi ne kowane layi ba ya iya zaman kansa, balle wani ya dogara da shi. Idan layuka biyu na da irin wannan dangantaka, to dole sai an karanta su a jere kafin a san abin da marubucin ke nufi.

### 2.3.5 Savi-zarce

Xangambo (2007:52) yana ganin cewa " Savi-zarce ita ma wata irin gangara ce mai zurfi, domin ita tana aukuwa ne daga wani baiti zuwa wani, wato tana qulla baitoci ne".

Sarvi (2007:119) ya bayyana cewa:

> Savi-zarce, dabara ce da marubuta waqoqin Hausa ke amfani da ita wajen jinkirta abin da suke son faxa daga wani baiti zuwa wani. Ma'ana mawaqi ne kan fara wata magana a wani baiti, amma ba zai qare ta ba sai a baiti na gaba. Kuma ana samun irin wannan dangantaka kai tsaye tsakanin xangon qarshe na baiti da ya gabata da kuma xangon farko na baitin da ke biye.

### 2.3.5.1 Savi-zarce na Gaba

Sarvi (2007:119) yana ganin cewa, "Wani zubi ne wanda marubuci zai fara wata magana a wani baiti amma ba zai qare ta ba sai a baiti na gaba. A wannan yanayi maganar da aka yi a baiti na farko ba ta da ma'ana sai an je baiti na gaba sannan a samu ma'anar. Kuma baiti na gaba yana cin gashin kansa ne, na baya ne yake dogara da shi".

### 2.3.5.2 Savi-zarce na Tsakiya

Wannan ya shafi irin yadda baitoci biyu, masu iyaka da juna kan dogara da juna wajen samar da ma'ana. Abin nufi a nan shi ne ma'anar baitin farko (na baya) ce ke zarcewa zuwa gaba, sannan ma'anar baitin da ke biye (na gaba) ta koma baya, su haxu kafin a fahinci wurin da kowanne baiti ya sa ga (Sarvi, 2007:122).

### 2.3.5.3 Savi-zarce na Baya

A nan, mawaqi ne zai yi wata magana mai ma'ana a cikin wani baiti. A baiti na gaba kuma, sai ya gina wata maganar da ta dogara kacokan ga wanda ya yi a

baya. Ma'ana, baitin da ke biye shi ne ya dogara ga baitin da ya gabata (Sarvi, 2007:121).

**2.4Ma'anar Kwatantawa**

A C.N.H.N (2006:268), an bayyana kwatantawa da"Gwada abubuwa domin nemo bambanci tsakaninsu".

Xangambo (2007:43) ya nuna cewa "Kwantatawa ta kasu zuwa gida biyu, Kamantawa da siffantawa".

Sarvi (2007:153) yana ganin "Kwatantawa hanya ce ta auna abubuwa biyu domin a tantance irin dangantakar da ke tsakaninsu. Wannan dabara tana taimakawa wajen bayyana kamanci ko bambanci tsakanin abubuwa biyu"

Kwatantawa tana nufin misalta wani abu ta hanyar yanayi ko tsari. Wato nazartar wasu abubuwa guda biyu ko fiye da haka mabambanta da juna da niyyar gano wuraren da suke da dangantaka da juna (kamanni da bambanci), tare da kawo qwararan hujjoji da dalilai da za su nuna kamancin ko bambancin (Bilkisu,2014:18).

**2.5 Kundayen Bincike da Bugaggun Litattafai da Sauran Takardun Ilimi**

Muhammad (1974) ya kalli tarihin waqoqin Hausa da Fulatanci, inda ya kawo wasu waqoqin da suka shafi harsunan guda biyu, sannan ya yi bayanin abubuwa da suka bambanta waqoqin, kuma ya duba jigon waqoqin da zubi da tsarinsu.Sannan kuma ya kawo misalan jigo da zubi kuma ya kawo bayani a kan

taqaitacen tarihi waqa (asalin samuwarta) da rabe-rabenta, kamar yadda masana suka raba(waqar baka da kuma rubutacciya). Manazarcin ya yi bayani da kuma nuna yadda waqoqin kowanne harshe suke.

Wannan nazari yana da alaqa da wanda ake nazarta saboda ya duba jigo da zubi da tsari, sannan ya kawo misalan jigo da zubi da tsarin waqoqin, ya kawo bayani a kan taqaitacen tarihi waqa da rabe-rabenta. Sai dai sun bambanta wajen kwatancin abun da aka duba kuwa shi ne ya kwatanta rubutattun waqoqin Hausa da na Fulatanci. Wannan bincike kuma ya taqaita ne kawai ga marubuta guda biyu da waqoqinsu, ba harsuna guda biyu ba.

Xangambo (1980) ya nazarci waqoqin da aka wallafa na wa'azi daga qarni 19-20 inda ya yi nazari dangane da jigo da zubi da tsari, sannan kuma ya yi nazari waqoqin bisa tsari na aruli, haka kuma a cikin kundin ya yi rataye na waqoqin da ya yi amfani da su. Wannan kundin yana da dangantaka da wannan, saboda ya tavo vangaren nazarin rubutacciyar waqa ya kuma kawo wasu waqoqi da dama da ya yi nazarinsu.

Bambanci aikinsa da wannan aikin shi ne, shi ya kalli waqoqin wa'azi ne na qarni na19-20, inda wannan nazarin ya kalli jigo da zubi da tsari cikin waqoqin Bello Mai Karama da Sani Abubakar ta hanyar kwatantasu.

Mukhtar (1984) ya yi bayani a kan ma'anar kwatantawa, sannan ya nazarci waqoqi daban-daban inda ya fito da nahawun da ke cikin baitocin waqoqin. Wannan aiki ya tavo sassa daban-daban na nazarin waqa.

Dangantakar wannan bincike da nawa shi ne abin da ya shafi rubutacciyar waqa, inda suka bambanta kuwa shi ne, shi ya kalli nahawun waqa, da kuma hanyoyin isar da saqo kafin waqa, wannan aikin ya kwatanta jigo da zubi da tsari ne a waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro.

Yahaya (1984) ya kawo tarihin samuwar rubuce-rubuce a qasar Hausa, tun daga kan rubutun ajami har zuwa na boko. A cikin littafin, an yi cikakken bayanin farkon samuwar rubutattun waqoqi, sannan an kawo tarihin samuwar rubutattatun waqoqin Hausa da hanyoyin da aka fara rubutasu, wato hanyar rubutu ta ajami.

Wannan maqala ta Yahaya (1984) tana da alaqa da wannan aikin ta abin da ya shafi rubutacciyar waqa, sai dai sun bambanta kasancewar ta kalli hanyoyin rubuta waqoqin Hausa musamman na ajami, a inda suka bambanta,a wannan kwatanta waqoqin marubuta guda biyu ne.

Yahaya da Xangambo (1986) sun yi bayani a kan ma'anar adabi da tushensa, sannan sun  kawo taqaitaccen tarihin samuwar waqoqi da manufofinsu, kuma suka raba waqoqin gida biyu, da waqoqin  qarni na sha tara da kuma waqoqin qarni na ashiri inda suka yi bayani a kan jigogin qarni na sha tara su ne jigogin da suke bayani a kan addini zalla. Amma  rubutattun waqoqin qarni na ashirin kuwa an

sami ci gaban jigon addini amma kuma an sami sabbabin jigogi musamman saboda zuwan Turawa. Haka kuma sun kawo hanyoyin da ya kamata a yi nazarin rubutacciyar waqa.

Littafin ya ba da gudummawa wajen jagorantar wannan bincike. Bambancin aikinsu da wannan shi ne, sun kalla jigo guda biyu, wato jigon waqoqin qarni na sha tara da na ashirin, sakamakon wannan kuma, an yi nazarí ne game da jigon waqoqin marubuta guda biyu, waxanda suka shafi jigo da zubi da tsari.

Jangebe (1991) ya tattara waqoqi da suke da jigon yabo, inda ya yi cikakken bayani kan zubi da tsarinsu da kuma sharhi a kansu. Mai bincike ya tavo bayani a kan abubuwan da ake nazarin su a rubutattun waqoqi, kamar jigo da zubi a tsari.

Dangantakar aikinsa da wannan, shi ne an yi tarayya a kan jigogin yabo, amma sun bambanta da juna ta fuskar nazarin marubuta waqoqi guda biyu, masu xauke da jigon yabo.

Dutsi (1992), ya kawo cikakken tarihin rayuwar Malam Tijjani Tukur Yola, a matsayinsa na mai yabo, sannan ya yi nazarin wasu waqoqi guda huxu. Wannan binciken shi ma ya tavo nazarin waqoqi, kamar yadda binciken ya gudanar da nazarin waqoqi ta fannin jigo da zubi da tsari, kuma ya yi taqaitaccen bayani game da samuwar waqoqi, da kuma gudummuwar da malamin ya bayar a fagen rubutattun waqoqi. Don haka suna da alaqa ta wannan fuskar abubuwan da aka yi

nazarí, amma sun bambanta da juna domin a wannan an fi mayar da hankali ga nazarin waqoqin Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro.

Isma'il (1994), ya duba kafuwar wasu qungiyoyi, kamar: *Usshaqun Nabiyi* da *Ahababu Rasulullah* da *Zumratul Madahu,* inda ya yi nazarin jigon wasu waqoqin da fito da wasu waqoqi game da qungiyoyin da kuma kawo waqoqinsu. Nazarinsa ya taimaka qwarai, kuma an amfana, sai dai ya fi mayar da hankali a wajen qungiyoyi na yabo. Wannan kuma an yi domin nazarta jigogin mawaqa guda biyu tare da zubi da tsarin waqoqinsu.

Auta (2001), ya bayyana ma'anar waqa ya kuma kwantata rubutattun waqoqin Hausa da na baka dangane da aiwatarwa da zubi da tsari da, ya yi bitar rubutattun waqoqin qarni 19 da na 20 dangane da jigo, sannan kuma ya kawo misalan wasu waqoqin qarni na 20 dangane da sigoginsu.

Dangantakar wannan muqala da wannan aikin shi ne ya qara haske kamar ta vangaran bayanin waqa da zubi da tsari, sai dai sun bambanta da juna, kasancewar shi ya kalli tarihin rubutattun waqoqin Hausa, ya kuma kwatanta waqoqin baka da kuma rubutattun waqoqi. Inda wannan ya yi nazarin a kan rubutacciyar waqa mai xauke da jigo da zubi da tsarin da ya shafi marubatan waqoqin yabo guda biyu.

Birnin Tudu (2003), ya xauki waqoqi guda uku ya nazarce su. Haka kuma ya kawo kashe-kashen jigogin waqoqin ta fuskoki daban-daban, kamar jigon aure da jigon tsarki da na kasuwanci da na zakka da makamantansu. A qarshe ya yi

cikakken bayanin sauye-sauyen da ake samu a cikin karuruwan aruli na Hausa dangane da waqoqin.Ya kalli rubutattun waqoqin furu'a, ya duba jigo a wasu rubutattun waqoqi.

Wannan bincike yana da alaqa da wannan domin ya tavo jigogin waqoqi a cikin nazarinsa ta inda ya kalli rubutattun waqoqin furu'a, ya duba jigo a wasu rubutattun waqoqi. Bambancin wannan bincike da wannan, kuwa shi ya duba waqoqin qarni na 20, wannan kuma ya duba jigo ne da zubi da tsarin waqoqin wasu marubuta guda biyu, Waxanda suke a wannan qarni na 21, inda aka kwatanta waqoqinsu.

Shi kuwa Sankalawa (2004), ya kwantanta waqar Sani Yusif Ayagi ne da Aliyu Namangi. Ya kawo taqaitaccen bayanin marubutan, sannan kuma ya yi bayanin a kan ma'anar waqa da kuma tarihin qasar Hausa. Marubucin ya fito da abubuwan da suka bambanta waqoqin marubutan, sannan ya kawo salon marubutan na jawo hankalin masu karanta waqoqinsu.Kuma ya yi bayani a kan waqa da rabe-rabenta.

Alaqar aikinsa da wannan, shi ne ya kwatanta marubuta guda biyu, ya kuma kalli tarihin rayuwarsu da kuma jigogin waqoqin nasu, kuma ya yi bayani a kan waqa da rabe-rabenta. Sai dai sun bambanta domin shi ya kwatanta waqoqin Aliyu Namangi ne da Sani Yusuf Ayagi, a inda wannan kuma ya kwatanta waqoqin Bello

Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro, amma ba a nazarci waqa da rabe-rabenta ba, saboda wannan aikin ya fi mayar da hankali a kan jigo da zubi da tsari.

Xangambo (2007), ya yi bayanin abin da shafi waqa da tarihinta da hanyoyin nazarinta kamar hanyoyin nazarin waqa ta gargajiya da kuma na zamani da bayanan sharar fage wajen nazarin waqoqin ya yi bayanin jigo da hanyoyin warwararsa da zubi da tsarin waqoqin da aruli da qarangiya da abubuwan da ake duba wa qarqashin zubi da tsarin waqa. Littafin ya ba da gudummawa sosai wajen gabatar da wannan nazari, kasancewar a cikinsa aka ciro ra'in da ka xora wannan aikin a kai.

Sarvi (2007), ya kawo ma'anar rubutacciyar waqa tare da kawo ma'aunin waqa, da kuma nau'o'in waqoqin kamar gwauruwar waqa da qwar - biyu da tarbi'i sannan kuma ya kawo ma'aunin waqa a ciki kuma ya yi bayani a kan mabuxin waqa da makullinta. Ya kuma kawo bayanin zubi da tsari na waqa ya yi bayani a kan zubi da tsari na waqa da savi- zarce ya kasa gangara zuwa gida uku, kamar yadda ya raba savi-zarce, ya kawo dabarun nazarin rubutacciyar waqa. Littafin ya qara haske tare da yin jagora, wajen ganin samun nasarar wannan aiki, duk da kasancewar sun bambanta, musammam ta fuskar nazarin marubuta waqoqin yabo guda biyu, Bello Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro.

Xangambo (2008),ya raba waqoqin Hausa zuwa gida biyu, waqoqin qarni na 19 da kuma qarni na 20, a ciki ya yi bayanin jigogi, tare da kawo misalan

waxannan waqoqin, musammam na lokacin masu jihadi. Littafin ya bada gudummawa wajen haska yadda aka gabatar da wannan nazari.

Bambancin wannan littafin da wannan bincike suna da yawa, shi littafi ne, wannan kuma kundin bincike ne. Sannan kuma shi a cikin littafin ya kalli abubuwa da dama, kamar qagaggu labarai da wasan kwaikwayo da sauran abubuwan da suka shafi adabi. Wannan bincike ya shafi rubutacciyar waqa ne kawai.

Auta (2008) ya yi nazarin jigogin waqoqin faxakarwa na ilimi da gyaran hali da kishin kai da na zamantakewa. Ya yi nazarin waqar "Ilimin Zamani" da waqar "Munin Zina" da "Suttura Ita ce Mutum" da kuma "Waqar Hakkin Maqwabci". Ya yi nazarinsu gaba xaya inda ya fitar da jigo da zubi da tsari, sannan daga qarshe ya yi ratayen wasu waqoqin da ya nazarta.

Aikin Auta da aikin da aka gudanar, suna da alaqa ta fuskar rubutacciyar waqa. Sai dai bambancin aikinsa da wanda aka gudanar shi ne, shi ya kalli jigogin waqoqin faxakarwa, ya yi nazarin jigo da zubi da tsari da salo kuma da sarrafa harshe. A wannan aiki kuwa an duba jigo ne da zubi da tsari a cikin wasu waqoqin marubuta guda biyu.

Xiso (2009), ya yi tsokaci a kan ma'anar waqa da ire-irenta da tasirin samuwar rubutacciyar waqa tare da nau'o'in rubutattun waqoqi dangane da tsarin layukansu, sannan ya kawo bayani a kan nazarin rubutacciyar waqa ta fuskar jigo da zubi da tsari. A qarshe ya jero wasu daga cikin rubutattun waqoqi.

Wannan littafi yana da alaqa da wannan binciken, kasancewar ya yinazari a kan rubutacciyar waqa, sannan kuma ya tavo muhimman abubuwan da aka kalla wato, jigo da zubi da tsari. A wannan aiki an amfana sosai – da –sosai duk da kasancewar ya yi nazarin abubuwa muhimmamai masu yawa wanda suka sava da wannnan domin wannan ya ta'allaqa ne a kan nazarin jigo da zubi da tsari.

Sadiya (2010) ta kawo tarihin rayuwar Mu'azu Haxeja, sannan ta kalli jigo da zubi da tsari. Bincike ya yi tsokaci a kan irin yadda Mu'azu Haxeja ya yi amfani da zubi da tsari a cikin wasu waqoqinsa.

Aikinta yana da alaqa da wannan bincike musammam abin da ya shafi zubi da tsari, sai dai sun bambanta kasancewar ta yi nazari ne a kan rayuwar Mu'azu Haxeja, wannan kuma an yi nazarin waqoqin Bello Mai Karama da Sani Hotoro.

Sulaiman (2011), ya kwatanta waqoqi guda biyu na qarni na 19 da na qarni na 20, inda ya nazarci jigo, sannan ya yi bayanin inda waqoqin suka yi kama da inda suka bambanta.

Alaqar aikinsa da wannan shi ne  sun yi tarayya a kwatanta jigo a rubutattun waqoqi, sai dai wannna ya fi mayar da hankali a kan marubuta waqoqi guda biyu masu xauke da jigo da zubi da tsari.

Halima (2012), ta yi nazarin yadda ake gina jigo a rubutaccen adabin Hausa. Haka kuma ta bayyana tubalan da ake amfani da su wajen gina jigo a rubutattun waqoqi Hausa.Ta fuskar rubutattun waqoqi, ta kawo tubalan gina jigo waxanda

suka haxa da xango da baiti tare da yadda za a sarrafa su. Sannan matanonin sun haxa da waqar "Wasiqar So" ta M. B. Umar da littafin *In da So Da qauna* na Ado Ahmad Gidan Dabino da kuma waqar "Qalubale" ta Aqilu Aliyu da littafin *Wa Zai Auri Jahila* na Balaraba Ramat.

Alaqar kundinta da wannan, a kundin an yi bayani a kan rubutattun waqoqi da duba jigo da zubi da tsarinsu, bambancin aikin da wannan kuwa an haxa waqa ne da qagaggen labarai , amma wannan aiki ya duba waqa ne kawai.

Nura (2012), ya duba waqoqin da aka yiwa Sarkin Kano na baka da kuma rubutattun waqoqin inda a ciki ya yi bayanin waqar baka da kuma rubutacciyar waqa sannan ya kalli yadda marubuta suke fito da abubuwa na yabo ga maimartaba da suka haxa da haquri da kuma juriya. Ya kuma xora aikin nasa a kan hanyoyin nazarin Gusau (2003) da Xangambo (2007), sannan binciken ya gano zubi a waqoqin da ya yi nazari.

Alaqar wannan aiki shi ne rubuttatu waqoqi, ya kawo jigogi da zubi da tsarin waqoqin. Bambancin aikin kuwa shi waqoqin Sarkin Kano ya duba na baka da rubutattun da aka yi masa, wannan kuma an yin nazarin waqoqin marubuta guda biyu ne, ta duba jigon waqoqin da zubi da tsarinsu.

Gusau (2012) ya yi bayanin asalin da matakan waqa kuma ya kawo jigogin waqoqin, sannan ya bayyana yadda ake shirya waqa, inda ya kawo bayanin masana a kan rubutacciyar waqa.

Wannan takardar ta qara wa wannan aikin haske, inda a cikin takardar aka yi bayani a kan matakan shirya waqa da bambancinsu da hanyoyin da ake bi wajen aiwatar da su. Alaqar aikin shi ne fito da abubuwan da rubutacciyar waqa ta ginu a kansu da matakan gabatar da ita. Bambancin su kuwa wannan kundi ne, kuma ya duba jigo da zubi da tsari ne kawai.

Muhammad (2013) ya duba waqoqi guda biyu waqar baka da rubutacciyar waqa inda ya kawo ra'ayoyi masana a kan waqoqin, ya bayyana jigogin rubutattun waqoqi, kamar jigon wa'azi da faxakarwa wa da nasiha da kuma wayar da kai da ilimi da kuma siyasa.

Dangantakar aikinsa da wannan ta vangaren nazarin rubutacciyar waqa shi ne ta wajen fito da jigoginta da bayyana misalan waqoqin da duba bayanan da masana suka yi a kan waqa. A wannan aiki na Muhammad an duba waqa ce ta mutum xaya,a wannan kuma marubuta waqoqi guda biyu aka yi nazarin waqoqinsu ta fuskar jigo da zubi da tsarin waqoqinsu.

Habiba (2014), ta fito da salon da Rahma A. Majid ta yi amfani da shi a cikin littafinta na *Mace Mutum* ta kwatanta shi da salon da Abdulqadir Alasan ya yi amfani da shi a waqarsa ta "Mikiyar Zuhudu" ta kwatanta kuma ta gano yadda marubuta suke xaukar mace da irin kalon da suke mata.

Alaqar tsakanin wannan aiki, shi ne ta yi nazarin waqar inda ta kwatanta yadda marubuta guda biyu suke amfani da basirarsu wajen isar da saqonninsu ga

al'umma, sannan kuma ta fito da jigon waqar. Bambancin aikinta da wannan kuwa, ita ta duba waqa da qaggagen labari, wannan aikin kuwa ya shafi waqoqi ne kawai.

Nalado (2015) ya yi bayani dangane da kwatanta waqoqi guda biyu ta fuskar jigo da zubi da tsarinsu da salon sarrafa harshe. Sannan marubucin ya kawo tarihin marubuta waqoqin da gudummuwarsu, haka kuma ya yi amfani da waqoqin wajen da fito da abubuwan da ya yi nazari a kai.

Alaqar aikinsa da wannan shi ne ya duba marubuta waqoqi guda biyu, ya fito da jigon waqoqinsu da kuma zubi da tsarin waqoqin. Haka yake a wannan binciken da aka gudanar an duba jigo da zubi da tsari da kawo misalai da suka shafi waqoqi. Bambancin aikinsa da wannan kuwa shi waqoqi biyu kawai ya kalla, wannan bincike ya duba waqoqi ne sama da guda biyu, sannan waxanda ya duba waqoqinsu, ba su wannan aikin ya duba ba.

Birnin-Tudu (2015) ya fito da matsalolin da suka sa marubuta da manazarta rubutattun waqoqin ke neman gushewa. Ya kawo jigogin da aka fara gina waqoqin a kansu da amsa-amo. Haka kuma yana ganin rumbunan adana waqoqi su ma an yi bankwana da su irin su:*Waqa a Bakin mai ita* da *Dandalin Hikima* da *Gasar ga ni ga ka* ta rubutattun waqoqi. Haka karin waqa da ramzi su ma duk suna neman gushewa. Alaqar wannan aiki shi ne dangantakar da suke da ita wajen abubuwan da suka shafi marubuta waqoqi da abubuwan da ake nazari a fagen.

Bambanci aikinsa da wannan ya gabatar da muqala ne, ya kuma duba abubuwanda suke faruwa a qarni na ashirin da xaya, wannan bincike shi kuma yana duba waqoqi ne da aka yi a qarni guda biyu: wato qarni na ashiri da kuma qarni na ashirin da xaya. Sannan kuma wannan bincike yana duba jigo da zubi da tsarin waqa na marubuta waqoqi guda biyu.

Tilde (2016), ya fito da bayanai a kan karin waqa, kuma ya yi wa karuruwa dukagoma sha shida (16) da ake da su a waqa. Dangantakar aikinsa da wannan shi ne, an yi tarayya a vangaren nazarin rubutacciyar waqa.

Bunguxu (2017), ya yi bayani a kan wasu da cikin waqoqi da samuwarsu da bayani a kan jigo da zubi da tsari. Ya kawo tarihin marubucin da ya yi nazarin waqoqinsa, sannan ya yi nazarin zavavvun waqoqi guda huxu, ya fito da abubuwan da ya yi nazari a ciki.

Alaqar wannan aiki da wannan shi ne, nazarin jigo da zubi da tsari a ciki, sannan marubucin ya duba karin waqa da bayani a kan abun da ya shafi nazarinta, haka wannan kundi shi ma ya duba waxannan abubuwan. Bambancin kuwa shi ne a wannan ana kallon kwatanci ne na waqoqin marubuta guda biyu, Bello Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro, ta fuskar jigo da zubi da tsari ba, na mutum xaya ba.

Muhammad (2018), ya kwatanta yanayin tatsuniyoyin da jigo da zubin tatsuniyoyin qasar Hausa da na jamhuriyar Nijar. Nazarin ya gano abubuwa masu

kama da juna da kuma waxanda suka bambanta da juna a tatsuniyoyin. Idan aka yi la'akari da jigo a tsarin sarautar gargajiya, musamman dangantakar sarki da talaka sun bambanta. Har ila yau, a zubin labari kuma a inda aka aka ba da misalan tatsuniyar Najeriya da Jumhuriyar Nijer. Marubicin ya yi haka ne ta hanyar kawo tatsuniyoyin da kamanci da kuma bambanci da aka samu.

Wannan aiki yana da alaqa ta fuskar kwatanci, wajen jigo da kuma zubi da tsari, sannan aikin ya qara ba da haske wajen yadda aka kwatanta wannan aikin da aka gudanar. Bambancin kuwa, shi ya kalli tatsuniya ne tsakanin qasashe guda biyu ta fuskar labari, wannan kuma waqoqin marubuta guda biyu aka kwatanta.

A qarshe wannan babin ya kawo ma'anoni da bayanin abubuwan da ake nazarinsu a waqa. Sannan an duba kundaye da littatafai da kuma muqalu, domin samun damar gano hanyoyin da suka bi domin sauqaqa hanyar gudanar da wannan bincike. Duk da haka ba a ci koro da aiki iri xaya da wannan ba.

# BABI NA UKU

# RA'I DA HANYOYIN GUDANAR DA BINCIKE

## 3.1 Gabatarwa

A wannan babi an kawo ra'in da aka xora wannan bincike a kai da kuma hanyoyi da aka bi wajen gudanar da bincike, wanxada suka haxa da tattara waqoqi da tattara bayanan da ya shafi wannan aiki.

## 3.2 Ra'in da aka Xora Bincike a Kai

Masana da dama sun gabatar da nazarce-nazarcen da ya shafi ra'o'i, don haka daga cikin waxannan ra'o'in da masana suka kawo akwai wanda ya shafi nazarin rubutacciyar waqa, musamman nazarin jigo da zubi da tsari. Binciken da aka gudanar ya yi bitar su, kuma an zavi biyu an xora aikin a kai, saboda da dacewarsu da aikin. Waxannan ra'o'in ta hanyarsu ne aka gudanar da wannan aikin. Xaya daga ciki ya yi bayani a kan hanyoyin nazarin jigo da zubi da tsari, sannan shi kuma xayan ya yi bayani a kan hanyoyin kwatantawa.

Ra'in farko da aka xauka shi ne ra'in Xangambo daga littafinsa mai suna *Xaurayar Gadon Fexe Waqa* (2007), wanda ya taimaka qwarai wajen nazartar yadda ake fito da jigo da nazarinsa da yadda ake duba zubi da tsari, ta hanyar duba yadda mawallafa suke zaven kalmominsu da sauran abubuwa da suke da dangantaka da zubi da tsarin waqoqinsu.

Ra'in ya yi bayanin yadda za a yi nazarin rubutacciyar waqa, ta hanyar bin wasu matakai da ya kawo.

Don haka, wannan bincike ya yi amfani da wannan ra’i don ganin an fito da waxannan abubuwan daga cikin misalan waqoqin marubutan wato jigo da zubi da tsari.

Muhimman abubuwan da aka duba a qarqashin wannan ra’i sun haxa da:

1. Jigo
2. Furucin Gundarin Jigo/ Qwayar Jigo
3. Jigo a Gajarce
4. Warwarar Jigo da Shimfixarsa
5. Zubi da Tsari
6. Zubi da Tsarin na Gaba Xaya
7. Zubi da Tsari na Cikin Baitoci
8. Nazarin Karin Waqa
9. Gangara da Savi- zarce
10. Jinkirin Faxar Sakamako

(Xangambo, 2007: 14-36)

Sannan ra’i na biyu shi ne,ra’in Kwatanta Adabi(*Comparative Theory*). Na Brandes, G. (1997). A taqaice ra’in na qoqarin bayyana yadda ake kwatanta abubuwa guda biyu. Ana gudanar da haka ne, da nufin gano kamanci da bambancin da ake hange, a tsakanin adabin guda biyu, tare da qoqarin gano dalilan kamancin ko kuma bambancin da ke tsakaninsu.

Ra'in kwatanci, ra'i ne da ake iya amfani da shi wajen kwatanta wasu abubuwa da suka shafi harshe, ko kuma adabi a tsakanin al'umma daban.

### 3.3 Hanyoyin Tattara Bayanai

A kowane irin bincike, akwai hanyoyin da ake bi domin aiwatar da shi. A wannan bincike, an bi hanyoyi da dama domin samun nasarar aikin. Irin waxannan hanyoyi sun haxa da karance-karance a xakunan karatu da tattaro waqoqin marubutan da ganawa da masana a wannan fanni na adabi, sai ziyara da sauransu.

#### 3.3.1 **Tattaunawa da Marubutan da Masu Alaqa da su**

An samu nasarar ganawa da marubutan a gidajensu. Haka kuma an sami damar tattaunawa da 'yan'uwa, don yi musu wasu tambayoyi game da marubutan da masu alaqa da su, sannan an tattauna da su domin samun bayanai waxanda suka taimaka wajen kai wa ga samun nasarar kammaluwar wannan bincike.

#### 3.3.2 Tattaro Waqoqin Marubutan

A yayin gudanar da wannan bincike, an yi qoqarin tattaro waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro ta hanyar tuntuvar su, inda aka samu waqoqin a cikin takardu da kuma kaset na ji. Wasu an same su ne a ofisin xinsu wasu kuma a gidajensu.

### 3.3.3 Karanta Waqoqin Marubutan

An karanta waqoqin marubutan da aka gabatar da bincike a kansu da kuma nazari a kan waqoqin, inda aka fito da duk abubuwan da aka a yi nazari a ciki, da kuma neman qarin bayani a wajensu a kan duk abin da ake buqatar hakan.

### 3.3.4 Ganawa da Masana a Fannin Adabin Hausa

A yayin tattaro bayanan gudanar da wannan binciken an samu nasarar tuntuvar masana da manazarta daga jami'o'i da kwalejoji daban-daban waxanda suke da alaqa da wannan bincike.An gana da wasu malaman Sashen Koyar da Harsunan Nijeriya na Jami'ar Bayaro Kano da wasu malamai na Jami'ar Ahmad Bello Zariya na Sashen Hausa da wasu malamai na Qwalejin Sa'adatu Rimi ta Kano. Masanan sun ba da gudummawa qwarai da gaske wajen kammaluwar binciken.

### 3.3.5 Ziyara Xakunan Karatu da Cibiyoyin Ilimi

An ziyarci xakunan karatu na wasu jami'o'i mabambanta waxanda ake koyar da harshen Hausa da nazarinta, kamar: Babban Xakin Karatu na Jami'ar Bayero, Kano da Xakin Karatu na Sashen Koyar da Harsuna da Al'adun Afirka da ke Jami'ar Amadu Bello ta Zariya. Haka nan an ziyarci Xakin Karatu na Sashen Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero, Kano da Xakin Karatu na Cibiyar Binciken Harsunan Nijeriya da Fassara da kuma Hikimomin Al'umma, Jami'ar Bayero, Kano.

Daxin-daxawa an sami littattafai da muqalu da kuma kundayen bincike da masana suka wallafa waxanda kai tsaye suka shafi jigo da zubi da tsarin rubutacciyar waqa. Wannan shi ne qarshen babi na uku da abin da ya qunsa.

## BABI NA HUXU
## KWATANTA WAQOQIN BELLO MUHAMMAD AJI MAI KARAMA DA SANI ABUBAKAR HOTORO

### 4.1 Gabatarwa

A wannan babin an kwatanta waqoqin waxannan marubuta ne guda biyu. An duba yadda suke amfani da fasahohinsu da tunaninsu wajen tsara waqoqin nasu, musamman dangane da abin da ya shafi jigo, inda aka kalli jigogin kamar haka: jigon yabo da jigon nasiha da gargaxi. Ta vangaren zubi da tsari shi ma an duba zubi da tsari na gaba xaya da kuma zubi da tsari na cikin baitoci. Sannan kuma an kwatanta su ta hanyoyin da aka faxa a sama. Wato Bello Muhammadu Aji Mai Karama (daga yanzu Mai Karama) da kuma Sani Abubakar Hotoro (daga yanzu Sani). Sannan an yi amfani da kawo misalan baiti ko baituka daga marubuci, sannan shi ma marubuci na gaba sai aka kawo waqarsa xaya. Bayan an yi haka kuma, sai aka kwatanta baitukan da aka kawo daga qarshe.

### 4.2.1Jigo

Jigo shi ne saqon da marubuci yake son isarwa ga al'umma ta cikin waqarsa. Saboda haka an duba jigo ta waxannan abubuwa: kamar yadda ya zo a Xangambo (2007).

### 4.2.2 Jigon Yabo

Waxannan marubuta suna da waqoqi masu jigon yabo da dama. A waqoqin Mai Karama akwai masu yabo kamar haka:

1.Mijin Aisha
2. *Khatumul Ambiya'i'*
3. *Wasilah*
4. Matsayi Nasa

Har ila yau a vangaren Sani ma akwai irin waxannan waqoqi masu jigon yabo kamar haka:

1.Mai Cikar Xaukaka
2. *Khairil Bariya*
3. Kai Nake Qauna
4. Abin Koyi

Yabo babban jigo ne a waqoqi musamman waxanda suke da tasirin addini.Waxannan marubutan sun yi amfani da wannan jigon a cikin waqoqinsu. An yi nazarin jigon yabon Annabi Muhammadu,Sallalahu Alaihi Wasallam,don fito da gwala-gwalan kalmomin da su marubutan suka yi amfani da su a ciki. Bayan yabon Annabi, yabo zai iya kasancewa yabon xaya daga cikin waxannan;yabon halaye da yabon nasaba da yabon mahaifa da yabon makusanta da yabon jarumtaka da yabon asali da yabon zumunci da kuma yabon kyauta da sauransu.

Da farko Mai Karama a Waqar *"Khatumul Ambiya'i",* watoxaya ce daga cikin waqoqin da aka xauka aka yi nazari, an yi mata take ne da suna na Annabi Muhammadu Sallalahu Alaihi Wasallam, wato ''*Khatumul Ambiya'i'',* *ma'ana*(Cikamakin Annabawa). Akwai baitukan da aka yi nazari aka gamsu da jigon waqar yabo ne. Ga misalan kamar haka :

Tun da farko na kirayi,
Sunan Allah *Buwayi*,
Taimake ni ka sa ni yayi,
Nai yabo a gurin masoyi,
Har abada ba zan bari ba.
(Mai Karama, *'Khatumul Ambiya'i'* bt. 1)

A wannan baitin, marubucin ya fara saka xan ba a jigon waqar, shi ne baitin farko, kuma tun daga nan jigon waqar ya fara. Marubucin ya bayyana abubuwan da zai yi, inda ya fara neman taimakon Allah, sannan kuma ya ci gaba da bayanin abin da zai yi kamar haka "Nai yabo a gurin masoyi". Haka ya qara da tabbatar da niyyarsaa kan xorewa da yabo, "Har abada ba zan bari ba". Wannan kalmomi ne da suka fara nuna jigon waqar.

Shi kuma Sani, awaqarsa mai taken ''*Kai Nake Qauna*'' ya yi wa Ma'aiki Sallalahu Alaihi Wasallam, baitoci da suke nuna yabo, ya yi amfani da kalmomin yabo kuma waxanda suke nuna yabon ne qarara. Misali.

Yabon Manzo a yau zan je,
Bege nasa za na je a guje,
*Rabbana* lamintamin na je,
Nai ta rera yabo ga *Imamina*.
(Sani, ''*Kai Nake Qauna*'' bt. 12)

Wannan baitin ya nuna irin kalmomin da Sani ya yi amfani da su don tabbatar da jigon waqarsa, misali ''Yabon Manzoda Bege nasa za na je, da kuma nai ta rera yabo''.

Ta la’akari da waxannan baitukan da aka kawo marubutan sun sami kamanci, saboda waqoqi ne na addinin Muslunci, sannan kuma wanda su ka yi wa waqar shi ma mutum xaya ne, haka duk waqoqin yabo ne.

Wani abin sha’awar ma duk marubutan sun nemi taimakon Allaha kan waqar da za su yi ga abin da Mai Karama ya ce “Tun da farko na kirayi”, sai a xango na biyu ya qara da cewa “Sunan Allah Buwayi”, sai ya qara da “Nai yabo a gurin masoyi”. Shi Mai Karama taimakon da ya nema zai yabi Ma’aiki wanda kuma yana ganin yabon ya zama aiki a wajensa. Sani shi ma sai ya ce “Rabbana lamintamin na je’’, a qarshen baiti sai ya qara da cewa ‘’Nai ta rera yabo ga Imamina’’. Ya roqi Allah shi ma ya ba shi dama saboda yadda ya xauki yabon ibada ne ba ma ranar dainawa.

Har ila yau, marubutan a cikin waqoqin sun qara tabbatar da jigon waqoqinsu kamar haka:

Mai Karama ya bayyana Manzo da cewa:

Manzo dattijo ne xan dattijan,
Shugaban na mutum da aljan,
Shi*Munirin* ne *Sirajan*,
Mu rike shi ya kai mai Aljan-,
Narsa mita yabonsa babba.
(Mai Karama, ‘‘*Khatumul Ambiya’i*’’ bt. 6)

A wannan baitin Mai Karama ya ci gaba da tabbatar da jigonsa na yabo, sakamakon yabon halaye da nasaba ta Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam. Yana nuna yabonsa, yadda ya ce: ‘’Manzo dattijo ne xan dattijan’’, sannan ya qara da

“Shugaban na mutum da aljan” haka yake Ma’aiki shugaba” ne, ga kowa da kowa, sannan ya ce “Shi *Munirin* ne *Sirajan*”,wato abin nufi da (mai haske wanda ake gane abin da ya haska) ko wato iya wannan kawai ya nuna jigon waqar yabo ne domin kalmomin da marubucin ya yi amfani da su na yabo suna da yawa a ciki.

Shi kuma Sani a xaya vangaren ya nuna cewa:

Ya fitar da ruwa a yatsunsa,
Xaha ba famfo ba ne gunsa,
Ba mita babu dam a jikinsa,
Isarsa ka kawai a gun Sarkina.
(Sani, ‘‘*Kai Nake Qauna*’’, bt, 15)

Ya fito da mu’ujizar Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, a lokacin da ya shayar da al’umma da hannunsa, saboda da isar da yake da ita a wajen Allah shi ne ya sami wannan baiwar. Yabon baiwa ga xan‘adam tana daga cikin abubuwan da ake yabonsa da ita. Waxannan kalmomin da marubucin ya yi amfani da su, kawai sun isa su tabbatar da halin Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,na kyauta da sadaukarwa da kuma son al’ummarsa.

Waxannan baitukan suma wasu ma’aunai ne na samun kamanci a waqoqin waxannan marubuta kamar yadda Mai Karama ya ce “Shugaban na mutum da aljan”,wato shugabancinsa na mutune da aljanu, wannan ma mu’ujiza ce kamar yadda Sani shi ma ya yi yabon ga Ma’aiki ta hanyar duba wata mu’ujiza da yake da ita inda ya ce “Ya fitar da ruwa a yatsunsa”, har zuwa qarshen baitin. Ashe

kenan, yabo kan iya zama na nasaba ne ko kuma na wata baiwa da Allah ya ba wa mutum.

Bugu da qari, Mai Karamaya ci gaba da kawo kalmomi na yabo a cikin waqarsa, ga abin da baitin marubucin ya faxa.

Ya mafi hasken lamiri,
Ya Ma'aiki mai sururi,
Mai yawan bautar Naziri,
Ya lazamci istigafari,
Bai tava savawa Rabba.
(Mai Karama, ''*Khatumul Ambiya'i*'' bt. 7)

A cikin wannan baitin, jumlolin da aka kawo duk akwai kalmomin da suke nuna yabo, misali: "Mai yawan bautar Naziri", wannan kawai a cikin baitin nan ta isa a yi taqama da ita sannan kuma duk wanda aka faxawa kalmar ya san an yabe shi. Mai Karama ya nuna bautar da Ma'aiki Sallalahu Alaihi Wasallam,yake wa Allah ba kaxan ba ce. Ya qara da cewa "Ya *lazamci istigafari".* Bayan mai yawan bauta, ga shi mai yawan tuba a wajen Allah. Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,yana cewa a Hadisi "Shi yana tuba ga Allah a rana sau xari, a wata faxar kuma sama da saba'in a rana" duk da kuma shi Allah ya gafarta masa amma ya fi kowa neman tuba,(*Libabul Hadis* Babi na 23 Hadisi na 8). Marubucin ya qara yabonsa da cewa "Bai tava savawa *Rabba"* Manzan,Sallalahu Alaihi Wasallam,bai ta va savawa Allah ba, amma kuma ya fi kowa neman tuba.

Har ila yau kuma, Sani ya qara jaddada wannan jigo na yabo inda yace:

Duk halitta wa aka ba wannan,
Annabawa da *Mussalan*nan,
Duk ciki nasu babu mai wannan,
Sai xan Abdullah da Amina.
(Sani, ‘‘*Kai Nake Qauna*’’ bt, 16)

A qarshe ma sai kawai ya yi bayanin yadda Allah ya xaga Ma’aikiSallalahu Alaihi Wasallam, da wannan baiwa domin duk halitta da Annabawa ba mai irin wannan baiwar. Wannan ya qara tabbatar da ya dace, ya yaba wa Ma’aiki saboda irin wannan kyautar da aka yi masa. Sannan wannan kawai ya nuna yadda Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ya zama abin yabo saboda irin wannan abun da ya kevanta ga al’umma, ta fuskar yadda ya shayar da ruwa ba tare da akwai dam ko wani abu da zai jawo ba.

Kamancin waxannan marubutan a nan sun qara bayyana halaye da kuma girman da Allah ya ba shi da kuma xaga shia kan dukkan hallita.

Duk da haka kuma, an sami bambanci a cikin baitocin musammam inda Mai Karama ya ce “Bai tava savawa *Rabba”*. Wannan wani hali ne da Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ya fifita ga duk hallita,saboda shi a rayuwa bai tava savawa Allah ba. Amma ta vangaren Sani kuma shi a cikin baitin sai ya kalli girma na Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, da kuma wannan mu’ujizarsa.

Haka kuma Mai Karama,a cikin waqa ya qara kawo baitukan da suke qara tabbatar da jigon yabo.

Na faxa kogin san *Nabiyu*,
Ga fiyyayen xan fiyyayu,
Gwarzo siriki ga Aliyu,
Ya fi kowa san marayu,
Har mai iyayen bai bari ba.
(Mai Karama, *''Khatumul Ambiya'i'' bt.* 12)

Mai Karama ya qara da yabon halaye ta amfani da kalmomin da suke nuna girma da darajar iyayen Ma'aikiSallalahu Alaihi Wasallam, ya ce "Ga fiyyayen xan fiyyayu". Shi Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, fiyyaye ne, to haka mahaifansa. Duk da haka ya ce "Ya fi kowa san marayu". Ma'aiki ya fi kowa son marayu, har mai iyayen ma Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ya fi su son 'ya'yansu. Ma'aiki saboda halinsa na kirki ya fi uwa son xanta, wannan hali ne nagari kuma abin koyi. Marubucin ya ci gaba da baitukan da suke qara nuna yabon ya riqe shi aiki kuma ba shi da lokacin da zai tsaya.

Amma vangaren Sani, haka ya ci gaba da kawo baitukan da suke nuna yabon Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,da kuma nuna tabbacin kamarsa ba za a samu ba, ga yadda ya ce a baiti na gaba.

Kai kamarka ba za a samu ba,
Matsayinka ba za a qara ba,
Kai kaxai ne Annabi babba,
Jagora kuma *Miftahul Janna*.
(Sani, ''*Kai Nake Qauna*'', bt. 17)

A wannan baiti marubucin ya yi mai gaba xaya inda ya tabbatar da cewar ba kamar Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, har abada ba za a yi ba, sannan matsayinsa ma haka, kuma shi ne shugaban Annabawa da al'umma, sannan

shinemai buxe Aljanna. Waxannan kalmomi da suka fito a wannan baiti su kansu sun daxa nuna yabo shi ne jigon wannan waqar.

A waxannan baitocin marubutan sun ci gaba da yaba wa Ma'aiki kamar yadda Mai Karama ya ce "Ga fiyyayen xan fiyyayu da Ya fi kowa san marayu" waxannan kalmomi sun qara nuna jigon da ake magana na yabo, tabbas Mai Karama ya ci gaba da qarfafa jigonsa. Haka Sani ya ci gaba da bayyana wannan jigon da yake kai na yabo wanda kuma shi ya qara nuna kamanci a ciki. Sani cewa ya yi "Matsayinka ba za a qara ba, Kai kaxai ne Annabi babba"

Sannan kuma Sani ya kawo girman na Ma'aiki da kuma nuna yadda ya zarce al'umma, kuma ya zamo don girman nashi, shi ne ma wanda zai buxe *Aljanna.*

Haka kumaMai Karama ya qara da cewa.

Ni yabon Manzo nake yi,
Wanda ka san bai shige yayi,
Ko a da can ma anayi,
Xan Abdullah xan Qusaiyi,
Mai binsa ba zai rashi ba.
(Mai Karama,*"Khatumul Ambiya'i''*, bt.13)

Bayan ganin yadda marubucin ya riqa yabon Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, a qarshe ma sai ya qara da yabon mahaifi da kuma kakansa, wannan ya qara fito da jigon waqar na yabon Ma'aikiSallalahu Alaihi Wasallam, a ciki.

Amma a wajen Sani kuma, marubucin ya qara tabbatar da yabon da kuma hujjarsa ta ba ranar da zai bar bege, shi kullum aikinsa kawai yaba waMa'aiki Sallalahu Alaihi Wasallam,ya qara da cewa:

Tsarkakakke mai cikar tsafta,
Hali nasa babu mugunta,
Kai nake wa yabo na nanata,
Qaunarka ta cikan raina.

Ni a nan ne zana taqaita,
Ko in ce nan Sani zan huta,
A yabon Manzo da na rubuta,
Na karanta don bayyana qauna.
(Sani,‘‘*Kai Nake Qauna*’’, bt. 20-21)

A waxannan baitoci da aka kawo, musamman kalmomin sun tabbatar da jigonsa shi ne ‘‘yabo’’. Haka kuma a kowanne baiti akwai kalmomin da ko babu su, to waxannan za su iya wakiltar su, domin tabbatar da kalmar yabo ‘‘Tsarkakkake mai cikar tsafta”, duk wanda aka gayawa waxannan kalmomi ko iya ita kaxai ce zai yi godiya domin kalmomin yabo ne. Wannan kenan ya qara tabbatar da waqar yabon Ma’aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ne.

Ta vangaren kamanci a waxannan baitoci kuwa, sun yi furucin gundarin qwayar jigo a ciki misali. Mai Karama ‘‘Ni *yabon* Manzo nake yi” Haka Sani ya ce “A yabon Manzo da na rubuta” wannan alaqar ta waxannan kalmomi sun fito da kamancin jigon yabona waxannan marubutan, guda biyu, wato Mai Karama da kuma Sani.

### 4.2.3 Jigon Nasiha

Haka kuma waxannan marubuta suna da waqoqi masu jigon nasiha da dama, a waqoqin Mai Karama akwai:

1. Farkon Halitta

2. Sha Rubutu

Ta vangaren Sani ma akwai irin waxannan waqoqi masu jigon nasiha kamar haka:

1. Shugaban Bayin Allah

2. Abin Koyi

Nasiha ita ce yi wa mutum hannunka mai sanda don ya lura da wasu abubuwa na rayuwa ko dan ya guje su ko kuma ya aikata su a rayuwa. Waxannan marubutan duk sun yi waqoqi masu jigon nasiha.

Mai Karama ya yi waqarsa mai suna*"Farkon Halitta"* don jama'a su gane girman Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam. A cikin waqar ya yi baituka na nasihaa kan kowa ya yarda ya sallama wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, saboda isarsa.Ga abinda yake cewa:

Ku ji ni ya *Ikwani*,
*Adi'ullaha wal ma'amuni,*
*Rasullah* ga dukkan *Kauni*,
Aya ta nuna *badadina*.
(Mai Karama, ''*Farkon Hallita*", bt.9)

Wannan baitin tun daga nan marubucin ya fara kawo jigon waqar ta hanyar kawo ayar Alkur'ani cikin *Suratul Al'imran* aya ta 30. Wannan baiti ya haskaka wannan jigo na nasiha kamar yadda marubucin waqar ya yi nasiha don jama'a ta

sani bin Allah da Ma'aiki umarni ne na Allah, kuma shi ne abun da ya dace ga dukkan wani mutum Musulmi ya yi.

Amma shi kuwa Sani,a waqarsa mai taken ''*Shugaban Bayin Allah*'' wadda take nufin Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,shi ne mai wannan sunan. Saboda haka sai ya sawa waqar sunansa ko kuma laqabi da ake gaya wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam.

Marubuci ya yi nasiha ga al'umma kan lalle ne kowa ya sallama wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, saboda girma da darajar da Allah ya ba shi, ga yadda baitin ya kasance:

Malam rayuwa ba tai amfani ba,
In ba ta sallama wa jagorana ba,
Kuma qarshe ta sha azaba da *uquba*,
Ba jinqai ga wanda bai so Manzo ba.
(Sani, ''*Shugaban Bayin Allah*'', bt.12)

Marubucin ya yi nasihar da nuna duk wanda yake ganin akwai wani abu da ya rage a cikin sha'anin Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, to ya sake tunani, ta inda ya nuna babu amfani ga duk wanda bai yarda da irin baiwar da Allah ya yi wa Manzo Sallalahu Alaihi Wasallam,ba.

Waxannan marubutun an sami kamanci na jigo a cikin waxannan baitukan da aka kawo, duk sun yi nasiha da sanin girman Ma'aiki. Mai Karama yana cewa

"*Adi'ullaha wal ma'amuni".* Sani shi ma a nasa baitin sai ya ce "Ba jin qai ga wanda bai so Manzo,Sallalahu Alaihi Wasallam, ba". A nan duk sun kawo yadda Ma'aiki Sallalahu Alaihi Wasallam,yake a wajen Allah.

Sannan kuma, an samu a cikin baitocin an yi amfani da kalmar Larabci, Mai karama (*Ikwani* da *Adi'ullaha),*wato 'yan'uwa da kuma a bi Allah.Sannan Sani kuma (*uquba*) azaba ke nan. Duk waxannan kalmomin marubutan sun yi amfani da su,domin nasiha ga al'umma ta amfani da su ne aka gina jigon nasiha a waqar.

Haka kuma Mai Karama ya qara nasiha da bin Allah, sannan da iyaye a baitin na gaba.

Allahu shi ya yi bayani,
Uwa uba har kakanni,
Da dukkanin mai imani,
In ya so Muhammadu gatana.
(Mai Karama, ''*Farkon Hallita*',bt.10)

Bayan Allah da Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,sai kuma iyaye su ya kamata abi su, saboda yadda Allah, Subuhanahu wa Ta'ala, ya faxa a yi musu biyayya, waxannan kalmomin da marubucin ya kawo da bayaninsu sun qara ba da haskea kan wannan jigo na nasiha.

Amma ta vangaren Sani, sai ya qara bayani kamar haka:

Baban Faxima masoyin dukka bayi,
Duk bauta da kai kaxai za a yi koyi,
Kuma qaunarka wajibi ce gun bayi,
Wanda ya qika Sidi bai yi nagarta ba.
(Sani, ''*Shugaban Bayin Allah*'', bt.15)

A wannan baitin, Sani ya qara tabbatar da abin da yake nufi ta hanyar wasu layukan da suka biyo. Misali ''Duk bauta da kai kaxai za a yi koyi", ashe kenan, duk wanda bai yi koyi da Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ba, to ya yi asara

Ta amfani da waxannanbaitukan da marubutan suka kawo, wani vangare na aya a cikin baitukansu, Mai Karama, ayar da ta nuna cewa abi Allah,Subuhanahu wa Ta'ala, da Manzansa,Sallalahu Alaihi Wasallam,*Suratul Muhammad,*aya ta 33,sannan kuma abi iyaye. Haka abin yake a wajen Sani sai ya kawo ayar da ta yi maganaa kan ayar da Mai Karama ya kawo ta abi Allah abi Ma'aiki, ta haka ne suka qara tunatar da al'umma ta yi musu wannan nasihar, don tabbatar da jigonsu.

Bugu da qari, suka sake samun kamanci wajan tabbatar da nasihar soyayyar Ma'aiki ita ce imani, duk wanda ya kauce ta, fa ba zai sami rahama ba.

A vangaren bambanci kuwa, Mai Karama ya kalli nasihar ta hanyar soyayya da kuma biyayya ga Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, amma shi kuma Sani sai ya kalli baitin ta soyayyar Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,ita ce tsira a rayuwa.

Har ila yau, Mai Karama a baiti na gaba ya qara qarfafar jigonsa da:

Allahu ka ji qaina ni,
Uwa uba har kakanni,
Da dukkanin mai imani,
Sai ya so Muhammadu gatana.
(Mai Karama, '*'Farkon Hallita*'', bt.11)

Marubucin yana nasiha da ya kamata duk Musulmi ya riqa yin addu'a ga iyaye da kuma duk wanda ya riga shi imani, kamar yadda *Alkur'ani* ya ce: "Wanda suka riga ku imani ku riqa nema musu gafara",*Suratul Hashr*, aya ta 10.

Idan aka duba Sani kuma, sai a ga ya qara bayyana wata nasihar a wannan baitin.

Kyan siffa da kyan hali ka wuce kowa,
Tsarkin zuciyarka ta nashe ta kowa,
Domin kai Ubangiji ya yi wa baiwa,
Don baiwarka xa ba za ya kwatanta ba.
(Sani, ''*Shugaban Bayin Allah*'', bt.16)

Marubucin daga qarshe ma sai ya rufe da cewa ''Don baiwarka xa ba za ya kwatanta ba" Wato duk tunanin mai tunani, to ba zai iya kwatanta yadda Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, yake a wajen Allah ba. Wannan ta sa ashe ya kamata ya qara nasiha da sanin yadda Ma'aiki ya kasance.

Marubutan sun haxu a kan jigonsu na nasiha, da qara sanar da jama'a matsayin Ma'aikin Allah, kamar yadda suka yi nasiha da haka, ta hanyar nuna girmansa.

Amma ta vangaren bambanci kuwa, Mai Karama a wannan baitin roqo ya yi da addu'a ga Allah da ya yi masa rahama da duk wani wanda ya yi imani. Amma ta vangaren Sani kuma, sai ya ci gaba da bayanin yadda Ma'aiki yake a wajen Allah "Tsarkin zuciyarka ta nashe ta kowa", sannan ya nuna har yau har gobe sanin Ma'aiki sai Allah.

### 4.2.3 Jigon Gargaxi

Marubutansuna da waqoqi masu jigon gargaxi, daga cikin waqoqin Mai Karama masu jigon gargaxi akwai:

1. Girman kai
2. Girman Sahabbai

Amma a vangaren Sani ma akwai irin waxannan waqoqi masu jigon gargaxi kamar haka:

1. Ubangijin Halittu
2. Tarbiyya

Gargaxi jan kunne nea kan wani abu wanda wani ko wasu suke aikatawa da ya sava da yadda al'umma take akai. Hakan ya sa in har ana son jama'a ta gyara to sai a gargaxe su, sannan a kuma yi musu bayanin illarsa idan har sun ci gaba da aikata wa. Marubutan waqoqin sun kasance masu jan kunne ga al'ummaa kan waxansu halaye da jama'a suke aikata wa waxanda kuma sun sava, sannan yin su kuma to akwai irin tanadin da Allah ya yi wa masu irin hali.

Wannan waqar mai taken ''*Girman kai*'', tana xaya daga cikin waqoqin da aka duba ta Mai Karama, inda aka duba jigonta da nazarinsa.

Na yi kiranku fa 'yan'uwa,
Ku bar girman kai gaba xaya.
(Mai Karama, ''*Girman Kai*''bt. 7)

Mai Karama ya yi gargaxi ga masu girman kai cewa su sani qarshensu ba zai yi kyau ba, sannan daga baya ya nemi al'umma ya kamata su daina wannan xabi'a.

Haka kuma Sani, shi ma an duba waqarsa mai suna "*Ubangijin Hallitu*" inda ya yi gargaxi nea kan mayar da martani ko raddi,a kan wasu da aka samu sun yi wani zane na hoto suka kwatantashi ga Ma'aiki. Marubucin ya yi waqa don gargaxar masu wannan hali. Ga yadda shi ma ya tsara baitukansa kamar haka:

*Alai* haxa Sahabbai,
Su suka xau takubbai,
Sun sare wasu Kafirai,
Don kare Annabina.
(Sani, ''*Ubangijin halittu*'', bt.4)

Wannan baitin ya nuna ya fara da gaisuwa ga Sahabbai, sannan ya ci gaba da bayanin yadda Sahabai suka kare Ma'aiki, sun yi gwagwarmaya sosai a ciki.

Waxannan baitukan da aka kawo sun zama kamar sharar fage nea kan jigon, duk da in aka duba baitin Mai Karama za a iya cewa tun a nan jigon waqar ya fito "Ku bar girman kai gaba xaya". Kuma ya yiwa masu wannan halin bushara da qarshensu lalle sakamakon da za su samu shi ne na tavewa.

Har ila yau Mai Karama, ya ci gaba da gargaxin da ya fara.

Mu bar girman kai yan 'uwa,
Qarshensa yana kawo tsiya.
(Mai Karama, ''*Girman kai*'', bt. 8)

Girman kai rawanin tsiya. Ya zama ke nan duk mutumin da ya kasance ba ya jin gargaxi to qarshensa ba zai zama ya yi kyau ba. Amma a vangaren Sani, ga abin da yake cewa:

Kuxin fetur aka qara,
Muka fito muna ta qara,
Muna ta ta da qura,
Wai gwamnati tai varna.
(Sani, ‘‘*Ubangijin Halittu”*, bt.5)

Marubucin ya yi gargaxi ga dukkan Musulmai a kan yadda yanzu ake xaukar soyayya ta abin duniya kamar ta fi ta AnnabiSallalahu Alaihi Wasallam.

Alaqar waxannan baituka shi ne kalmomin da aka yi amfani da su, Mai Karama ya ci gaba da gargaxin da ya xauko, sannan a qarshe kuma ya nuna makomar mai yin girman kai. Amma a vangare Sani sai ya ci gaba da gargaxin da ya faro tun a baitin farko da aka kawo yake cewa, “Muna ta ta da qura, wai gwamnati tai varna”.

Bambancin kuwa Mai Karama jigon ya kawo kai tsaye da, amma Sani har yanzu yana maganaa kan tarihin abun da ya faru har ya yi wannan waqa, mai jigon gargaxi.

Xadin daxawa Mai Karama, ya jero wasu mutane wanda sakamakon girman kai suka dauwama a cikin wuta, sai ya ce:

Fir’auna ma yai shisshigi,
Ruwa ya haxe shi gaba xaya.

Qaruna ma yai isgili,
Qasa ta haxe shi gaba xaya.

Lamarudu ma yai bai ji bari,
Qarshe an sa shi a *Hawiya.*
(Mai Karama, ‘‘*Girman Kai”*, bt.10-12.)

Waxannan baitukan kawai sun isa ba da tsoro ga mai yin girman kai, saboda tsoratarwa da marubucin ya yi a cikin waxannan baitukan kamar haka“qarshensa yana kawo tsiya”, marubucin ya tabbatar da qarshe mai wannan hali zai zama bai yi dace ba. Saboda nuna illar yin girman kai a ciki sai ya qara da kawo misalan waxansu bayin Allah, wanxanda a qarshen rayuwarsu sun tave, kamar Fir’auna da Lamarudu da kuma Hamana, waxanda a qarshen rayuwarsu sun zama tavavvu, ashe duk mai hali irin nasu zai kasance ya yi mummunar makoma.

Haka abin yake a vangaren Sani, ga abin da baiti na gaba ya faxa:

Muka rinqa zanga-zanga,
Wasu na ta yaga riga,
Yau Annabi aka zaga,
Mai mukai a zamanina.

Duk da ban da sanda,
Banda bindiga da adda,
Shi ne na yo *qasida*,
Don waqe Annabina.

Ya Ubangijin Halittu,
Wasu kafirai vatattu,
Su ne sukai rubutu,
Don kushe Annabina.
(Sani, “*Ubangijin Halittu*”, bt. 6,22-23)

Marubucin ya yi gargaxi da kakkausar murya a cikin waxannan baitukan inda ya gargaxi duk masu munanan kalamai ga Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam, da kuma yadda Musulmai suke xaukar soyayya ta abin duniya kamar ta fi ta Annabi. A baiti na farko ya yi jan hankali, inda ya tabbatar da yadda Sahabbai suka tsaya don kare Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, da duk abun da Allah ya ba su. Sai a baiti na biyu ya yi shaguve, haka a baiti na uku ya yi shaguve tare da tambayar da ba ta neman amsa. Mai saurare shi ne zai ba wa kansa amsa.

Haka ya ci gaba da yin shaguve a cikin wanxanan baitocin, kasancewar yanzu halin da al'umma take ciki kusan duk wani abu na kare martabar Annabi Muhammadu,Sallalahu Alaihi Wasallam,, sai abin ya zama kamar yanayin baya, sai waxansu abubuwa na rayuwa su ake fifitawa, kuma su ake neman karewa.

Dadin daxawa, marubucin ya yi magana da kakkausar murya a kan masu wannan aqidar ta faxar kalaman vatanci ga Shugaban Hallita. Ya ci gaba da yi gargaxi ga mutane, da su guji masu yi wa Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam, maganganu na vatanci, kuma su tashi su kare shi da duk irin damar da Allah ya ba su. Shi ya sa ya nuna da ba shi da qarfin hanawa, to bari ya yi amfani da abin da yake da shi, wato harshensa, shi ne ya yi qasida don ya kare Annabi Muhammadu,Sallalahu Alaihi Wasallam. Wannan ya yi daidai da Hadisin Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam, da yake nuna duk wanda ya ga wani abin qi ya

hana shi da ikonsa ko qarfinsa, ko ya qyama ce shi a cikin ransa. (*Arba'una Hadis* Hadisi na 34).

Alaqar waxannan baitoci shi ne, duk baitukan da aka yi nazari gargaxi shi ne jigonsu, sannan marubutan sun yi waqoqin ne cikin harshen Hausa.

A waxannan baitocin Mai Karama dukkansu ya xauko bayaninsu daga cikin *Alkur'ani*, amma Sani sai ya yi gargaxi da abubuwan da suka faru na vatancin da yake faruwa a yanzu. Sannan vangaren Sani ya yi amfani da kalmomin Larabci da kuma kalmomin da suke nuna wasu kayan da ake amfani da su don yaqi ko faxa. Amma Mai Karama ya yi amfani da kalmomin Larabci ne kawai, bayan na Hausa da suka rubuta waqoqin akai.

### 4.2.4 Jigo a Gajarce

Jigo a gajarce hanya ce da mai nazari yake taqaita abin da waqa ta qunsa ta bin baiti bayan baiti ba tare da yin cikakken sharhi a kanta ba. Manazarci yana duba muhimman wurare ne na waqar yana fito da su daki-daki.

Ta vangaren Mai Karama, an duba waqar ''*Xan Suwaiba*''. Marubucin waqar ya sa mata wannan suna ne saboda ya ba da labarin rainon Ma'aiki a ciki. Haka kuma ya yi bayanin yadda aka tsaga qirjinsa. Nana Suwaiba kuma tana xaya daga cikin waxanda suka raine shi.

Wannan waqar tana xaya daga cikin waqoqin da aka yi nazari a kai, an taqaita jigonta ne kamar haka:

Baiti.1-4 Mabuxin waqa/Addu'ar farawa, salati da yabon Annabi, Sallalahu Alaihi Wasallam,da Sahabbai da kuma waliyai.

Baiti. 5-16 Bayani tsaga qirjinsa Annabi,mai tsira da amincin Allah.

Baiti. 17-Mayar da shi garin Makka.

Baiti. 18-24 Bayanin nemansa a Ka'aba.

Baiti. 26-27 Addu'ar rufewa.

Amma a vangaren Sani, an duba waqarsa kuma aka taqaita ta waqarsa mai suna *Mai Qur'ani*kamar haka:

bt.1-9 Addu'ar farawa/ salati ga Ma'aiki da Sahabbai.

bt.10-19 Bayanin girman Annabi Muhammadu, mai tsira da amincin.

bt.20-25 Bayanin darajar Alkur'ani.

bt. 26- 35 Shawara da falalar karanta Alkur'ani.

bt. 36- 40 Addu'ar rufewa.

Alaqar waxannan marubuta ta hanyar duba waxannan waqoqi guda biyu shi ne, yin amfani da jigo da kuma mabuxin waqa da maqullinta.

Ga misalin, Mai Karama a cikin aqarsa ta "*Dan Suwaiba"* yana cewa:

Bismillah ni da farko kai na roqa,
Ya *Ilahu Rabbu* maqagin *halaqa*,
Kai mutane kai dabbobi kai *Buraqa*,
Ba ni haske ni Bello na shirya waqa,
Ka sa ba kuskure baiti yai ta zuba.

Na roqe ka *Tabara* kai min agaji,
Nai kiranka kai min agaji,
Wanga waqa zan yi ne kan buxe qirji,
Na Muhammadu mai kyau in faxe shi ku ji,
Yan da aka wanqe zuciyarsa xan Suwaiba.
(Mai Karama, "*Xan Suwaiba*", bt,1-2)

Amma ta vangaren Sani kuwa, ga yadda abin yake a waqarsa mai suna*Mai Qur'ani*.

*Bismilla*ni zan fara,
Na yi kiran Sarki Allah *Rabbani*.

Da farko waqar nai *ta'awizi*,
Ina neman tsarin Shaixani.

Sarkin da ba shi da xa ko,
Mata balle ta haifi Usaini.

*Tabara* Allah shi ya kaxaita,
Cikin *Zati* Allah *Rabbani*.
(Sani, "*Mai Qur'ani",* bt, 1- 4)

A nan marubutan sun tsaya kan jigonsu, sannan kuma sun yi amfani da mabuxin waqa duk sun fara da sunan Allah da yabon Annabi da kuma Sahabbai.

Amma ta vangaren bambanci kuwa, Mai Karama ya kalli yadda aka tsaga qirjin Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, da kuma yadda aka raine shi, amma Sani shi kuma ya yi wa Alkur'ani waqa ne ya faxi darajojinsa da kuma girmansa. Mai Karama a wannan waqarsa da aka duba baitocinta 27, amma ta Sani Baitoci 40 ne.

Buxewa da rufewa wani tsari ne da aka samu duk marubutan suna amfani da shi a cikin waqoqinsu, misali :

Mai Karama a waqar ‘‘*Farkon Halitta*” ga yadda ya yi amfani da buxewa da rufewa:

*Bismillah Allah Rabbani,*
Allahu ni ma ka haskani,
In waqe *Sayyadil Kaunaini*,
    Muhammadu shi ne gatana.

Ya *Rabbi Allah Rahamani*,
Domin ni in ka haskani,
Buqata Allah babu saura ni,
    Sai dai in waqe *Badadina*.

Yi dubun salati Rabbani,
A gareshi xan Adanani,
Mata da ‘ya’ya nai imani,
    Ba kamarsa Xaha *Badadina*.

Bari in saka da Sahabbaini,
Abubakar nasu da Umar ni,
Aliyu Usman Zul Nuraini,
    Domin sun so shi *Badadina*.

Sa da Abdulqadir Jilani,
Shaihunmu Ahmadu Tijjani,
Na haxa da *Gausul* zamani,
    Burhama shi ne tsanina.

Ya Rabbana kai min auni,
In koma in hau kan tsani,
In dinga baitika launi-launi,
    Domin in ba wa *Badadina*.

(Mai Karama, ‘‘*Farkon Halitta*” bt, 1-6)

Waxannan su ne kalmomin da marubucin ya yi amfani da su wajen buxe waxannan baitukan. Ya fara da sunan Ubangiji da salati da Sahabbai da kuma

waliyyai daga qarshen kuma sai ya nemi taimako wajen Allah don ya fara yin baitukan yabo.

Haka kuma a wannan baitin da aka kawo na qasa shi kuma misali na rufewa a cikin wannan waqar ta ‘‘*Farkon Halitta*”.

Na gode Allah *Rabbani,*
Tun da na haxe buqatani,
Na yabonsa shi Mai Qur’ani,
Xaha Muhammadu gatana.
(Mai Karama, ‘‘*Farkon Halitta*” bt, 12)

Marubucin ya rufe waqarsa da wannan baitin da yake nuna godiya ga Allah, saboda damar da ya ba shi na gama baitukan yabo.

Amma a vangaren Sani ga yadda wannan tsari yake na buxewa da rufewa a cikin waqar ‘‘*Abin Koyi’’*.

A gun Malamai na ji wani bayani,
Suka ce ayyuka ai ba sa muni,
Idan an kira *Arrahamani*,
To don haka ni ma Sani na sanya*Bismillah*.

Da sunanka Allah zana fara,
Nake addu'ar ka daxan basira,
Na shiryo yabon Manzo na rera,
Allah gareka nake nema ka qaran yawan falala.

Allah dukkan arziki na nan gareka,
Kana ba da kyauta ba a ba ka,
Don haka na yi sujjada gareka,
Daxa min basira zan yabon Annabin Allah.
Da tsiranka da aminci *Karimu,*
Ka qara wa jagoran cikinmu,
Wanda ka bai wa Kur'anin *Karimu*,
Ka zave shi a halitta ya zam Annabi Allah.

*Aminci* haxa *ahalin* gidansa,
Da mata dan 'ya'yan gidansa,
Haxa Shabbansa masu hidima gurinsa,
Ko'ina suna bisa don qaunarsu gun Annabin Allah.
(Sani, ‘‘*Abin Koyi’’* bt.1-5)

Waxannan baitukan na sama su ne misalan buxewa a cikin wannan waqar ta Sani. Da farko ya fara da sunan Ubangiji da salati da kuma Sahabbai da jama’ar gidan Ma‘aiki.

Marubucin a cikin wannan waqar mai suna‘‘*Abin Koyi’’*ya yi amfani da rufewa a cikinta ga abin da yake cewa :

Tammat a nan nake nufin na huta,
A yan baitukan da na yo na furta,
Na bege ga jagoran halitta,
*Ilahi* ka karvi yabon da nai wa *Rasulillah.*

Sunan mai yin wannan qasida,
Sani Abubakari mai qasida,
Mai son ya cika da kalmar Shahada,
Xan Hotoron da Kawo masoyin *Rasulillah.*
(Sani, ‘‘*Abin Koyi’’* bt.17-18)

### 4.2.5 Warwarar Jigo da Shimfixarsa

Wannan hanya ce da mai nazari kan duba waqa da yi mata sharhi a ciki da wajenta, ta hanyar yin bayaninta da danganta da wasu abubuwan da za su taimaka masa wajen fito da abubuwan da yake ganin waqar ta qunsa.

Ga yadda aka nuna wannan misali a waqar “*Girman Kai*” ta Mai Karama wadda jigon waqar shi ne “gargaxi” kamar yadda aka bayyana a baya.

Ni na yi kiranku fa ‘yan’uwa,
Ku bar girman kai gaba xaya.
(Mai Karama, “*Girman Kai*’’, bt, 6)

A wannan waqar, marubucin ya yi amfani da qwarewa da fasaharsa da kuma nuna tasirin da yake da shi a vangaren Larabci, ta inda yake xauko Aya ya kawo ta ko wani vangarenta cikin harshen Hausa, inda wani wajen yake kawo aya xaya ba tare da Larabci ba, ya fassara ta. Misali:

Gaba xaya sun bi umarni,
A ciki nasu sai qwaya xaya.
(Mai Karama, “*Girman Kai*’’, bt. 10)

Kamar yadda mai bincike ya bayyana jigon wannan waqar shi ne “gargaxi,” haka ya kasance a waqar inda marubuci ya kawo ayoyi da suka qara tabbatar da hakan, cikin *Suratul Hijir*, aya ta 33 da *Suratul Yunus,* aya ta 89, da*Suratul Ankabut*, aya ta 38-39 da kuma *Suratul Baqara*aya ta 31.

Ni na yi kiranku fa ‘yan’uwa,
Ku bar girman kai gaba xaya.

Mu bar girman kai ‘yan ‘uwa,
Qarshensa yana kawo tsiya.
(Mai Karama, “*Girman Kai”*, bt. 7-8)

Bugu da qari, marubucin ya yi nuni da irin nadamar da masu yin girman kai suke haxuwa da ita, inda ya fara kawo Shaixan, kamar haka:

A nan Shaixan kuma yaq qiyi,
Yai girman kai halin tsiya.

A nan*Rabbana* ya la’ance shi.
Sai ya watso shi a duniya.
(Mai Karama, “*Girman Kai”*, bt.10-11)

Shaixan shi ne wanda ya fara girman kai kuma a qarshe, sai Allah ya sauko da shi qasan duniya, sannan kuma Allah ya la’ance shi.

Sannan kuma marubucin waqar ya kawo su Fir’auna da Lamarudu da kuma Hamana inda ya nuna yadda qarshensu ya kasance. To, ashe ke nan duk wanda ya yi girman kai lalle zai kasance tare da waxannan da ya kawo a cikin waqar.

Fir’auna ma yai shisshigi,
Ruwa ya haxeshi gaba xaya.

Qaruna ma yai shisshigi,
Qasa ta haxe shi gaba xaya.

Lamarudu ma yai shisshigi,
Qarshe an sa shi a *Hawiya*.
(Mai Karama,“*Girman Kai’*, bt.13-15.)

Marubucin ya ci gaba da bayanin yadda su Fir’auna da Hamana da kuma Lamarudu suka kasance bayan sun yi girman kai inda a qarshe sun kasance cikin wuta.

Haka marubucin ya qara bayania kan amfanin ilimi, da kuma ribar da wanda ya yi ilimi yake samu, misali:

Shi ilimi doki ne ga kai,
Sai ka nema kuma kai juriya.

Ka yi ilimi xan’uwa,
Zuciyarka ka zam mai gaskiya.

Jaki ka san bai da ji,
Sai loda mar kayan wuya.
(Mai Karama,"*Girman Kai'*, bt.16-18.)

Waxannan baitukan qara nuna muhimmancin ilimi suka yi, saboda Ma'aiki ya ce "Neman ilimi wajibi nea kan dukkan Musulmi ko Musluma", sannan ya nuna yadda mai ilimi yake gane gaskiya. *Muktaril Hadis,Huruf* X, Hadisi na 11).Sannan ya kawo yadda mara ilimi yake kasancewa.

Daga qarshe kuma ya yi addu'ara kan Allah ya kare shi daga yin da-na-sani da nadama.

Ina roqon ka *Tabaraka*,
Ka tsare *qalbun*mu gaba xaya.

Mugun ji mugun gani,
Ka tsare mana *Rabbi* gaba xaya.

Shairin mutun ko aljani,
Kare mana *Rabbi* gaba xaya.

Na gode Allah ni nai yabo,
Nai Salati ga *Khairil Ambiya*.
(Mai Karama,"*Girman Kai'*, bt.19-22)

Marubucin ya ci gaba da addu'a kamar yadda yake marubuta waqoqin kan yi a duk lokacin da suka zo rufe waqarsu, sannan ya nemi taimakon Allah ya kare shi da dukkan sharri da kuma duk wani abun qi, Allah ya kare shi.

Amma a nan kuma Sani, an yi amfani da waqarsa ta "*Israi*" kamar haka:

Isra'i,shi ne tafiyar da Allah ya sa Ma'aiki ya yi daga qasa zuwa saman bakwai. Waqar tana daga cikin waqoqin da aka yi nazari. An yi nazarin abubuwa

da dama a cikinta. Baitocin farko su fara bayani ne a kan tauhidi, wato kaxaita Allah, baitocin sun dogara da surar da take cikin Alkur'ani ta *Suratul Iklas.*

*Arrahamani Rahim Lamyalid* kai ba ka haifa ba,
Sannan ba mata a gareka Allah balle ka yi uba,
Allah ba ka da kishiya ko qani fa ni na dudduba,
Ba farkon Allah Ahadin gwani Sarki Allah.
(Sani. "*Isra'i"*, bt:1)

Marubucin ya ci gaba a kan maqasudin waqar ya kuma fara bayani cewa soyayyar da Allah yake yi wa Ma'aiki, shi ne ma ya sa aka yi *Isra'i* da shi zuwa sama da kuma ba shi haquri ko rarrashinsa, saboda rasuwar matarsa Nana Khadija da kuma baffansa Abu Xalib, ya qara da cewa dalili na biyu:

Wannan shekarar Abu Xalibi ya mutu shi ma,
Sai kuma matarsa mai baiwa Nana Khadija ma,
Dukkansu biyu nan sun so shi Manzon alfarma,
Sai Rabbi ya xauke su manyan masoyan *Habibullah*.

Wannan dalili ma ya sanya an yi kiransa sama,
Domin rarrashinsa ga masoyi Manzon alfarma,
Sannan da nuna masa hallitu masu ibada ma,
Ko da mutun da Aljan ba sa yin bautar *Jallalah.*
(Sani. "*Isra'i*," bt. 7-8)

Sai karvo Sallah, marubucin ya ce shi ma dalili ne na*Isra'i* kamar haka:

Soyayya tsantsa shi ne dalilin tafiyar Isara'i,
Sai karvo Sallah shi ma dalilin tafiyar Isara'i,
Don duk Annabawa da mirsalai ba wanda ya yi,
Sai dai Muhammadu cikakken masoyin gun Allah.
(Sani. *Isra'i*, bt, 4)

Wannan baitin ya bayyana jigon waqar shi ne tafiya Isra'i da kuma Mi'irajin da Manzan Allah ya yi haka kuma ya tabbata a cikin *Alkur'ani* Suratul *Isra'i,* inda

ya nuna cewa akwai Annabawa waxanda ba a kirawo su ba,amma shi Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam,shi ne masoyin Allah, mai girma da xaukaka.

An sami alaqa a nan, saboda yadda duk marubutan aka samu sun yi amfani da ayoyi, musammam Mai Karama ga abin da ya ce

Fir'auna ma yai shisshigi,
Ruwa ya haxeshi gaba xaya.
(Mai Karama,"*Girman Kai'*, bt.13)

Sani kuma sai ya kawo a cikin *suratul Iklas*

*Arrahamani Rahim Lamyalid*

Waxannan kaxan kenan daga cikin ayoyi da aka samu a ciki, duk marubutan sun saka a cikin waqa. Da kuma Hadisai da kuma sira duk a cikin waqoqin, sannan sun yi amfani da kalmomin Larabci.

### 4.3 Zubi da Tsari na Gaba Xaya

Shi wannan vangaren ana duba cikin waqa ta la'akari da tsarin baitocin waqa, ta yadda ake duba baitocin yanayin tsarin da kuma irin jimlolin da aka yi amfani da su. Sannan ana duba dangantakar xangwayen, ana kuma duba gangara da savi - zarce duk a wannan fagen.

An lura da yadda marubutan suke yin baitoci ba tare da yin kwan-gaba-kwan baya ba.

Mai Karama a cikin baitin da yake tafe yana cewa:

A yabo zan kira Makaxaici,
Sannan na sanya mai adalci,

Manzon da yake ya fifici,
Dukkannin halittu hujja.
(Mai Karama, "*Mijin Aisha*", bt, 2)

A wannan baitin da ya gabata a sama, an fito da yadda marubucin ya yi wannan baitin, marubucin ya fara da yabo wajen Ubangiji, sannan kuma sai Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, sannan ya qara bayani da girman Ma'aiki a wajen Allah. Haka ya sa marubucin ba a samu ya yi kwan-gaba-kwan baya a cikin wannan baitin.

Har ila yau kuma Sani yana cewa:

Da sunanka Allah zana fara,
Nake addu'ar ka daxan basira,
Na shiryo yabon Manzo na rera,
Allah gareka nake nema ka qaran yawan falala.
(Sani, "*Abin so*",bt.2)

A wannan baitin na Sani, marubucin ya fara da yabon Ubangiji da kuma addu'ar neman basira saboda samun sauqin yin yabo ga Ma'aiki, da kuma neman yardar Allah. Don haka, shi ma marubucin ba a samu ya yi kwan-gaba-kwan baya a cikin baiti ba.

Alaqar waxannan baituka kuwa, duk marubutan sun yi yabo ne ga Ubangiji, sannan kuma baitukan duk ba su yi kwan-gaba-kwan baya ba. Sannan an samu marubutan sun kawo yadda suke neman taimakon Allah a cikin waqoqinsu.

Ta vanaren bambanci kuwa, Mai Karama bayan ya saka Allah da Ma'aiki sai kuma ya qara bayyana girman Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, a wajen Allah.

Sani kuma bayan ya yi yabo ga Allah, sai kuma ya nemi taimakon Allah don ya qara masa basira da falala wajen yin yabon Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam.

Haka kuma an samu ba sa sassaqa kalmomi masu wahalar fahimta ga jama'a ba. Duba wannan misalin na Mai Karama don ganin yadda yake amfani da kalmomi masu sauqin fahimta.

*Rabbi* Allah ina roqonka,
Ka haskaka ni don Manzanka,
In yabi na A'i mai kyan fuska,
Shi ne Xaha Sidi Siraja.
(Mai Karama, "*Mijin Aisha*", bt. 3)

Wannan baitin na Mai Karama ya fara da yabon Ubangiji da ya ba shi dama da ya yabi Ma'aiki, sannan ya qara da kawo Sayyada Aisha a ciki kuma ya qara da yaba masa da kyan da yake da shi. A baitin marubucin ya kawo kalmomi masu sauqin fahimta kuma bai maimaita kalma a ciki ba.Sani kuma a baitinsa sai ya qara da:

Da tsiranka da aminci *Karimu,*
Ka qarawa jagoran cikinmu,
Wanda ka baiwa Kur'anin *Karimu*,
Ka zave shi a halitta ya zam Annabi Allah.
(Sani, "*Abin so*", bt, 4)

A wannan baitin, Sani ya fara da roqon Allah ya bawa Ma'aiki*Wasila* da *Fadila,* sannan ya qara da bayanin kyautar da aka yi wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ta ba shi *Alkur'ani* mai girma, da kuma zavo shi da Allah ya yi ya zama

Annabi. Haka ya sa wannan baitin marubucin bai yi amfani da kalmomi masu tsauri ba, sannan kuma baitin yana xauke da kalmomi ne masu sauqin fahimta.

Ta duba waxannan baitukan za a iya cewa, marubutan duk sun yi amfani da kalmomi masu sauqin fahimta. Haka kuma ba su sarsarqa kalmomi ba. Amma kuma sun sami bambanci kamar haka, Mai Karama bayan ya roqi Allah sai kuma ya nemi qarin baiwa wajen yabo, amma Sani kuma, sai ya fi ba da qarfi wajen bayanin girman Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam.

Mai Karama a wannan baitin yana cewa:

To Bismillahi ya Allahu,
Sarkin da ya yo *Musbahu*,
Ya yo shehunai da su Shehu,
Albarkacinsa Sidi Siraja.

(Mai Karama, "*Mijin Aisha*", bt, 1)

Mai Karama ya kawo wannan baitin da buxewa da sunan Ubangiji, sannan ya kawo manyan waliyyai amma dukkansu ya kawo su ne saboda sun bi Ma'aiki, wannan ya nuna an sami jerantuwar tunani a ciki.

Sannan a wannan baitin ga abin Sani yake cewa:

*Aminci* haxa *ahalin* gidansa,
Da mata dan 'ya'yan gidansa,
Haxa Sahabbansa masu hidima gurinsa,
Ko'ina suna bisa don qaunarsu gun Annabin Allah.
(Sani, "*Abin so*", bt, 5)

Sani ya qara jero duk waxanda suka yi rayuwa tare da Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,kamar matansa da Sahabbai da kuma 'ya'yansa. Kuma marubucin

ya yi amfani da fasaha wajen jera wannan tunanin nasa. Haka kuma ya qara da yadda suke yi wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, biyayya da kuma yadda suke qaunarsa.

Waxannan baitukan sun nuna yadda marubutan suke amfani da kalmomi masu sauqin fahimta da kuma jera tunaninsa, sannan kuma an samu sun yi amfani da kalmomin da suka daganci Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, da ahalinsa. Sannan duk marubutan sun yi amfani da nuna alaqar da take tsakaninsu da Ma'aikiSallalahu Alaihi Wasallam.

**4.3.1 Zubi da Tsari na Cikin Baitoci**

Wannan waje ne da ake dubawa kuma a yi nazarin baitocin waqar marubuci, yadda baitocin suke kasancewa akwai amsa-amo(qafiya) da yawan baituka da kuma yanayin tsayinsu da sauransu.

Waxannan kaxan ne daga cikin abubuwan da mai nazari yake la'akari da su a wajen zubi da tsari na baitoci har ma da duba yawan ma'anoni da ke qunshe ciki baitin duk da wani lokaci ana duba yawan gavovin dake cikin murya.

A vangaren Mai Karama a waqarsa mai suna *Farkon Hallita*marubucin ya yi amfani dababban amsa-amo wato ''na'' mara karyewa, sannan kuma baitukan duk suna da dangantaka da na gabansu, kuma tsayinsu yana zama xaya a mafi yawan baitocinsa. Ga misalin zubin baitocin.

*Bismillah Allah Rabbani,*
Allahu nima ka haskani,

In waqe *Sayyadil Kaunaini*,
Muhammadu shi ne gatana.

Ya Rabbi Allah Rahamani,
Domin ni in ka haskani,
Buqata babu sauran ni,
Sai dai in waqe *badadina*.

Yi dubun Salati Rabbani,
Agare shi xan Adanani,
Mata da 'ya'yan mai imani,
Ba kamarsa *badadina*.
(Mai Karama, "*Farkon Hallita*" bt. 1-3)

Waxannan baitukan sun fito da zubin marubucin a kan baituka inda tsayinsu yake zama kusan tsayi xaya, kuma suna da dangantaka da juna, sannan kuma duk layukan waxannan baitukan masu layi huxu (qwar - huxu) ne. To kusan duk waqoqinsa suna hawa layi xaya, wato idan waqar layi biyar (qwar - biyar) ce, haka yake yin ragowar baitocin baixaya.

Sannan kuma yana qoqari wajen fito da babban amsa-amo da kuma amsa-amon ciki inda duk baitocin da aka kawo suka tabbatar da haka.

Haka kuma Saniwaqarsa mai taken waqar *Aure*, tana da qaramin amsa-amo da babban amsa-amo, sannan ya yi amfani daamsa-amo mara karyewa, har ila yauta kasance mai layi huxu ce(qwar-huxu), sannan kuma layukan kusan duk tsayinsu xaya.

Allah yi Salati ga Muhammadu *Nuruzzati*,
*Sayyadin Sadati Xaha Sahibul Darajati*,
Mai halin girma me jikoki *Ahlil baiti,*

Duk ina qaunarsu an same su ta hanyar aure.

Ina yara qanqana ku taho ku fahimci batuna,
Da samari da 'yammata ku zo ku fahimci batuna.
Har ma da ma'aurata ku matso ku ji batuna,
Waqa ce na yi ta na yi ta ne harkar aure.

Aure babban lamari ne ba harkar wasa,
Wasu su xau aure al'ada ba addini ba,
Addini ne shi bauta ce ba ‘yar qarama ba.
Kuma Manzan Allah yana tare da mai son aure.

Ni wannan zamani ya saka ni ina wasi -wasi,
Wasu su xau rayuwarsu da faxi *ayyuhanassi*,
Ba su yin mu'amala da mutumin da ba shi sisi,
Wanda ba shi da sisi ya za su ba shi 'ya ya yi aure.
(Sani, “*Aure*”, bt.1-4)

Waxannan baitukan da aka kawo, duk da marubucin waqar ya yi su ne a kan aure, ya fara da addu’ar farawa don kuwa wannan kamar sunna ce ta marubuta waqoqi buxewa da rufewa da yabon Ubangiji da salatin Ma’aiki. Sai ya ci gaba da ba da shawara tun daga kan yara, wato samari da ‘yan mata da kuma iyaye kan yadda ya kamata su lura da wanda ya zo neman auren ‘yarsu.

Shawara ga iyaye in mutum yana son 'yarku
Sai ku binciki halinsa kan ku ba shi ya auri xigarku,
Binciken addini wajibi ya zamo a gare ku,
Kar ku duba tufafi ko mota da gidan da ya qere.
(Sani, “*Aure*”, bt.5)

A wannan waqar, marubucin ya yi amfani da kalmomi masu sauqin fahimta kuma ya yi amfani da babban amsa-amo “re” amma kuma amsa-amo ciki yana

bambanta daga baiti zuwa baiti, sannan layukan kusan tsayinsu xaya. Marubucin ya yi amfani da xango huxu(qwar - huxu). Sannan kuma tana da yawan baituka 22.

Waxannan baitukan da aka kawo na waxannan marubuta sun nuna yadda zubi da tsarin cikin baitocin marubutan yake kasancewa. Sannan kuma sun yi kamanci wajen amfani da amsa-amo yadda ya dace. Haka kuma suna tsayawaa kan qa'ida idan suka fara da layi biyar(qwar -biyar), to duk waqar za ta kasance haka ne.

Marubutan suna amfani da waqoqi masu xangwaye biyu ko huxu wani lokaci har mai xango biyar. Amma a cikin waqoqin da aka yi nazari, an samu sun fi yin amfani da waqoqi masu xango huxu-huxu, sannan kuma an samu sun yi amfani mai xango biyu a ciki. Haka kuma an samu Mai Karama ya yi amfani da waqa mai xango biyar guda biyu.

Ta la'akari da wannan an sami kamanci ta wajen amfani da layukan da marubutan suke amfani a waqa,duk da haka kuma an sami bambanci ta wajen da Mai Karama ya yi amfani da waqa mai xango biyu da mai xango huxu da kuma mai xango biyar, amma a vangaren Sani ba a samu waqa mai xango biyar ba sai dai mai xango huxu da kuma biyu.

### 4.3.2 Gangara

Gangara na  nufin wajen da marubuta waqoqi suke fara bayyana wani abu a cikin xango, sannan su ci gaba da bayyana abun da suke nufi a cikin xango na gaba, ko xangwayen baituka na gaba.

Gangara a waqa tana kasancewa ne waje na haxa layi da layi na waqa, wato a nan wani layi ne ma'anarsa ta ke zarcewa ta ci gaba zuwa layin gabansa da yake bin sa, ko wasu layuka  a cikin baiti.

Marubuta waqoqi suna amfani da gangara wajen isar da saqonsu, waxannan marubuta suma sun yi amfani da ita a wasu daga cikin waqoqinsu.

Mai Karama, kamar yadda yake a baiti na qasa, yana cewa:

Shekara dubu xaya da tara,<br>
Casa'in da biyu *Miladiya*.<br>
(Mai Karama,''*Girman kai''*, bt. 21)

A wannan baitin, Mai Karama ya kawo gangara, inda ya ce '' ..da tara'', sai ya qara da ''Casa'in…'' kasancewar ya xauko magana a layi na xaya, sai kuma ya qarasa a layi na gaba.

Har ila yau a vangaren Sani kuma, a nan samu gangara kamar haka:

Tsira da amincinka qarawa,<br>
Mustafa me yawan baiwa,<br>
Adadin ya zarce kidayawa,<br>
*Alihi Sahabbai* abokansa.<br>
(Sani, "*Mai Cikar Xaukaka"*, bt. 8)

Wannan baitin ya nuna yadda layukan suke da dangantaka da juna, musammam layuka na xaya da na biyu na baitin, “qarawa”, mai saurare ko mai nazari zai so ya ji wa za a qarawa, amma yana shiga layi na gaba sai amsar ta zo, wato shi ne “Annabi Muhammad, mai tsira da aminci”, sannan kuma duk daga jin qarashen ya dace da layi na gaba, tun da ita gangara tana afkuwa ne tsakanin layukan cikin baiti.

Gangara ta rabu kashi uku. Gangara ta gaba da gangara ta baya da kuma gangara ta tsakiya. (Sarvi, 2007:110-111). Dukkaninsu suna iya shafar ‘ma’ana ko zubi da tsari, haka ne ya sa aka  kalli gangara ta waxannan fuskoki domin nazarin ya qara samun wasu misalai gamsassu a ciki.

### 4.3.2.1Gangara ta Gaba

Gangara ta gaba ita  ce wace take fara kasancewa a farko, wato ke nan layin sama ne ma’anarsa take ci gaba da wanzuwa har zuwa wani layin, kuma su layukan da suke gaba layin farko yake dogara da su.

Wannan fage ne da marubuci yake nuna gwaninta ta hanyar haxa layi da layi don ci gaba a kan wani abu da yake son sanar da mai saurare ko mai karatu, haka kuma gangara tana faruwa ne saboda haxa layukan.

Wannan misalin ya zo a waqar Mai Karama:

Shi ne ya sanya hannunsa,
Cikin abincin al'ummarsa,
Sai da mutum dubu suka qosa,
Albarkacin hannunsa Siraja.
(Mai Karama, "*Mijin Aisha",* bt.12)

Marubucin a layi na farko ya fara wata Magana, amma sai ya ci gaba har a sauran layukan, sannan aka sami ma'ana cikakkiya a layin qarshe. Marubucin ya ce "Shi ne ya sanya hannunsa'', za a ji akwai neman qarin bayani sai a layi na gaba ya qara bayani da cewa "Cikin abincin al'ummarsa". Wannan dangantakar da aka samu ta layi na xaya da kuma layi na biyu, ita ce gangara ta gaba.

Sani kumaamisalin a gangara ta gaba, ga abin da yake cewa:

Waye Mala'iku ke inuwa gareshi?
Domin su kare zafin rana gareshi ?,
Wa ya kira wata ya zo har gabanshi?,
Amsar bayanin *Khairir Bariya*.
(Sani,"*Khairil Bariya*", bt.12)

Kamar yadda aka gani, wannan wani baiti ne da marubucin ya fara wata magana a xango na farko da tambaya,

Waye Mala'iku ke inuwa gareshi?

Sai ya ci gaba da ba da amsa kamar haka

…….Amsar bayanin *Khairir Bariya.*

Wannan alaqar da aka samu tsakanin waxannan layuka ita ce misalin gangara ta gaba. Haka kuma ya nuna waxannan xangwayen suna tare da xango na farko, a iya cewa su ne ci gabansa.

Ta la'akari da waxannan baitukan za a lura da marubutan sun yi amfani da gangara ta gaba a ciki. Haka kuma duk sun fara gangarar ne tun a layin farko, sannan ta zarce har ragowar layukan.

Wani abun sha'awa a cikin baitukan marubutan duk sun nuna mu'ujizar Ma'aiki, a cikin Mai Karama ya kawo yadda Annabi,mai tsira da aminci, ya saka hannu a cikin abinci da aka kawo, amma sai da duk waxanda suke wajen suka ci abincin, kuma suka qoshi. Sani kuma ya kalli yadda Mala'iku suke yi wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, inuwa lokacin da suka je kasuwanci da Maisaratu, wato yaron Sayyada Khadijatu, wacce ta zama ita ce matar Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, ta farko, wannan mu''ujizar ita ya kawo.

Mai Karama a wannan baitin na qasa ga abin da yake cewa:

Marabar yaro da babba,
Hankalinsu baka haxa ba,
Nutsuwarsu idan ka duba,
Za ka gane akwai maraba,
Dan'uwana zo ka duba.
(Mai Karama, "*Khatumul Ambiya'i"*, bt.17)

A nan marubucin waqar ya fara bayani tun a xangon farko, "Marabar yaro da babba", idan manazarci ko mai karantawa ya karanta wannan kawai ba zai gane me marubucin yake son isarwa ba, amma idan ya ci gaba da wannan "Hankalinsu baka

haxa ba", za a fahimci wani abu. Bayani ya ci gaba a kan jimlarsa ta farko, sannan marubucin a nan kamar shaguve ya yi,a kan ya kamata jama'a su gane matsayin Ma'aiki, a cikin halitta. Sannan kuma karanta layi xaya ba zai sa a fahimci baitin sosai ba, sai an haxa da layi na qarshe.

Ta vangaren Sani kuwa a wannan baitin na qasa yana cewa:

> A nan zan taqaita waqena,
> Wanda nai waMa'aikina,
> In an tambaye ka sunana,
> Ka ce da su Sani sunansa.
> (Sani, "*Mai Cikar Xaukaka*", bt: 20)

A nan wannan baitin ya nuna yadda baitin ya nuna inda marubucin ya fara magana,

> "A nan zan taqaita waqena"

Amma sai a xango na gaba ya qarasa maganar kamar haka:

> Wanda nai wa Ma'aikina,
> In an tambaye ka sunana,
> Ka ce da su Sani sunansa.

Ta haxa wannan baitin, kenan za a iya fahimtar yadda gangara ta gaba ta yi tasiri a nan, wato inda yake sanar da mai sauraro ya zo qarshen waqarsa, tunda har sunansa ya kawo da sunan unguwarsu.

Wannan ya nuna yadda marubutan a waxannan baitukan suka yi amfani da wannan fasaha ta gangara ta gaba.

Sannan kuma marubutan sun samibambanci ta baitukan da suka yi, Mai Karama ya duba wani abu da ya shafi nasiha a kaikaice, amma kuma Sani shi a nan ya yi bayanin ya zo qarshen waqarsa ne.

Har ila yau Mai Karama, a misali na gaba kuwa a cikin waqar *Wasilah* an ga irin misali na gangara ta gaba.Murubucin ya ba wa wannan waqar suna ne saboda kirarin da ake yi wa Ma'aiki, na wanda ya zamo tsakanin Allah da bayinsa, kuma ita ma tana xaya daga cikin waqoqin da aka nazarta.

Da ma ni tun da na taso,
Manzan Allah nake so,
Ya zamo mini sosan,
Wanke zubi da nay yi.
(Mai Karama, "*Wasilah"*, bt.13)

Marubucin a layi na farko ya fara da cewa "Da ma ni tun da na taso'' idan iya nan kawai ya tsaya abin zai zama ba wata ma'ana, amma da ya ci gaba da layi na gabasai ya za an sami amsa mai ma'ana cikakkiya, ta cewar "Manzan Allah nake so", ashe kenan qarshen maganar ta fito kuma misalin gangara ta haxa layi na farko da na biyu ta fito.

Amma ta vangaren Sani, a waqar me taken "*Abin koyi*", marubucin ya sa mata wannan suna ne, saboda yadda ya kawo halaye da kuma girman Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam, da kuma isar sa a wajen Allah. Marubucin ya qara da baituka da suke nuna kyawun fuskar Ma'aikiSallalahu Alaihi Wasallam, da

kwar jini da daraja, ita ma ta na xaya daga cikin waqoqin da aka yi nazari, ga yadda yake cewa:

Biyayya ga Annabi wajibi ce,
Idan ka bi Annabi za ka dace,
Domin na ji har Allah ya ce
Muslumi mu bi Allah a bi Xaha Manzo Rasulillah.
(Sani,"*Abin koyi*", bt: 7)

Marubucin ya fara magana ta bin Ma'aiki wajibi ne amma kuma kawo layukan qarshe sai suka nuna da cewa "Idan ka bi Annabi za ka dace" sannan har ya qara da bayani da Ayar da ta ce "Abi Allah da Ma'aiki" ta karanta sauran layukan, ashe za a gane lalle ne biyayyar Ma'aiki dole ce.

Waxannan baitukan an sami misalan gangara ta gaba a ciki, kuma marubutan sun yi amfani da yadda suke alfahari da soyayya da kuma nuna dacewar yi wa Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,biyayya da kuma qara sanin girmansa da kuma matsayinsa.

### 4.3.2.2 Gangara ta Baya

Suna linzami, gangara ta baya duk da cewar ana fara magana a farkon baiti, amma wani abin sha'awa sai an karanta layi na ga ba ko na qarshe, sannan mai karatu zai fi fahimtar inda aka saka gaba.

Marubuta waqoqi sukan bayyana abin da suke son faxa a cikin baitin waqarsu tun a layi na farko, amma kuma ma'anar ba ta fita, ba sai layi na gaba Mai Karama a wannan baiti yace:

Allah kai Salati ba iyaka,
Gwargwadon dauwamarka,
Da gwargwadon iliminka,
Daxa shi gurin *Nabiyi*.
(Mai Karama, "*Wasila*", bt. 3)

Marubucin ya fara magana a layi na farko mai cikakkiyar ma'ana, inda ya ce "Allah kai Salati ba iyaka", wannan layin ma'anarsa ta cika, amma tun da waqa ce, sai marubucin ya qara wasu layuka da suka dogara da shi, marubucin ya roqi yadda za a yi salatin da kuma wa za a yi wa salatin, wato za a yi wa Ma'aiki.

Wannan ya sa kenan layukan baya ne suka dogara da na farko.

Ta vangaren Sani an yi amfani da wannan baitin don fito da misalin:

Farko da sunansa mai bayar da kyauta,
Allah *Ganiyu* kai kaxai kake don ka wadata,
Kai ke da arzikin komai ka azurta,
Mun shaida Allah kai kai ne xaya.
(Sani, "*Khairil Bariya"*, bt: 1)

Marubucin ya fara magana mai ma'ana a layi na xaya, sannan nan sai ya ci gaba da layukan da suka dogara da layi na farko. Don a layi na farko da ya ce "Farko da sunansa mai bayar da kyauta", a ragowar layukan sai ya qara fito da waye me bayar da wannan kyautar, sai ya qara da "Allah *Ganiyu* kai kaxai kake don ka wadata".A ciki kuma ya sake kawo wata buwaya ta Allah "Kai ke da arzikin komai ka azurta", to waxannan layukan duk sun dogara ne da jingina da layi na farko.

Waxannan baitukan na waxannan marubuta sun nuna yadda duk marubutan suke amfani da wannan dabara ta gangara ta baya.

Ta fuskar bambanci, Mai Karama ya fi ba da qarfi a wannan baitin wajen roqon Allah da ya yi salati ga Ma'aiki, amma a vangaren Sani shi kuma sai ya ba da qarfi wajen tauhidi, inda ya nuna kyauta da kuma yadda Allah yake azurta bayi, saboda shi Allah mawadaci ne.

Ga wani misalin gangara ta baya a wasu waqoqin marubutan. Kamar haka:

Ga damo yankakke,
Shi ma ya yi sheda take,
A nana gaban bafatake,
Ya yi shedar aiken Nabiyuna.
(Mai Karama,"*Matsayi Nasa*",bt.17)

Tun a xango na farko za a iya fahimtar wani abu, ''Ga damo yankakke'', tun a nan mai saurare zai so ya ji mai ya faru da damon da marubucin ya fara kawo shi,

''Shi ma ya yi sheda take''

Amma kuma haxa waxannan layuka har zuwan xangwaye na gaba wato na qarshen sai bayanin ya qara fitowa. Duk xangwayen da suka zo lalle ba zai zama an fahimce su in baba tare da xango na farko ba, saboda idan aka cire shi, to ma'anar ba za ta fito ba, sannan kuma jimlar ba za ta zama cikakkiya ba.

Sani a wannan baitin kuwacewa ya yi:

Gaisuwa zan yi wa manyan nan,
Wanda ake kira Sahabban nan,
*Khulafa'ur Rashidinan*nan,
Sun kashe Kuffaru mai varna''.
(Sani, "*Kai Nake Qauna''*, bt.6 )

A xango na farko a nan marubucin ya fito da mai yake nufi, wato ''Gaisuwa zan yi wa manyan nan''.Amma duk da haka, idan aka karanta ragowar xangwaye sai a fahimci xango na farko fiye da idan an karanta shi shi kaxai, ba dole ne mai karatu ya gane su wa yake gaisarwa, ba sai ya ci gaba da ragowar xangwayen sannan zai fahimta, cewa yana nufin *Khulafa'ur Rashidina.* Wato Sayyadina Abubakar da Sayyadina Umar Faruk da Sayyadina Usman bin Affan da kuma Sayyadi Ali bin Xallib, Allah ya qara yadda a garesu.

**4.3.2.3 Gangara ta Tsakiya**

Marubucin waqa kan yi irin wannan dabara domin qarawa waqarsa armashi, xangwayen suke dogara da juna, sai an haxa su an karanta sannan za a fahimce su,a kuma gane saqon da suke xauke da shi. Mai saurare sai ya tsaya ya nutsu wajen ganin ko gano dangantakar layuka a cikin baiti, haka ne zai gane abin da baitin yake nufi.

Mai Karama a waqar mai taken ''*Khatumul Ambiya'i'' ta* Mai Karama, an duba misalin gangara ta tsakiya ne ga yadda aka ba da misalinta.

Allah yai nufin zai raya birni,
Har da qauye kullu mini,
*Farilla* da *sunnah* ta yi rauni,
Sai ya aiko shi Alamini,
Yai kiran yaro da babba.

(Mai Karama, "*Khatumul Ambiya'i'* bt. 3)

Idan aka duba wannan baitin da aka kawo, zai yi wuya a fahimci inda saqon ya sa gaba, dole sai an yi amfani layuka na gaba sannan za a fahimci saqon.

Allah yai nufin zai raya birni,
Har da qauye kullu mini.

Abin nufi ko iya waxannan layuka biyu aka tsaya wannan saqon bai fitoba, amma daga an haxa a ragowar layukan sai ma'anar baitin ta cika kuma baitin ya zama ya ba da ma'ana cikakkiya.

*Farilla* da *sunnah* ta yi rauni,
Sai ya aiko shi Alamini,
Yai kiran yaro da babba.

Ta amfani da wannan layuka na qarshen, mai karatun zai gane ashe da kenan al'umma sun daina vautar Allah yadda ya da ce, ma'ana tun da an sami yankewar Annabci tsakanin Annabi Isa, (A.S.)da Annabi Muhammad,mai tsira da aminci, amma da Allah ya aiko Ma'aiki don ya zama rahama ga al'umma, kuma ya fitar da su daga cikin duhun da suke da shi, sannan kuma ya kirowa sua kan kaxaita Allah shi kaxai.

A vangaren Sani ga yadda aka kawo baitin wannan misalin.

Nai iyakar tunanina,
Na kasa gane manzona,
Na yi roqo ga Allahna,
Ko da a barci in ga suffarsa.
(Sani, "*Mai Cikar Xaukaka*" bt.11)

Waxannan layuka dukkansu sun dogara da juna saboda ma'anar kowanne xango ba ta fito ba sai an haxa da sauran xangwayen. Wannan ke nan yana nuna dangantakar layukan, kuma karanta dukkan layuka shi ne zai sa a fashimce su duk wanda mai karatu ya karanta ko mai saurare ya saurara sai ya san akwai wata magana a gaba, ''Nai iyakar tunanina''. Idan kawai wannan layin ne, ba zai sa a fahimci me ake son isarwa ba, sai an haxa da ragowar layukan.

Na kasa gane manzona,
Na yi roqo ga Allahna,
Ko da a barci in ga suffarsa

Amma daga an kawo waxannan shi ke nan mai saurare zai gane, sannan ya fahimci saqon na shi marubucin ya kasa gane matsayin Ma'aiki, a wajen Allah, saboda haka, sai ya roqi Allah ko a barci ya ga Ma'aiki.

Wannan ya nuna gangara ta tsakiya lalle ne sai an karanta sauran layukan, sannan za a fahimci saqon.

Alaqar marubutan shi ne duk baitukana kan yabon Ma'aiki suka yi, kuma sannan da qara nuna xaukaka da buwaya ta Ma'aiki.

Haka kuma wani misalin gangara ta tsakiya shi ne a cikin waqar Mai Karama kamar haka:

Allah ba qasa kawai yake ba,
Sannan ba a qasa yai gida ba,
Ba inda za ka duba,
Ka ce a gun ba Ubangijina
(Mai Karama, "*Yarjajjen Allah",* bt.15)

Haka kuma Sani a nan an yi amfani da baitinsa don qara ba da misali.

Ya kai magidanci ko in ce ango na amarya,
Ka tsaya ka fahimci rayuwa yau ta juya,
Ji tsoron Allah komai za ka yi wa amarya,
Sai kai adalci don ka sami ribar aure.
(Sani, ''*Aure*'', bt. 17)

Waxannan misalan sun nuna akwai kamanci a tsakanin marubutan dangane da abin da ya shafi amfani da gangara ta tsakiya kamar yadda aka gani a cikin misalan baitocinsu.

**4.3.3 Savi-zarce**

Masana suna kiran fasahar da marubuta waqoqi suke yi ta haxa baitoci guda biyu wajen samar da ma'anar wani abun da suke son isarwa a cikin saqonsu da savi-zarce, wato ke nan ana fara bayyana wani abu a wani baitin kuma an ci gaba da bayani a wani baitin, ta haka ake samun dangantaka tsakanin baituka.

Misalin savi- zarce a waqar marubutan inda baitukan suka nuna wannan dabarar, ta haxa baiti da baiti.

Mai Karama ya yi amfani da irin wannan dabara ta savi-zarce a waxannan baitukan, kamar haka:

Cikin wata na *Rajab* aka aiko,
Mala'ika Jibrilu ya sanko,
Sai ya zo shi ga Manzan farko,
Annabi Shi ne Rasulillah.

Sai ya ce in faxa maka sai kajiya,
Sai ya faxa masa sai ya shirya,
Tafiya can har *samaniya*,
Tare da shi da Rasulillah.
(Mai Karama, "*Cetonsa*" bt. 7,8)

A waxannan baitukan marubucin ya yi bayania kan tafiyar Ma'aiki zuwa *Isra'i,* inda ya fara bayani tun daga watan da aka yi, 'Cikin wata na *Rajab''.*

Sannan kuma ya qara bayanin wanda ya zo suka yi tafiya da Ma'aiki, da kuma wajen da suka je wata saman duniya. Haxuwar waxannan baituka sun fito da alaqar da ke tsakaninsu, saboda marubucin ya fara bayani a baiti na xaya kuma ya ci gaba da ita a baiti na biyu, sannan daga jin baitin na biyu za a gane ci gaban baitin farko ne.

Ta vangaren Sani kuma ga yadda ya kawo misali a wannan baitin:

Sarkin da ba shi da xa ko,
Mata balle ta haifi Usaini.

*Tabara* Allah shi ya kaxaita,
Cikin *Zati* Allah *Rabbani*.
(Sani, "*Mai Kur'ani*", bt.3-4)

Waxannan baitikan suna da dangantaka da juna, marubucin ya xauko bayani a baiti na farko, kuma ya cigaba da bayanin a baiti na gaba, inda ya kawo tauhidi a wannan baitukan, kamar yadda ya ce "Sarkin da ba shi da xa ko", haka kuma ya ci

gaba da “*Tabara* Allah shi ya kaxaita” duk wannan da abin da yake cikin baitukan biyu tauhidi ne, sannan kuma ma’anar baitin farko ce ta zarce har baitin na biyu.

Waxannan marubuta suna yin amfani da wannan dabara ko fasaha ta savi – zarce a waqoqinsu.

**4.3.3.1 Savi-zarce na Gaba**

Hanya ce da marubuta waqoqi suke bi don haxe wasu baituka da fitar da abun da suke son isarwa, duk da hakan kan kasance ta hanyar fara bayyana abin da suke son sanarwa a wannan baitin, amma ma’anar sai ta zarce har baiti na gaba, wanda zai kasance yana cin gashin kansa, baitin farkon shi kuma ya zama ba shi da cikkakiyar ma’ana.

Misali Mai Karama ya ce:

Hankali ba tsawo bane ba,
Ba a gajarta ma yake ba,
Ba girman jiki ba ne ba,
Ni abun da naso ka duba,
Ni tsuwarsu ba abari ba.

Masu yabo ku taho mu tare,
Kun ga a cikinmu babu bare,
Kar wanda duk sake ya ware,
Bai da tudu bai da gangare,
Mu’amularsa ba ta yi kyau ba.
(Mai Karama, "*Khatumul Ambiya’i’’*, bt.15-16)

A nan marubucin ya fara magana a baiti na farko, amma kuma masu sauraro ko mai karantawa zai ta tunanin mai ake son cewa saboda ma’anar ba ta fito fili ba, kenan baitin bai bayar da cikakkiyar ma’ana ba, amma mai karatu yana karanta

baiti na gaba zai gane marubucin yana magana ne a kan masu rubuta waqoqin yabon Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam, cewa suna da bambanci da mutane waxanda su ba marubuta waqoqin ba ne, ko kuma su ba gama gari ba ne, ya kamata su haxe kai, wannan kuma ya yi la'akari da Ayar da take magana kan haxin kai, ya jingina ta ga masu yabo, da su yi koyi da ita.

Ga misalin Savi-zarce na gaba a cikin waqar ''*Ubangijin Halittu*'', ta Sani kamar haka:

Kuxin fetur aka qara,
    Muka futo muna ta qara,
    Muna ta tada qura,
    Wai Gwamnati ta yi varna.

Muka rinqa zanga-zanga,
Wasu na ta yaga riga,
Yau Annabi aka zaga,
    Mai mukai a zamanina.
(Sani, ''*Ubangijin Halittu*'', bt.6-7)

Waxannan baitikan dukkansu idan aka duba baitin farko an fara magana kuma bayanin sai ya zarce har zuwa baiti na gaba, baiti na gaba shi ne ya nuna dalilin fara maganar, saboda idan aka karanta baiti za a ga ma'anar ba ta fito ba, in an karanta shi shi kaxai, za a ji ba shi da wata ma'ana. Amma karanta na biyun zai sa a fahimci na xaya, sannan kuma na biyun shi yana cin gashin kansa.

Ta amfani da waxannan baitukan da aka kawo duk marubutan suna yin amfani da savi-zarce a cikin waqoqinsu kamar yadda bayanai suka gabata.

#### 4.3.3.2 Savi-zarce na Tsakiya

Wannan dabara ta haxa baitoci guda biyu su bayar da cikkakiyar ma’ana ta hanyar karanta su tare cikin waqa, inda duk baitukan sune suke haxuwa sai ma’anar ta fito.

Marubuta kan ja hankalin mai saurare wajen son nuna nutsuwa da kuma tsaida hankali don lura da abubuwan da suke rubutawa a cikin waqa, don haka wani lokaci sai su haxa baituka domin fitar da wata ma’ana a tsakanin.

Ga misalin Savi-zarce ta tsakiya a cikin waxannan baitukan na Mai Karama:

Ku jini ya *Ikwani,*
*Adi’ullaha wal ma’amuni*,
Rasulahu ga dukkan *kauni*,
Aya ta nuna *badadina*.

Sannan ya qara da bayani,
Uwa uba harma kakanni,
Da dukkani wani mai imani,
In yaso Muhammadu gatana.
(Mai Karama, “*Farkon Halitta*” bt: 9-10)

Ma’anar baitin farko ce ta zarce zuwa baiti na gaba kuma haxa baitocin guda biyu, zai saka a fahimce su, marubucin ya kawo Ayar da take bayyana cewa sai mutum ya bi Allah da Annabinsa da kuma iyaye, sannan zai sami cikakken imani.

Ga misalin Savi-zarce na tsakiya a cikin waqar *Mijin Hafsat* ta Sani:

Nai iyakar tunanina,
Na kasa gane Manzona,
Na yi roqo ga Allahna,
Ko da a barci in ga siffarsa.

In yana zaune kyakkyawa,
In ya miqe kyakkyawa,
Ga ka wanda baka inuwa,
Shin ya kake ne mijin Hafsa.
(Sani, "*Mai Cikar Xaukaka*",bt.11-12)

Waxannan baitikan sun kasance misalin savi-zarce na tsakiya, saboda ma'anar baitin farko ce ta zarce zuwa baiti na gaba, amma kuma ta hanyar karanta na baya ne za a fahimci na farkon, ta haka ne kuma za a gane inda kowanne baitin ya sa gaba, ta hanyan haxa su a karantu su biyun, sannan kuma aka gane ashe baitin yana magana a kan Annabi,Sallalahu Alaihi Wasallam, sannan shi baitin qarshen shi ne ya sa za a fahimci baitin da ya rigaye shi.

A wannan misalin na savi-zarce na tsakiya an samu duk waxannan marubuta suna amfani da shi a cikin waqoqinsu. Sannan an samu Mai Karama ya yi nasiha da bin Allah da Ma'aiki da kuma bin iyaye, amma ta vangaren Sani kuma sai aka yi amfani da waqar da ya yi ta nuna girman Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam,.

#### 4.3.3.3 Savi-zarce na Baya

Marubuta waqoqin kan fara magana wata mai ma'ana a xango na farko sannan kuma su kawo wani baitin da zai dogara da na farko, duk da haka ma'anar baitin na fakon kan kasance jagora a waxannan baitukan.

Mai Karama yana cewa:

Kututture yai nishi,
Don rashin *Baqureshe*,
Sanda za ya tashi ya bar shi,
A masallaci ne na Annabina.

Kutunturen a gabansa,
Sanda ya yi kukansa,
Manzo ya sa hannunsa,
Yai mai alkawari Nabiyuna'.
(Mai Karama,''*Matsayi Nasa*'', bt.5-6)

Waxannan baitikan su biyu suna magana ne a kan abu xaya,wato ''Kututture'' na itace lokacin da Ma'aiki yana hawa kansa ya yi huxuba, daga baya sai aka qera masa munbari don ya koma ya ci gaba da huxuba. Wannan ta sa shi wannan itacen ya yi nishi. Baitin na farko ma'anarsa ta cika, sannan baiti na biyun ma'anarsa, ta cika amma sai dai in aka cire na farkon to sai an yi qarin bayani sannan za a fahimci shi. Bayan haka kuma baitin farko ya nuna mene ne ya faru har aka sami baitin na gaba.

Ga misalin savi-zarce na baya daga baitukan Sani:

Allahu ga ka ga su,
Ka san abin nufinsu,
Sharrin mayar shi kansu,
Da sukai wa Annabina.

Allah sa musu cuta,
Cutar da ba irinta,
Da kuturta da makanta,
Kuma ransu yai ta quna.
(Sani, "*Ubangijin Halittu*", bt.10-11)

Baitin farko ma'anarsa ta fito, sannan marubucin ya qara baitin da ya dogara da baitin farko, saboda in mai karatu ko mai saurare ya karanta baiti na farko, ba zai fahimci mai marubucin yake magana a kai, amma da zai fara daga baiti na biyu zai yi ta saqe-saqen toa kan mene ne marubucin ya yi wannan baitin, amma idan mai karatu ya duba baiti na farko zai gane, kuma ya fahimci ma'anarsu gaba xaya.

Ta amfani da waxannan misalai za a gane marubutan suna amfani da savi-zarce na baya a waqoqinsu. Duk da Mai Karama an samu a baitukansa an yi amfani da mu'ujizar Ma'aiki ta jin magana duk abin da ya yi magana, ya kuma gane mai ya sa ya yi wannan abun kuma ya fahimci maganar. Amma Sani kuma sai aka duba baitukan da suka yi magana a kan addu'ar da ya yi ga masu sukar Ma'aiki,Sallalahu Alaihi Wasallam.

### 4.3.4 Jirkinta Faxar Sakamako

Jirkinta faxar sakamako waje ne da marubuta waqa suke xauko bayanin wani abu inda suke yin cikakken bayaninsa saboda mai saurare ya fahimta, tare da gane manufar waqa, hakan tana samuwa ne ta hanyar haxa baitoci fiye da guda biyu.

Ga misalin jinkirin faxar sakamako a cikin waqar Mai Karama:

Nan na jingina da Ka'aba ina ta kuka,
Ana haka sai ga wani tsohon boka,
Ya ce don mene ne kike ta kuka,
Na ce yaro na shayar na zo zani miqa,
Na aje shi na zo ban tarda shi a gun ba.

Ya ce zo in ba ki shawara game da saqo,
Ki je ki nemo gumba da zuma ki sa a qoqo,

In kin samo wannan kuma sai ki leqo,
Ni kuwa in kai ki wurin da a kan yi roqo,
In kin sa'a yaronki ba zai vace ba.

Daga jin haka ni kuma ban tsaya ba,
Sai na sayo zuma na haxa da gumba,
Na sa sabon qoqo wanda ba a tava ba,
Na doshi gurin bokan bai tsaya ba,
Sai da ya kai ni wurin gunkinsa babba.
(Mai Karama, "*Xan Suwaiba*", bt. 12-14)

Waxannan su ne misalin jinkirin faxar sakamako a cikin baitocin, saboda baitocin dukansu suna magana ne a kan abu guda sannan kuma ci gaban bayani ne. Duk waxannan baitukan sun yi bayanin ne a kan yadda Nana Halima ta yi lokacin da suka zo da Ma'aiki ta neme shi a Ka'aba ta rasa, da kuma shawarar da boka ya ba ta.

Har ila yau, Sani shi ma an duba irin wannan misalikamar haka:

A nan zan taqaita waqena,
Wanda nai wa Ma'aikina,
In an tambaye ka sunana,
Ka ce da su Sani sunansa.

Ka ce da su Sani sunana,
Abubakar ne mahaifina,
Allah ka yafewa babana,
Laifin da ya yi duk girmansa.

'Yan'uwa masu sauraro,
Nan Kano nake a Hotoro,
In da ka zo kadda kaji tsoro,
Ka yi tambaya za ka ga gidansa.
(Sani, ''*Mai Cikar Xaukaka*'' bt 21-23)

Waxannan baitocin su ne misalan a cikin wannan waqar inda marubucin aka duba baitoci guda uku na jere waxannan da suka haxu don bayani a kan sunan marubuci da sunan babansa da kuma sunan unguwar da yake zaune.

Marubutan waxannan waqoqi duk an samu suna amfani da wannan dabarar ta jinkirin faxar sakamako a waqoqinsu kamar yadda bayanai suka gabata.

**4.3.5 Kari/Aruli**

Kari na xaya daga cikin abubuwan da ake dubawa a qarqashin zubi da tsarin waqa, masana da dama sun yi bayani a kan wannan fanni na Aruli.

Aruli wata hanya ce da marubuta waqoqi ke yin amfani da ita don samarwa waqa karin da za a xora ta a kai, saboda samun sauqin rubutu, da jerantuwar gavovinta da layukanta. A Hausa yanzu akwai karori guda goma sha shida (16) da marubuta waqoqi suke xaura waqoqinsu:

A qasa, ga jadawalin waqoqin da aka nazarta tare da karuruwan da aka xora su a kai:

| **Mai Karama** | **Sani** |
| --- | --- |

| Sunan Waqa | Kari | Sunan Waqa | Kari |
|---|---|---|---|
| *Mijin Aisha* | Mutadarak | Aure | Ramal |
| *Khatimul Ambiya'i* | Ramal | *Shugaban Bayin Allah* | Mujtas |
| *Cetonsa* | Basix | *Mai Xikar Xaukaka* | Ramal |
| *Girman Kai* | Rajaz | *Ubangijin Halittu* | Basix |
| *Farkon Halitta* | Mujtas | *Khairil Bariya* | Mujtas |
| *Wasilah* | Mutadarak | *Kai Nake Qauna* | Hafif |
| *Matsayi Nasa* | Rajaz | *Abin Koyi* | Kamil |
| *Xan Suwaiba* | Ramal | *Isra'i* | Mujtas |
| *Yarjajjen Allah* | Mutaqarab | *Mai Kur'ani* | Rajaz |

Bisa la'akari da wannan jadawali da ya gabata, za a ga duk marubutan suna xora waqoqinsu a kan kari. Ta wannan vangare ma ashe sun yi tarayya. Idan aka duba vangaren Mai Karama za a ga ya yi amfani da karin Mutadarak (2), karin Ramal (2), karin Rajaz (2), da karin Basix (1), karin Mujtas da kuma karin Mutaqarab (1). Ta wajen Sani kuwa, za a ga waqoqin sun hau kan karin Mujtat (3), karin Ramal (1), karin Kamil (1), karin Hafif (1), karin Basix (1) da kuma karin Rajaz (1).

Idan aka yi la'akari da waxannan karoridaa aka kawo a sama ya nuna cewa a cikinsu an sami bambancin kari tsakanin Mai Karama da Sani, inda Sani ya yi

amfani da karin kamil sau xaya, amma a vangaren Mai Karama ba a samu inda ya yi amfani da wannan karin ba, a waqoqin da aka yi nazari. Haka kuma a vangaren Mai Karama ya yi amfani da karin Mutadarak har sau biyu, amma ta vangaren Sani bai yai amfani da shi ba ko sau xaya. Sannan Sani ya fi amfani da karin Mujtas inda ya yi amfani da shi har sau uku, sai dai Mai Karama ya yi amfani da shi sau xaya a cikin waqoqin da aka yi nazari.

Waxannan su ne abubuwan da aka yi nazari a cikin wannan babi na huxu, inda aka kawo jigogin waqoqin marubutan da zubi da tsarin waqoqinsu tare da misalai, wanda tun a farko an kawo bayanan masana a kan waxannan abubuwa da suka shafi nazarin jigo da kuma zubi da tsari a cikin waqa.

# BABI NA BIYAR

## KAMMALAWA

## 5.1 Gabatarwa

Wannan babi shi ne na qarshe a ciki wannan bincike, Hausawa na cewa " komai nisan dare…" wannan batu haka yake "zara bata barin dami", wannan babi ya haxa da taqaitawa da sakamakon bincike da matsalolin bincike da kuma shawawari.

## 5.2 Taqaitawa

*Alhamadulillahi*, godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin *talikai* Mai Rahama da jin qai. Wanda bai haifa ba, kuma ba a haife shi ba,wanda ya rabe tsakanin mutane da dabbobi, a cikin mutane kuma ya fitar da zavavvansa, masoyinsa Annabin Rahama, Annabi Muhammad, Sallalahu Alaihi Wasallam, wanda ya zo mana ya kuma nuna mana hanyar neman ilimi domin samun rabauta a duniya da lahira. Allah ka qara tsira ga Sahabbansa da matansa da dukkan waxanda suka bi haryarsu har zuwa ranar *qiyama*, amin.

Kamar yadda bayanai suka gabata wannan bincike da aka gudanar mai suna "Kwatanta jigo da zubi da tsari waqoqin Bello Muhammad Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro". Binciken ya gudana ne a kan babi guda biyar, abun nufi a nan shi ne an fara shi tun daga babi na xaya zuwa babi na biyar.

Babi na xaya ya haxa da manufar bincike gudummawar bincike da iyakar bincike da tambayoyin bincike da hasashen bincike da dalilin bincike da kuma tarihin marubutan Bello Muhammadu Mai Karama da Sani Abubakar Hotoro.

Babi na biyu ya yi bayani a kan ma'anar kalmomin da aka yi amfani da su wajen nazari da kuma waiwaye a kan bitar ayyukan da suka gabata masu alaqa da wannan aikin, tun daga kundayen digiri na xaya da na biyu da kuma na uku, tare da kawo littatafai da muqalu da kuma mujallu.

Babi na uku shi kuma ya qunshi ra'in da aka xora binciken a kai da kuma hanyoyi da aka bi wajen gudanar da binciken wanda ya haxa da tattara waqoqi da kuma wuraren da aka kai ziyara da waxanda aka yi hira da su.

Babi na huxu ya haxa da bayani a kan yadda waxannan marubuta waqoqin suke amfani da fasahohinsu da tunaninsu wajen tsara waqoqinsu, inda aka kawo bayanai tare da wasu misalan waqoqin marubutan kuma aka duba jigogin da kuma zubi da tsarinsu sannan aka ba da misali a kan gangara da savi-zarce, an kalli gangara ta gaba da ta baya da kuma ta tsakiya, haka kuma an duba jinkirin faxar sakamako, an kwatanta waqoqin waxannan marubuta inda aka fito da kamancin waqoqinsu ta fuskarjigo da zubi da tsari da kuma fito da bambance- bambancen da aka samu a tsakani.

Babi na biyar shi ne ya haxa da kammalawa da sakamakon bincike da matsaloli da shawarwari.

## 5.3 Sakamakon Bincike

Dangane da sakamakon bincike kuwa, babu shakka kamar kowane aiki da aka gudanar, a qarshe a kan sami wata manufa da aka cimma. Don haka wannan bincike ya yi qoqarin gano abubuwanda suka haxa da bibiyar tarihin mawallafan. Haka nan bincikn ya gano duk marubutan sun yi tarayya wajen amfani da jigon nasiha da gargaxi da kuma yabo.

Dangane da furucin gundari jigo, an gano duk suna bayyana babbar manufar wallafarsu a cikin baitocin farko na waqoqinsu.Kazalika an yi nasarar gano, kamanci da kuma bambanci da ke tsakani waxannan marubuta ta fuskar jigo da kuma zubi da tsarinsu.

Haka kuma binciken ya gano waxannan marubuta sun haxu ta fuskoki da dama, musammam wajen zubi da tsari na gaba xaya, ta inda suke amfani da kalmomi masu sauqin fahimta kuma suna daidaita baiti da baiti.

Ta fuskar zubi da tsari na cikin baitoci, kuwa binciken ya gano duk marubutan suna amfani waqa mai qwar–biyu da qwar-huxu da kuma qwar–biyar.Ta vangaen bambanci an ga Sani ya fi xora waqoqinsa a kan tsarin qwar–huxu, inda Mai Karama ya fi xora waqoqinsa a kan qwar-huxu da kuma qwar–biyar, kamar yadda aka kawo waqoqin a rataye.

Sannan kuma duk suna amfani da babban amsa–amo da qarami a cikin waqoqinsu.

Har ila yau kuma an gano marubutan suna amfani da *nassi* a cikin waqoqinsu.

## 5.4 Matsalolin Bincike

Kamar yadda yake a rayuwa duk wani abu da aka samu nasara, to ba a rasa shi da matsaloli. A wannan bincike an ci karo da matsaloli duk da yake ba su taka kara sun karya ba, amma ya kamata a ambace su.

Matsala ta farko ita ce, ta rashin masu gidan rana (kuxi), da ta lokacin zirga-zirga. Matsala ta gaba ita ce, ta rashin samun wasu waqoqin a rubuce cikin takardu ko littafi da sauran abubuwa makamantan waxannan.

Wata matsalar kuma, ta yajin aiki da kuma annobar *Covid*-19da ta shigo duniya.A taqaice, waxannan su ne matsalolin da aka ci karo da su yayin gudanar da wannan bincike, a kan ‘‘Kwatanta Jigo da Zubi da Tsarin Waqoqin Bello Muhammadu Aji Mai Karama da na Sani Abubakar Hotoro’’.

## 5.5 Shawarwari

Shawarwarin da wannan bincike zai iya bayarwa su ne kasancewar fagen adabi, fage ne mai ban sha’awa wanda ke jawo hankulan jama’a da su yi rubuce-rubuce a wannan vangaren.

Bincike yana bayar da shawara ga mawallafa da su dinga qoqarin adana rumbun rubutattun waqoqinsu domin kauce wa rasa su ko wani vangare nasu.

Yana da kyau mawallafa da su dinga ba xalibai masu nazarin waqoqinsu cikakken haxin kai da amince musu kai tsaye, domin ba su qwarin gwiwar gudanar da bincike.

Yakamata masu nazari, su riqa qarfafa wa mawallafan guiwa na aqalla yabawa da aikinsu da kuma irin hikimomin da Allah ya ba su.

MANAZARTA


Abdullahi, U.M. (2007). “Jigon Yabo na Rubutattun Waqoqin Hausa Na Garba Gashuwa, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Abdulqadir, X.(2008). “Kwatanta Rubutattun Waqoqin Siyasa na Hausa Daga1804 zuwa 1966’’, Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Bayero, Kano.

Abubakar S.M. da Yahaya U.F. (2012). “Gudunmuwar Rubutattun Waqoqin Hausa na Siyasa wajen Samar da Inganciyar Dimokaradiya a Nijeriya”,Takardar da aka gabatar don *Qarawa Juna Ilimi na Farko a kan Harshe da Adabi da Al’ada*, Jami’ar Bayero,Kano.

Adamu, F.U.(2012). “Kwatanta Jigon Yabo a Waqoqin Sarakuna na Baka da Rubutattu”,Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Adamu, M.T. (1998).*Aure da Buki a Qasar Hausa.*Kano: Xan Sarki Kura Publishers Limited.

Ahmad, T.A.(2005). “Kwatanta Wasu Waqoqin Talla na Gargajiya da na Zamani a Kafafen Yaxa Labaran Gidan C.T.V. da Rediyon Freedom”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Aisha, I.A (2011). “Salo Da Sarrafa Harshe A Cikin Wasu Waqoqin Jam’iyyun ANPP Da PDP A Kano Da Jigawa,” Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Aliyu, T. (1974).“Rayuwa da Ayyukan Aqilu Aliyu”, Kundin Digiri na Xaya, Jami’ar Bayero, Kano.

Amin, A.A.(2009).“Nazari a kan Wasu Waqoqin Sarkin Kano Alh. Ado Bayaro: Sigoginsu da Fasahar da ke Cikinsu”,Kundin Digiri na Farko, Jami’arBayero,Kano.

Auta, A.L. (2001). “Tarihin Rubutattun Waqoqin a Qasar Hausa”, a cikin *Algaita, Jornalof Current Research in Hausa Studies* No. 1 Vol, 1 Sashen Harsunan Nijeriya, Jami’arBayero, Kano.

Auta, A.L. (2014). “Aure a Rubutattun Waqoqin Hausa”,in Sa’idu Muhammad Gusau et al (eds.)*Garkuwar Adabin Hausa: AFestschrift in Tribute to Abdulqadir Xangambo*)”, pp. 279-288. Bayaro University, Kano.

Bangudu, A.I. (2017). “Turke Rubutattun Waqoqin Siyasa na Kabiru Yahaya Kilasik’’, Kundin Digiri na Biyu,Jami’arBayero, Kano.

Bello A. da Sheshe I. N. (2014).*Arulin Hausa a Sauqaqe.* Kano: SM Graphics Printers & Publishers.

Bilkisu,Y.H.(2012). “Kwatanta Salon Rubutun Bilkisu Ahmad Funtuwa da Bilkisu Yusif Ali”,Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Bayero, Kano.

Birniwa H.A. (1983). “Tasirin Nassoshin Alkur’ani da Hadisai a kan Rubutattun Waqoqin Hausa”, Takarda da aka gabatar a *Taron Qara wa Juna Ilimi*, Jami’ar Usman Xanfodiyo, Sakkwato.

Birnin Kudu S.Y. (2003). “Jigo da salon Rubutatttun Waqoqin Furu’a na qarni NaAshirin”, Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Usman Xanfodiyo,Sakkwato.

C.N.H.N, (2006). *Qamusun Hausa*. Zaria: Ahmadu Bello University Press Limited.

Xangambo A.(1980). “Hausa Wa’azi verse from 1800 to C.A 1970’s. A Critical Study of Form Conference Language and style’’A Ph.D Dissertation University of London.

Xangambo, A. (2007).*Xaurayar Gadon Fede waqa*. (Sabon Tsari) Zari’a: Amana Publisher Limited

Xangambo A. (2008).*Rabe-Raben Adabin Hausa.(sabon tsari)*Kano: K.D.G. Publication

Xangambo, H.A. (2012).“Kwatanta Tubalin Gina Jigo Tsakanin Rubutattun Waqoqi da Qagaggun Labarai na Hausa” Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Bayero, Kano.

Xangulbi, A.R (2003). “Siyasa a Nijeriya Gudummuwar Marubuta Waqoqin Siyasa na Hausa ga Kafa Dimokurraxiyya”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Usman Xanfodiyo,Sakkwato.

Fatima, U.A (2012). “Kwatanta Jigon Yabo a Waqoqin Sarakuna na Baka da Rubutattu”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Garba, S. (2013). “Qayen Harshe: Nazarin Sako a Hannun Mumini ta Aqilu Aliyu”,1[ST]*National* Jornal on Language, Literature and Culture. Centre for theStudy of Nigerian Language, (381-387),Bayero University,Kano.

Gusau, G.Y.(2010). “Kwatanta Tsakanin Waqoqin Muslumci na Hausa da Kuma Waqoqin Zamani”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Gusau, S.M. (2003). *Jagorar Nazarin waqar Baka*. Kano: Bechmark Publisher Limited.

Gusau, S.M. (2008). *Waqoqin Baka a Qasar Hausa: Yanaye-Yanayensu da Sigoginsu.*Kano: Benchmark Publishers Limited.

Gusau, S.M. (2012). “Mizani tsakanin waqoqin Hausa na baka da Rubutattu” Takardar da aka Gabatar don Qarawa Juna Ilimi Karo Na Farko a kan Harshe da Adabi da Al’ada Jami’ar Bayero, Kano.

Habiba, A.U. (2014). “Kwatanta Salo da Sarrafa Harshe a Waqar Mikiyar Zuhudu” ta Abdulqadir Alhassan Babajo da Littafin *Mace Mutum* na Rahma Abdulmajid”,Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero,Kano.

Halima,A.X (2012). “Kwatanta Tubalin Gina Jigo Tsakanin Rubutattun Waqoqi da Qagaggun Labarai na Hausa”, Kundin Digiri na Uku,Jami’ar Bayero, Kano.

Hauwa, M.L (2015). “Gudummuwar Waqoqin Reno na Mata a Kazaure da Kewaye Wajen Bunqasa Adabi da Al’adun Hausawa”, Kundin Digiri na Xaya,Jami’ar Bayero, Kano.

Isah, B.M. (2012). “Salon Amfani da Nassin Alkur’ani a waqoqin Mudi Sipikin”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Isah, B.M. (2013). “Gudummuwar Adabi ga Bunqasar Dimokaraxiya a Nijeriya: Tsokaci a kan rubuttatun Waqoqin Hausa”,1ST International Jornal on Language, Literature and Culture. Pp.(434-444),Bayero University,Kano.

Isma’il, A.(1994). “Rubutattun Waqoqi a Qasar Kano Nazarin Waqoqin Yabon Annabi (S.A.W.)”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Lawan, A. (2012). “Qwatanta Salo da Jigo a Waqar Muhammadu Gawo Filinge da Musa na Dada”, Kundin Digiri na Farko, a Jami’ar Ahmadu Bello Zariya

Maitama, S.A (2014). “Kwatanta Waqar Duniya ta Audu Waziri Xan’duna da ta Mahmud Isma’il Nagudu”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Muhammad, H. (2011). “Wa’azi a Rubutattun WaqoqinMata na Qarni Na Ashirin”,Kundin Digiri Na Biyu, Jami’ar Ahmadu Bello,Zariya.

Muhammad, K. (1974). “Kwatanta Tsakanin Rubutattun Waqoqin Hausa da na Fulatanci”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Muhammad, S.A (2013). “Waqa Sako ce”, 1ST International Jornal on Language,

Literature and Culture. Pp. 381-388.Bayero University,Kano.

Muhammad, S.S. (2011). “Qwatanci Waqar Jiddul Aziji da Waqar Kanzul Azimi”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Ahmadu Bello,Zariya.

Muhammad, Y. (2014). “Kwatanta Salon Wasu Waqoqin Aminu Ladon Ala da na Fati Nijar”,Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Mukhtar, I. (1984) “Nahawun waqa, Yanaye – yanayen sa da Sigoginsa cikin Rubutattun Waqoqi Hausa”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero,Kano.

Mukhtar, I (2004). *Bayanin Rubutattun Waqoqin Hausa*. Garki Abuja: country Side Publisher Limited.

Mustafa, S. (2011). “Rayuwa da Gudummuwar Shehu Ibrahim (Qasida) a Fagen Rubutattun Waqoqin Hausa”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Nalado, H.(2015).“Kwatanta Waqar Bulaliya ta Sani Yusif Ayagi da Waqar Matacciya ta Rabi’u Usman Baba”,Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Nura, B. (2012). “Kwatanta Waqoqin Sarkin Kano Alh. (DR) Ado Abdullahi Bayaro na Baka da Rubutattu”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Sankalawa, D.H.(2004). “Kwatanta Waqoqin Aliyu Namangi da Takwaransa

Sani Yusif Ayagi”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Salihu, D. M. (1982). “Rabe-Raben Waqoqin Hausa da Tasirinsu ga Rayuwa A Qasar Hausa”, Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Bayero, Kano.

Sarvi, S.A. (2007).*Nazarin Waqen Hausa.* Kano: Samarib Publisher.

Rabi’u, M.T. (2018).“Kwatancin Habarcen Nijeriya Da Nijer: Tsokaci A Kan Tatsuniya”,Kundin Digiri na Biyu, Jami’ar Ahmadu Bello, Zariya.

Tilde, A.U. (2016).*Waqoqin Aruli.* Jos: Majesty Printers and Publisher.

Uba, M.T. (2012). “Nazari a kan Waqar Tutocin Shehu da Waninsa ta Mu’azu Haxeja”, The Writer Jornal,Vol. 2, pp 86-93. School of Language,Sa’adatu Rimi College ofEducation Kumbotso, Kano.

Usman, N.A. (2013).“Adon Harshe a Waqoqin Siyasa: Nazari a kan Waqoqin Haruna Aliyu Ningi’’,*1ST National Jornal on Language, Literature and Culture*. Pp.397-413, BayeroUniversity,Kano.

Yahaya I, Y da Xangambo, A.(2004).*Jagoran Nazarin Hausa.* Zaria: N.N.P.C

Yakasai, M.G.(2014). “Kwatanta Salo a Waqoqin Shaihu Abubakar Atiku Sanka da na Liman Muhammad Xan’amu”,Kundin Digiri na Uku, Jami’ar Bayero, Kano.

Yusuf, A. (1972). “Kwatanta Arewa Jamhuriya ko Mulikiya da Tutocin Shehu da Waninsa”, Kundin Digiri na Farko, Jami’ar Bayero, Kano.

Yahya, A. B. (1997).*Jigon Nazarin Waqa*. Kaduna: Fisbas Media Services.

Yahya, A. B. (2001).*Salo Asirin Waqa*. Kaduna: Fisbas Media Services.

Yahaya, I. Y.(1984). ‘’Trends in the Development of Creative Writing in Hausa’’, A Paper Presented at New Writing in Africa Conference. Held at Commonwealth Institute/African Centre, London: 1-3 November, 1984.

Yahaya I.Y (2002). *Hausa a Rubuce Tarihin Rubuce Rubuce cikin Hausa*

(SabonTsari). Zaria: N.N.P.C.

Yahaya I.Y (2001). *Salo Asirin Waqa.* Kaduna: Fisbas Media Services.

Yahaya, U.F (2014). “Amfani da Ayoyin Alkur’ani a Wasu Daga CikinWaqoqin

Hausa na Bello Mai Karama Guda Bakwai”, Kundin Shaidar Babban

Difiloma ta Qasa, Jami’ar Bayaro, Kano.

**Mutanen da aka yi Hira da su:**

**1.** An yi hira da Mubarak Idris *Alqadiri* rana ta farko ita ce 22/10/17 da 02/03/2018, a unguwar Giginyu da qarfe 5:00- 5:34 na yamma.
**2.** Sannan an yi hira da Yahaya Isa (Babaye) ranar 12/01/2018, a unguwar Giginyu da qarfe 8:13- 9:34 na dare.
3. An yi hira da Sunusi Muhammad ranar 23/01/2018, gidan Malam Sani a Hotoron Walawai da misalin qarfe 3:30- 4:30 na yamm
**4.** An sami damar yin hira da Abdullahi Abdulkarim ranar 25/01/2018, a Hotoron Walawai da misalin qarfe 4:34 – 6:17, na yamma.
5. An tattauna da Malam Nura Baba, a ranar 07/10/2017 da kuma 07/03/2018 a ofishinsa da ke Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano.
6. Dr. Mahe Isa Ahmad, a ranar 08/11/2017 da kuma 02/01/2018 a ofishinsa da ke Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano.
7. Dr. Babangida Magaji Isa, a ranar 08/11/2017 a ofishinsa da ke Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano.
8. Malam Garba Yakubu, a ranar 08/07/2018 a ofishinsa da ke Kwalejin Ilimi ta Sa'adatu Rimi, Kumbotso, Kano.

## RATAYE NA XAYA

## SAMFURIN JERIN TAMBAYOYI

An yi hira da wasu daga cikin yaran marubutan ga kuma kaxan daga tambayoyin da aka yi musu, da kuma amsoshin da aka samu.

1. Shin yaya waqoqin Mai Karama da Sani suke a wajan tallafawa al’ummar Hausawa?

   Waqoqin suna qara tunasar da al’umma matsayi da girman Ma’aiki, sannan kuma suna amfani da zubin da kowa yake fahimta cikin sauqi.

2. Marubutan suna saka abubuwan da suke qara wa harshen Hausa kalmomi?

   Gaskiya ne wannan tana faruwa a cikin waqoqinsu, domin suna xauko kalmomi ko dai daga wani harshe zuwa harshen Hausa ko kuma su Hausance ta.

3. Suna amfani da karin magana a cikin waqoqinsa?

   Duk marubutan sukan saka karin magana a cikin waqoqinsu.

4. Wane darasi waqoqinsu ke koyarwa ga al’umma?

   Waqoqin suna nuna darasi kamar yadda aka samu a cikin a waqoqin da su ka yi na gargaxi da nasiha da kuma jan kunne, sannan da yadda suke kawo ayoyin da Hadisai a ciki.

5. Idan ba sa nan wani yana karanta waqoqinsa?

Eh suna da su.

6. Ko suna da halifa?

Mai Karama yana da halifofi kamar guda biyu manya, su ne Mubarak Idris Alqadiri da Yahaya Isa (Babaye), amma a vangaren Sani kuma akwai Sani Muhammad.

## RATAYE NA BIYU

### Waqoqin Bello Muhammad Aji Mai Karama

## WAQA TA XAYA

### Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama

### 'Mijin Aisha'

**Amshi:** Ya Muhammad Mai Cetona ya Mijin Aisha da Khadija

1. To *Bismillahi* ya Allahu,
Sarkin da ya yo Musbahu,
Ya yo shehunai da su Shehu,
Albarkacinsa Sidi Siraja.

2. A yabo zan kira Makaxaici,
Sannan na sanya mai adalci,
Manzon da yake ya fifici,
Dukkannin halittu hujja.

3. *Rabbi* Allah ina roqonka,
Ka haskaka ni don Manzanka,
In yabi na A'i mai kyan fuska,
Shi ne Xaha Sidi Siraja.

4. *Assalatullahi ma'attasalimi*,
Ga Muhammadu khairil *Anami*,
Mata da 'ya'yansa *zul'ikirami*,
Har da A'isha har da Khadija.

5. *Wa'alihi* na Manzan Allah,
*Wa'assahabu* xan Abdallah,
*Watabi'ina* bayin Allah,
Dukkansu saboda da Siraja.

6. Na sa da Shehuna Jilani,
Na haxa da *Sheikh* Tijjani,
Jikokin Xaha xan Adanani,
Dukkansu saboda da Siraja.

7. Na sa da Shehi na Inyasi,
Gwarzo jikan *Mahsusi*,
Dole ne ni in sa Inyasi,
Don qaunarsa Sidi Siraja.

8. Shehu Nasiru ni kama ni,
Ka xora ni bisa tsani,
*Baharul ilmu wal insani*,
Don qaunarsa ga Sidi Siraja.

*9.* *Rabbana* ka ba ni fasaha,
In yabo Muhammadu Xaha,
Don in zamto na yi nasiha,
Cikin yabon Sidi Siraja.

10. Ya Muhammadu xan Adanani,
Ka ga xan gatan Rabbani,
Kai Allah ya ba *Qur'ani*,
Ya haxa maka dukkan hujja.

11. Shi ya fid da ruwa ta yatsansa,
Har ya shayar da al'ummarsa,
Don Allah ya nuna isarsa,
Bai yi xa kamar Sidi Siraja.

12. Shi ne ya sanya hannunsa,
Cikin abincin al'ummarsa,
Sai da mutum dubu suka qosa,
Albarkacin hannunsa Siraja.

13. Shi ne ya shafa hannunsa,
Bayan akuyar Sahabinsa,
Ta zamo garke a hannunsa,

Albarkacin hannunsa Siraja.

14. Shi ya xauki ice a hannunsa,
Ya zamo takobi a hannunsa,
Ya bayar a qashe maqiyarsa,
Don kwa suma ba su da hujja.

15. Shi ya kira bisahiya a gabansa,
Ta jijjigo ta tsaya a gabansa,
Har ta yo gaisuwa a gurinsa,
Ta nuna ba kama da Siraja.

16. Kai Allah ya bawa *Wasila*,
Sannan ya qara ma da *Fadila*,
Ya cire maka dukka kasala,
A jiki har da zuci Sidi Siraja.

17. Zan dakata a wannan waqa,
*Rabbi* qara wa Bello hazaqa,
Har da masu sauraron waqa,
Bege gurinsa Sidi Siraja.

18. *Rabbana* Allah ka jiqanmu,
Malamai har da iyayenmu,
Har da dukkan masoyanmu,
Ka nuna mana Sidi Sirajo.

19. Sai ni da na rubuta yabonka,
Bello Muhammadu *Madihinka,*
Xan Muhammadu mai qaunarka,
Ni ina sanka Sidi Sirajo.

Tamat

**WAQA TA BIYU**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**

**'Waqar *Khatumul Ambiya'i*'**

**Amshi:** *Ya Khatimul Ambiya'i Wa Imamur Mursalina*

1.Tun da farko na kirayi,
Sunan Allah *Buwayi*,
Taimake ni ka sa ni yayi,
Nai yabo a gurin masoyi,
Har abada ba zan bari ba.

2.Yi Salati *Rabbi* Sarki,
Ka daxa a gurin Ma'aiki,
Xaha ne baban sadauki,
Zavavvan *Rabbi* Sarki,
Na ce kamarsa ba a daxa ba.

3. Allah yai nufin zai raya birni,
Har da qauye *kullumini*,
*Farilla* da *Sunnah* ta yi rauni,
Sai ya aiko Manzo Al'amini,
Yai kiran yaro da babba.

4. Da wannan labari ya sauka,
Kun ga shexan ya yi kuka,
Shi da masu bautar gumaka,
Manufa tasu ma a haqiqa,
Daba a yi wa gunki sujjada ba.

5. Marhaba zavavven mutane,
Da aljan hasken burane,
Mun shaida kai Annabi ne,
Na Allah, kuma mai kira ne,
Domin a bauta wa *Rabba*.

6. Manzo dattijo ne xan dattijan,
Shugaban na mutum da Aljan,
Shi*Munirin* ne *Sirajan*,
Mu rike shi ya kai mai Aljan-,
Narsa, mita yabonsa babba.

7. Ya mafi hasken *lamiri*,
Ya Ma'aiki mai *suriri,*
Mai yawan bautar *Naziri,*
Ya *lazamci istigafari*,
Bai tava sava wa *Rabba*.

8. Zuciya in ta yi murna,
Dole ne fuska ta nuna,
Yau da taron masu qauna,
Arzikin gaba ni da quna,
Kowa ya taho muna maraba.

9. Xaha Manzo mai daraja,
Mun riqe ka kana da hujja,
Ya na Aisha, mijin Khadija,
Tallafa mana ya Suraja,
A fagen begenka babba.

10. Na yi roqo gun *Rahimu,*
Don Muhammadu shugabanmu,
*Rabbi* ka taimaki qungiyarmu,
Kuma ka yadda a unguwarmu,
Yabonsa ba ma bari ba.

11. *Rabbi* ban digiri na girma,
Taimaka wa Mai Karama,
Kan sani da nake ta nema,
Har in cim ma qarin himma,
Duk da yabo na bai yawa ba.

12. Na faxa kogin san *Nabiyu*,
Ga fiyyayen xan fiyyayu,
Gwarzo sirikin ga Aliyu,
Ya fi kowa san marayu,
Har mai iyayen, bai bari ba.

13. Ni yabon Manzo nake yi,
Wanda ka san bai shige yayi,
Ko a da can ma ana yi,
Xan Abdullah xan Qusaiyi,
Mai binsa ba zai rashi ba.

14. Akwai marabar yaro da babba,
Hankalinsu ba ka haxa ba,
Nutsuwarsu idan ka duba,
Za ka gane akwai maraba,
Xan'uwana zo ka duba.

15. Hankali ba tsawo ba ne ba,
Haka ba a gajarta yake ba,
Sannan ba girman jiki ba,
Ni abun da naso ka duba,
Nutsuwarsu ba a bari ba.

16. Masu yabo ku taho mu tare,
Kun ga a cikinmu babu bare,
Kar wanda duk sake ya ware,
Bai da tudu bai da gangare,
Mu'amularsa ba ta yi kyau ba.

17. Sai in ce *Alhamdullilah*,
Bello ni na gode Allah,
Ya aje ni gaban fitila,
Mai kawar da duhun *jahala*,
Kowa ya biyo mu ba zai rashiba.

Tamat.

**WAQA TA UKU**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**

**'Waqar Cetonsa'**

**Amshi:** Allah ka sa mu Cikin Cetonsa Manzo Rasulullah

1. Farko na roqi Allah *Wahabu,*
Damin ni ma ya da xan *habbu,*
In zama gwarzon yabon Habibu,
Shi ne Xaha Rasulillah.

2. Tun da na roqi Allah da farko,
Domin ni ma ya daxan qarko,
Don in zamanto nai qarko,
A gurin yabon Rasulullah.

3. Na yi salatina nai jimla,
Na haxa shi ga Monzan Allah,
Allahu sahabba duk bayin Allah,
Da 'ya'yan matan Rasulullah.

4. Sa da Tijjani bawan Allah,
Mai salatin Monzan Allah,
Ka taimake ni bawan Allah,
Kun ji jika ga Rasulullah.

5.Na sa da Abdulqadir namu,
Babban Gwarzo jikan imamu,
Ni dai da kai na kamu,
Sannu ya jikan Rasullah.

6. Na haxa da Shehu Burhama,
Babban gwarzo mai himma,
Ka ga mai haske da karama,
Gai da kai jikan Rasulillah.

7. Cikin wata na *Rajab* aka aiko,
Mala'ika Jibrilu ya sakko,
Ya zo shi ga Manzan farko,
Wato shi ne Xaha Rasulillah.

8. Sai ya ce in faxa maka, sai ka jiya,
Sai ya fada masa sai ya shirya,
Tafiya can har wato *Samaniya*,
Tare da shi Xaha Rasulullah.

9. Faxar haka ai sai ya shirya,
Ina nufin Mahammadu ya bi shi,
Suka kai har can *Al'arshi*,
Tare da shi har da Saifullah.

10. Sai ya ce nan zan tsaya,
Tafiyarka kai za ka iya,
Sai ya tashi, sai ya juya,
Har ya je shi ga Sarki *Jallah.*

11. Faxar haka ai sai ya qarasa,
Ya je can ga *Khalilinsa*,
Da ya je can sai ya durqusa,
Gabansa Allah *Jallah*.

12. Muhammadu shi ya ga Allah,
To daga nan sai ya karvo *Sallah*,
Ga ta muna yi vauta ga Allah,
Saboda da Allah da Rasulillah.

13. Ya Sarki Allah mai wadata,
Ya masanin sirrin zukata,
Ga ni ni ma ka biyan buqata,
Allah saboda Xaha Rasulillah.

14. Ya Muhamadu baban Binta,
Ya shugaban dukkan halitta,
Ka ga mai haquri mai fahimta,

Shi ne Annabinmu Rasullillah.

*15. Fa qaba qana qausaini,*
*Au'adama* inji *Arrahamani*,
Girmamawa ce a *Alkur'ani*,
Allah ya yi wa shi *Nurullah*.

*16. Subahanal lazi* inji *Arrahamani*,
*Asra bi audihi* kaji bayani,
Shi ya faxa a ciki *Qur'ani*,
Ya yi wa Annabinmu *Sallalah.*

17. Nan zan tsaya na haxa himma,
An gai da ni Bello Mai Karama,
Ya Rabbana kai mana *ilhama,*
Domin Xaha shi Rasulillah.

Tamat

## WAQA TA HUXU

### Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama

### ‘Waqar Girman kai’

**Amshi:** Girman kai Rawanin Tsiya

1. To *Bismillah Rabbi Tabaraka*,
   *Arrahamu* maqagin duniya.

2. Inna rokonka *Tabaraka,*
   Ya *Ilahu* ka haskaka zuciya.

3. Daxo tsira ya *Rabbana*,
   Ga Annabi har *taslimiya*.

4. Daxo tsira ya Rabbana,
   Ga Annabi har Sahabiya.

5. Jikoki na sanya da su,
   Jilani da mai Tijjaniya.

6. Ni na yi kiranku fa ‘yan’uwa,
   Ku bar girman kai gaba xaya.

7. Mu bar girman kai ‘yan ‘uwa,
   Qarshensa yana kawo tsiya.

8. In kana da shi ko xan kaxan,
   Rabbana zai saka shika *Hawiya*.

9. San da *Tabara* yai yo Adamu,
   Ya kirayi Mala’iku diya.

10. Gaba xaya sun bi umarni,
    A ciki nasu sai qwaya xaya.

11. A nan Shaixan kuma yaq qi yi,
    Yai girman kai halin tsiya.

12. A nan *Rabbana* ya la'ance shi.
Sai ya watso shi a duniya.

13. Fir'auna ma yai shisshigi,
Ruwa ya haxe shi gaba xaya.

14. Qaruna ma yai shisshigi,
Qasa ta haxe shi gaba xaya.

15. Lamarudu ma yai shisshigi,
Qarshe an sa shi a *Hawiya*.

16 . Shi ilimi doki ne ga kai,
Sai ka nema kuma kai juriya.

17. Ka yi ilimi xan'uwa,
Zuciyarka ka zam mai gaskiya.

18. Jaki ka san bai da ji,
Sai loda mar kayan wuya.

19 . Ina roqon ka *Tabaraka*,
Ka tsare *qalbun*mu gaba xaya.

20 . Mugun ji mugun gani,
Ka tsare mana *Rabbi* gaba xaya.

21. Shairin mutun ko aljani,
Kare mana *Rabbi* gaba xaya.

22. Na gode Allah ni nai yabo,
Nai Salati ga *Khairil Ambiya*.

23. Mai Karama yai jan hankali,
Ni na yi kiranmu gaba xaya.

24. Baban Maryam ga Fatima,
Da Hasina dukka gaba xaya.

Tamat.

## WAQA TA BIYAR
## Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama

### ‘Waqar Farkon Halitta’

**Amshi:** Farkon Halitta Mukhatari Muhammad kai ne Gatana

1. *Bismillah Allah Rabbani,*
   Allahu ni ma ka haskani,
   In waqe *Sayyadil Kaunaini*,
   Muhammadu shi ne gatana.

2. Ya *Rabbi Allah Rahamani*,
   Domin ni in ka haskani,
   Buqata Allah babu saura ni,
   Sai dai in waqe *Badadina*.

3. Yi dubun salati Rabbani,
   A gareshi xan Adanani,
   Mata da ‘ya’ya nai imani,
   Ba kamarsa Xaha *Badadina*.

4. Bari in saka da Sahabbaini,
   Abubakar nasu da Umar ni,
   Aliyu Usman Zul Nuraini,
   Domin sun so shi *Badadina*.

5. Sa da Abdulqadir Jilani,
   Shaihunmu Ahmadu Tijjani,
   Na haxa da *Gausul* zamani,
   Burhama shi ne tsanina.

6. Ya Rabbana kai min auni,
   In koma in hau kan tsani,
   In dinga baitika launi-launi,
   Domin in ba wa *Badadina*.

7. Kullum in zan buxe bakina,
   Sai nai yabon *Maulana*,

Shi ne Xaha macecina,
Domin fa shi ne gatana.

8. Don haka dukkan aikina,
Yabon Muhammadu aikina,
Don haka dukkan aikina,
Sai na saka shi *Badadina.*

9. Ku ji ni ya *Ikwani*,
*Adi'ullaha wal ma'amuni*,
*Rasulahu* ga dukkan *kauni*,
Aya ta nuna *Badadina*.

10. Allahu shi ya yi bayani,
Uwa uba har kakanni,
Da dukkanin mai imani,
In ya so Muhammadu gatana.

11. Allahu ka ji qaina ni,
Uwa uba har kakanni,
Da dukkanin mai imani,
In ya so Muhammadu gatana.

12. Na gode Allah *Rabbani,*
Tun da na haxe buqatani,
Na yabonsa shi Mai Qur'ani,
Xaha Muhammadu gatana.

Tamat

**WAQA TA SHIDA**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**

**'Waqar *Wasilah*'**

**Amshi:** Kai ka Zamo *Wasila* Tsakanin Allah da Bayi

1. Ya Sarkin sarauta,
   Ka biya min buqata,
   Yarda in sarrafa ta,
   Waqa ta yabo da nay yi.

2. Ya *Rabbi* ka taimake ni,
   Komai na bixa ka ba ni,
   Allah ka horan bayani,
   A dukkan yabon da nay yi.

3. Allah kai Salati ba iyaka,
   Gwargwadon dauwamarka,
   Da gwargwadon iliminka,
   Daxa shi gurin *Nabiyi*.

4. *Alai* Allah har Sahabi,
   Na *Nabiyun Awwabi*,
   Masu girma da *hubbi*,
   Ba kamarsu gurin *Nabiyi*.

5. Shehunai duk na *Xariqa*,
   Inuwarsu ta zam sarqa,
   Gaisuwarsu na sa a waqa,
   Da nai ta yabon *Nabiyi*.

6. Da ma ni tun da na taso,
   Manzan Allah nake so,
   Don ya zamo mini sosan,
   Wanke zunubi da nay yi.

7. Ya Xaha *Nurul Anwari*,
   Ya mai kyauta da qari,

Xaha ba zai maka gori,
Komai hidimar da ya yi.

8. Komai ka ga mun ka samu,
Daraja tasa Allah ya ba mu,
Haka ne gun bayi *Rahimu*,
Sannan *Ra'uf* gurin *Ilah*i.

9. *In kuntutu hibbunnallah*,
*Fattabi'u Rasulillah,*
Mu bi Manzan Allah,
Umarni *Rabbi* yai yi.

10. Matsayi nasa ya kaxaita,
Yai daban a cikin halitta,
Duk mai neman ravauta,
Ya kama yabon *Nabiyi*.

11. Xaha kai ne mai *Wasila*,
Kuma kai ne mai *fadila*,
Kuma kai ne mai *Sallah*,
Vautar da ta tara bayi.

12. Xaha ko gun halinsa,
Da cikin matsayinsa,
Allah ke yabonsa,
Domin qyauta ga bayi.

13. Xaha ya ziyarci Allah,
A can aka ba shi Sallah,
Sai ya roqi Sarki Allah,
Jin qai Rahama ga bayi.

Tamat.

**WAQA TA BAKWAI**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**
**Waqar Matsayi Nasa**

**Amshi:** Yaka Duba-Duba Malam Duba Matsayi Nasa Sayyadina

1. To*Bismillah* Allah,
   Yai wata bai *qalah*,
   Dare da rana jimla,
   A ciki nasu ba mai *kalamuna.*

2. Allah shi ne yai yi jallo,
   Ya yi ni ya sa mini Bello,
   Baki na ya sa mishi sallo,
   Har da launin begen *Khalikuna*.

3. Shi ne yai rana ta qyallo,
   Haskenta ne ya kallo,
   Duniya fari har falo,
   Ba inda ya voye masa *Khalikuna*.

4. Ya *Rabbi* qara Salati,
   Domin na yi *Salatul Fati*,
   Gun Ahmad abban Fati,
   Nasa *alaye* da Shaihuna.

5. Kututture yai nishi,
   Don rashin *Baquraishi*,
   San da za ya tashi ya bar shi,
   A masallaci ne Annabina.

6. Kututturen a gabansa.
   San da ya yi kukansa,
   Manzo ya sa hannunsa,
   Yai mai alqawari *Nabiyuna.*

7. Ga damo yankakke,
   Shi ma ya yi sheda take,

A nan  a gaban bafatake,
Ya yi shedar aiken *Nabiyuna.*

8. Sannan ga ma raqumi ,
Shi ma ya yi kalmomi,
A gun Xaha mai hidimomi,
Qara ya kawo wa *Nabiyuna*.

9. Haka ga ma girgije,
Shi ma ya sheqo a guje,
A gun Manzo na ya je,
Yai mai inuwa daga rana.

10. Shi ya kira wo wata,
Duba *Iqqitirabati sa'ata*,
A nan sai ya tsage wata,
A gaban Manzona *Shafi'una*.

11. Ya baban Mu'azzam,
Tun da na sha Zamzam,
Har ya cikan ciki dam,
Ka ba mu mu sha kuma *Kausarina.*

12. Malam duba matsayi nasa,
Matsayin da *Ta'ala* yai masa,
Xaukakar da Allah yai masa,
Yarjajjen Allah *Kaliquna*.

13. Duba tun a farkon fari,
Allah ya yi masa*Nuri*,
Ya sa maka suna Muktari,
Hasken Allah *Khalikuna*.

14. Annabi mai haske ne,
Kuma hasken*Zati* ne
Kuma Manzon Allah ne,
Yarjajjen Allah *Khaliquna.*

15. Ya Xaha*Nuril Anwari,*
Ya *Xahirul Muxahhiri*,
Ya *Bashirul Naziri*

Kai nin qyauta Muhammadina.
Tamat

**WAQA TA TAKWAS**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**
**'Waqar xan Suwaiba'**

**Amshi:** Xan Suwaiba Annabi xan Suwaiba

1. Bismillah ni da farko kai na roqa,
Ya *Ilahu Rabbu* maqagin *halaqa*,
Kai mutane kai dabbobi kai *Buraqa*,
Ba ni haske ni Bello na shirya waqa,
Ka sa ba kuskure baiti yai ta zuba.

2. Na roqe ka *Tabara* kai min agaji,
Nai kiranka kai min agaji,
Wanga waqa zan yi ne kan buxe qirji,
Na Muhammadu mai kyau in faxe shi ku ji,
Yan da aka wanqe zuciyarsa xan Suwaiba.

3. Kafin in je bayanin nai roqon *Rahimi,*
Yi Salati *Rabbani* har da *Taslimi*,
Gun Muhammadu Manzo shi *Imami*,
Mata 'ya'yansa mai garin *Baitul Harami*,
Guda cikin begensa ba zan cire ba.

*4. Wa'alihi* Manzan Allah har sahabbai,
Mata 'ya'yansa *Rabbi* ka nunka dubbai,
Da dukkanin jikokinsa ka sa sharifai,
Har da dukkanin makusanta waliyyai,
Har Tijjani Jilaninsa ba zan bari ba.

5. Bari in dawo kan dalilin yin *qasida*,
Ta da zan yi a kan Mahmuda,
Yana shekara huxu zuwa ta shida,
Kan abin da aka gani na *ajabi* zan fid da
Rabbi sa guda a ciki ba zan bari ba.

6. Lokacin yana gurin shayar da mama,
Sai ta yaye shi ummuna Halima
Yana bin yara kiwo Mai Karama

Su kan je su dawo wannan ba nadama,
Da Muhammadu yarjajjen Allahu *Rabba*.

7. Wata ran yaran sun dawo sun yi jere,
Suka ce da Halima mun ga wasu farare,
Na mutane ne sun iske mu tare,
Amma fa da xanki kaxai shi suka ware,
Suka tafi ba mu qara ganinsu ko ba.

8. Halima ta ce zancan nan yana ba ni tsoro,
Ta fito da sauri nan wajen sai ta iske taro,
Tana dubawa ko ta ga wannan yaro,
Can sun bi sawu sai ga yaron ya shararo,
Sai ta gan shi ba da baqin ciki ba.

9. Da ganinsa Manzo ana ta yi mata barka,
Tana tambayarsa shin ina suka kai ka,
Ta ce Aminu shin wane ne ma ya ja ka,
Ya ce Jibrilu ne shi da abokinsa Mika,
Ilu ba kowane a cikin duniya ba.

10. Ya ce muna cikin wasa ne sai xaya ya cafe ni,
Muka je mu cikin dutsen can ya kai ni,
Ya kwantar da ni ya rigirgine ni,
Nan suka buxe kirjina *bissi sikini*,
Duk bai kai zafin cirar qaya ba.

11. A nan ne suka fito da zuciyata,
Suka yanka suka fid da jinin jikinta,
Suka zubar kuma nan suka xauraye ta,
Suka sa hikima a ciki da yawan fahimta,
Da cirowar da mayarwar bai minti bakwai ba.

12. A sannan ne suka tashe ni zaune,
Sai suka kira ni zavavvan mutane,
Domin kwa martaba tasa ta fi wane,
Sau dubu xari uku domin su yi aune,
Har abada ba a yi kamata tasa martaba ba.

13. Da dai muka dawa lafiya sai,
Na ce da mijina za ni mai sai,
Gurin iyayensa na fi so in kai sai,
Mijina ya ce don mene ne za ki mai sai,
Tun bai qwashe bakwainin shekara ba.

14. Sai na ce don nai mugayen mafarkai,
Cikin mafarki ne tsutsuwa ta xaukai,
Ana nemansa cikin daji ta saukai,
Wasu na kan jakuna wasu ko dawakai,
Sai na farka hankalina bai nutsu ba.

15. Sai mijina ya ce lalle ki kai shi,
Gun mahaifiyarsa da kakansa su gan shi,
A yayin komawa sai ki barshi,
Sai ta ce da ni ni dai in na kai shi,
Ba na buqaci komowa da shi ba.

16. Muka isa Makka muka iske Nasara,
Da Yahudawa suna ta hira,
Suna cewa *Injila* da *Attaura*,
Sun yi bayanin Annabi mai tsira,
Ga shi har yau ba a haife shi ko ba.

17. Suna cewa yau da xauke Isa,
Aka taho har yau zuwa haihuwarsa,
Da xauke shi zuwa yau shekarunsa,
Xari shida ke nan har yau ba amonsa,
Ba su san suna zaune suka wuce ba.

18. Muka rava Ka'aba ya yi zaune,
Ya jira ni don zan zagaya ne,
In dawo wai in iske shi zaune,
Na duba warin don in gan shi zaune,
Ban gan shi ba hankalina bai nutsu ba.

19. Nan ne na jingina da Ka'aba ina ta kuka,
Ana haka sai ga wani tsohon boka,
Ya ce don mene ne kike ta kuka,
Na ce yaro na shayar na zo za ni miqa,
Na'aje shi na zo ban tar da shi a gun ba.

20. Ya ce zo in ba ki shawara game da saqo,
Ki je ki samo gumba da zuma ki saka a qoqo,
In kin samo kin saka kuma sai ki leqo,
Ni kuma in kai ki wurin da akan yi roqo,
In kin sa a yaronki ba zai vace ba.

21. Daga jin haka ni kuma ban tsaya ba,
Sai na sayo zuma na haxa da gumba,
Na sa sabon qoqo wanda ba a tava ba,
Na doshi gurin bokan bai tsaya ba,
Sai da ya kai ni wurin gunkinsa babba.

22. Da muka je ya ce zauna ki buve baki,
Ki faxi 'yan buqatun zuciyarki,
Gaban mai alfarma don ya ji ki,
Abin da kike so dukka za ya ba ki,
In kin sa a burinki ba zai daxe ba.

23. Nan da ta zauna ta ce *Nobel* zuwa na yi,
Da yaro don shayar da shi na yi,
In kai shi gurin iyaye nai,
Mahaifiyarsa Amina don ta ga nai,
Gunki ya yi fushi tun ban faxi ba.

24. Ina faxar haka nan gunkin ya vare,
Ya zubo gabana dukka tare,
Duk ya faskare a gabana dukka tare,
A nan kuwa ni da boka ne a tare,
Kamar ya mare ni ba don Allah ya hana ba.

25. Sai wani ya taho ya ce ki gaya wa kakan,
Sa shi ya san inda zai nemi jikan,
Na san duk su taru da dukkan,
Quraishawa kan raquma wasu ko a jakan,
Su dai da ba su san inda ya sa qafa ba.

Tamat

**WAQA TA TARA**
**Marubuci Bello Muhammad Aji Mai Karama**

**Waqar 'Yarjajjen Allah'**

**Amshi**: Ni Dole in Yabi Yarjajjen na Ubangijina

1. Da sunan Maqagi,
   Na na kaji agwagi,
   Ya Allah ka tsare ni wargi
   San da zan kira Annabina.

2. Kai dubun Salati *Rahamani,*
   Har da aminci *Mamnani*,
   Allah daxa wa Aminu,
   Muhammadu hasken idona.

3. Har *alaye* ka sa da sahabai,
   Abubuakar da Umar nake bai,
   Ga Usman Ali in ka dubai,
   Yana kashe mai qin Annabina.

4. Amma na fito yanzu zan je,
   Fadar mijinsu Dije,
   Sai dai ba mai bi na mu je,
   Sai mai yabon Annabina.

5. Amma kafin in zam tahowa,
   Dole in nemo masu rakawa,
   Kun sa can da fadawa,
   Kar su hanan ganin Annabina.

6. Bara in je ga Abul Abbasi,
   Kun ji jika gun*Ma'asisi*,
   Na Annabi shugaban dukkan jinsi,
   Farko da qarshe Annabina.

7. Na sanyo Hassan sai Usaini,
Bara in je ni gun Jilani,
Shi ma in mai bayani,
Irin abun da ya dami raina.

8. Xan Amina mafi daraja,
*Rabbana* ya ba ka hujja,
Wadda ba ta ga mai daraja,
Wani ba kai ba Annabina.

9. Xan 'uwana ya ka duba,
*Shabba*ki da na yi duba,
Lalle akwai *Muhibba*
Ziyara Muhammadina.

10.Kullum ina roqon*Tabara*,
Ga *jebi*na babu naira.
Allah ka mai da ni ziyara.
Madina birnin Annabina.

11. Xan'uwana yaka duba,
Allah ba sama kawai yake ba,
Sannan ba a qasan yai gida ba,
Ba inda za ka duba ka ce ba Ubangijina.

12. *Rabbana* ya kira ka ka je,
In da ba wani wanda yaj je,
Ko a tunani cikin mazaje,
Wani ba kai ba Annabina.

13. Sidi yai sujjada da goshi,
Nan ga wanda ya xaukaka shi,
*Rabbi* ya ce ya ma zo *Arshi*,
Ya Xaha hasken Ubangina.

14. Mun kira ka mu ba ka Sallah,
Ga sharuxa na ta dukka jimla,
Mu riqa *sunnah*da *farillah,*

Masoyan Muhammadina.

15. Allah ba qasa kawai yake ba,
Sannan ba a qasa yai gida ba,
ba inda za ka duba,
Ka ce a gun ba Ubangijina

16. Ya matsera ya madafa,
Ya mafi tsausan mahaifa,
Bargonka sa min in rufa,
In wake zunubi na raina.

17. *Rabbi* ka haskan zuciyata,
Sannan ka gyara tunaninta,
Ya Allah sanya ambatonta,
Daga Allah sai Annabina.

18. Amma da damuna ta sauka,
Sirrika in bi in shusshuka,
Kan mu je ga kaka,
In yi ta girbin yabo da qauna.

19. Gonata ta yi yabanya,
Mai san ta sai ya kama hanya,
Yai ta bege ga *Nabiya*,
Masoyin Ubangijina.

20. Gonata ta gama komai,
Tun da na yi fari na yi mai mai,
Roqana mu sam muqamai,
A can fadar Ubangijina.

21. Ba ni da guru ban da layu,
Na sake hanyarku gayu,
Na yi riqo ga kakan marayu,
*Mujittaba* don ya ceci raina.

Tamat

## RATAYE NA UKU

## Sani Abubakar Hotoro

## WAQA TA XAYA
## Marubuci: Sani Abubakar Hotoro

### Waqar 'Aure'

**Amshi:** Don Allah mu yi Aure, Aure Sunnar Manzona Ribar soyayya ita ce qarshe

ai Aure

1. Allah yi Salati ga Muhammadu *Nuruzzati*,
*Sayyadin Sadati Xaha Sahibul Darajati*,
Mai halin girma me jikoki *Ahlil baiti,*
Duk ina qaunarsu an same su ta hanyar aure.

2. Ina yara qanqana ku taho ku fahimci batuna,
Da samari da 'yammata ku zo ku fahimci batuna.
Har ma da ma'aurata ku matso ku ji batuna,
Waqa ce na yi ta na yi ta ne harkar aure.

3. Aure babban lamari ne ba harkar wasa,
Wasu su xau aure al'ada ba addini ba,
Addini ne shi bauta ce ba 'yar qarama ba.
Kuma Manzan Allah yana tare da mai son aure.

4. Ni wannan zamani ya saka ni ina wasi wasi,
Wasu su xau rayuwarsu da faxi *ayyuhanassi*,
Ba su yin mu'amala da mutumin da ba shi sisi,
Wanda ba shi da sisi ya za su ba shi 'ya ya yi aure.

5. Shawara ga iyaye in mutum yana son 'yarku
Sai ku binciki halinsa kan ku ba shi ya auri xigarku,
Binciken addini wajibi ya zamo a gare ku,
Kar ku duba tufafi ko mota da gidan da ya qere.

6. In ya kawo kaya kar a yi ta tozarta shi,
Kar a dinga maganganu qanana don tozarta shi

A wani gun ka ga tsohuwa ta tsaya tana tozarta shi,
Har ta rinqa gaya musu wa za ya ba wannan aure.
7. Sai ta xauko labari wata ‘yar mai girma,
Kun ga auren wance akwati bakwai aka yo ma,
Ga gida qerarre ga mota *Homa* ta alfarma,
Kun ga yadda ake yi shi wannan ya zai iya aure.

8.Ta manta Ubangiji shi yake azurtawa ma,
Yau ba ka da komai gobe ka zam mai girma,
*Rabbi* ya hore ma har a rinqa babu yi kai ma,
Ka ji ikon Allah yau mara shi Allah ya hore.

9. Ba ruwanta da cewa ta bai wa xa mai son addini,
Mai tsoron Allah mai riqo da sunnar xan Adnani,
Mai girma kowa xan kirki mai yin tsantseni,
Ba ruwanta da wannan bai da wannan ta ture.

10. Ta fi so ta ga mai dala da mota da gida kyakkyawa,
Ya zo gun ‘yarta wannan ‘yar ita ce yar baiwa,
Nan sai ka ji ta ce ‘yar nan Allah ya yi miki baiwa,
Wa zai bai wancan ba ajinki ba ne gun aure.

11. ‘Yata kyakkyawa ya za na ba wa qaton wawa,
Komai nitsuwarsa ba shi da naira ya zama wawa,
Ita ma yarinyar hankalinta shi ake jujjuyawa,
Tun tana qaunarsa sai ta qi shi a harkar aure.

12. Mai dalar mai moto qila ba xan kirki ne ba,
Ba ruwansa da komai bai xau addini komai ba,
Ga shi kin ba shi ‘yarki ya ya ba zai yi miki wauta ba,
Ya saya kin ba shi to qarshe kya ga sakin aure.

13. Ya iyaye maza ya kamata ku zam tsayayyu,
Gun auren ‘yarku kar ku zam tamkar gajiyayyu,
Wata ran babu ranku ‘ya’yayen sun zamo marayu,
In ka bai xan kirki bata shan wahala gun aure.

14. Mai dalar mai motar ba kowanne xan banza ba,
Da yawa a cikinsu da ‘yan mutumci ba qarya ba,
Wani gun bin Allah ko sawunsa ba ka risqa ba,

Yana da tsoron Allah sannan ya san darajar aure.

15. Shawara ga ma'aurata musamman ango da amarya,
Ku sani yau kun shigo wani fage da ba a qarya,
Sai dai a yi gaskiya wajen haquri a yi juriya,
Haquri ribar dukkanin mutum mai aure.

16. In ya ce ki yi na yi in ya ce ki bari bari ya fi,
Babu cecekuce balle zagin tsofaffi,
Ki tsaya ki bi aure kar ki yi wa ango laifi,
Shi ke kawo danqon soyayya gun aure.

17. Ya kai magidanci ko in ce ango na amarya,
Ka tsaya ka fahimci rayuwa yau ta juya,
Ji tsoron Allah komai za ka yi wa amarya,
Sai kai adalci don ka sami ribar aure.

18. Yau ma na dawo vangaren ango da amarya,
Ki riqe angonki ban da yawo ba kuma qarya,
Ki zamo mai tsafta gun miji kar ki jayayya,
Sai ki zam mai riba kin martaba sunnar aure.

19. Ku 'yammata in mutum ya zo yin hira,
Ki tsaya ki fahimci magagganun ki xau gyara,
Wannan hanyar kaxai za ta sa ki gane tsira,
Za ki san mai yaudara za ki gane mai yin aure.

20. Waqar nan da na yi ban yi ne don kushe wani ba,
Ba don zagi ba ba don yi wa wani habaici ba,
Ba kamar yadda aka ce ta faru a kaina ba,
Wai an yi min ne lokacin da na je neman aure.

21. Haka ba daidai ba maganganun ba haqqun ne ba,
Na yi don faxakarwa ba don kushe wani xa ba,
Da mu lura mu gane hakan ba zai kai mu ga mafita ba,
Wannan zamani mai mutumci ya rasa aure.

22. Nan za na taqaita wannan waqar ya *Ikwani*,
Sai ni da na tsara waqar suna na ne Sani,

Abubakar Saddiqu babana ne da ya Haifa ni,
Daga nan Hotoro ni ne nai yo waqar aure.

Tamat

**WAQA TA BIYU**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**

**‘Shugaban Bayin Allah’**

**Amshi:** Ya Muhammad Shugaban Bayin Allah ban ji banga Wanda yai
ka girma ba

1. Na fara da ambaton mahallicina,
Wanda gare shi nake miqa buqatuna,
Dukkan arziki yana gareka maqagina,
Shi ke ban abin da ma ban roqa ba.

2. *Allahumma Rabbana* ka kiyaye ni,
Ka tsare mini harshe kar na yi savo ni,
Kar ka sa na furta kalma mai muni,
Na shiga hallara da ba gun wasa ba.

3. Allah kai daxin amincika da tsira,
Ga mafi xaukakar halitta mara tsara,
Wanda ka ba shi *Khafi* har da *Tabara*,
Alayensa kaf ba zan ware guda ba.

4. Kan na wuce na fara wannan baitoci,
Sai na gai da jarumai masu mutumci,
Wanda ya qi su yai wa kai nai ganganci,
Duk vautarsa *Rabbi* ba zai karva ba.

5. Dole na gai da ku Sahabban Manzona,
Tare da ba mata da ‘ya’yan Manzona,
Sayayadina Abubakar ga kuma Usmana,
Sa da Umar bai san tsoro ba.

6. Ga ni da baitukan yabon *Sirillahi*,
*Sayyadina Rasulu Sayyadina Mahi*,
Nai duba kaf hallitta wallahi,
Allah bai yi mai cikar daraja tai ba.

7. *Almukhatari Rabbi* ya fifita ka,
Ya zave ka ya zave ka ya zave ka
Da rayukar ya rantse mai Makka,
Wa Allah ya yi wa haka in ba kai ba.

8. Ran yaqin *Badar*abin ba qarami ba,
Kai dan qa kai jifa ba kai kai ba,
Ya kai xan'uwa idan ba ka gane ba,
Ayar na nan ba nine na faxa ba.

9. Annabi ne ya xebi tsakuwa maulana,
Ya yi jifa idan *Kuffaru* Ma'aikina,
Sai Allah ya ce da Sidi masoyina,
Ni ne nai jifan ba kai ne kai ba.

10. Dubi batun Khatada ya mai sauraro,
Ya yi rashin ido idan yan zazzaro,
Sai ga shugaban da ba ya yin qwauro,
Ya yi masa magani kamar bai cuta ba.

11. An sa mai guba a nama Manzona,
Duk domin a cuci mai daxin suna,
Sai Allah ya kare qimar maulana,
Naman ne ya mai bayani ba wai wani ba.

12. Malam rayuwa ba tai amfani ba,
In ba ta sallama wa jagorana ba,
Kuma qarshe ta sha azaba da uquba,
Ba jin qai ga wanda bai so Manzo ba.

13. Ya Rahamar Ubangiji ga dukkan bayi,
Duk mai sanka har gurin Allah ya yi,
A masoyanka ne ake gane waliyi,
Ban tava jin wali ga mai inkari ba.

14. Duk maqiyinka Sidi bai yi tunani ba,
Duk rahamar Ilahu ba za ya yi mai ba,
Sannan ba shi da qima a gurin Rabba,

Ba kuma za ya zam cikin 'yantattu ba.

15. Baban Faxima masoyin dukka bayi,
Duk bauta da kai kaxai za a yi koyi,
Kuma qaunarka wajibi ce gun bayi,
Wanda ya qi ka Sidi bai yi nagarta ba.

16. Kyan siffa da kyan hali ka wuce kowa,
Tsarkin zuciyarka ta nashe ta kowa,
Domin kai Ubangiji ya yi wa baiwa,
Don baiwarka xa ba za ya kwatanta ba.

17. Mai haquri da juriya Manzan Allah,
Mai iya taimakawa duk bayin Allah,
Ga shi gwanin mu'amula Manzan Allah,
Ko cutar sa kai ba zai rama shi ba.

18. Annabi in ya taka dutse ba wai ba,
Sawayensa na fita ba qarya ba,
In kuma rairayi ya taka kai duba,
Sam ba za ka ga sawayen Manzo ba.

19. Sunan mai karanta waqar nan Sani,
Xa ga Abubakar mahaifinsu Usaini,
Xan Kawon Kudu kar da ku zarge ni
Daga Hotoro ina nan ban qaura ba.

20. Nai waqar saboda girman Manzona,
Kuma ta zamo hadiya ga mahaifana,
Ta dalilinsu ne na waqe ma'aikina,
Allah saka musu ba don ni ba.

Tamat

**WAQA TA UKU**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
**'Mai Cikar Xaukaka'**

**Amshi:** Mai Cikar Xaukaka da isa Ma'aiki Mijin Hafsa

1. Dukkan aikin da zan xauko,
*Rabbana* nai kira farko,
Don abin nawa ya yi qarko,
Allah nake sanya sunansa.

2. Bismillahi gwanin Sarki,
*Rabbana Malikil Mulki*,
Zan yabon *Sayyadil Kalqi*,
Ahmad Muhammadu sunansa.

3. Allahu kai ne maqagina,
Kai kai dare ka yo rana,
Kai mai kyau da mummuna,
Mai hankali ke tunaninsa.

4. Tsira amincin ka qarawa,
Mustafa mai yawan baiwa,
Adadin ya zarce qidayawa,
*Alai* sahabai abokansa.

5. Haxa sahabansa yan baiwa,
San Annabi sun wace kowa,
In za shi yaqi suna da yawa
Wasu na gabansu wasu bayansa.

6. Almusxafa karvi baitoci,
Wanda zan maka don ka ci,
Ka fi kowa yawan 'yanci,
Allah ka sa mu ga mujin Hafsa.

7. Anbatonka ya zamo dole,

Ko in ce ya zamo lalle,
*Rabbana* ya saka dole,
Don ko a Sallah da sunansa.

8. Wa ya san *Rabbi* bayan kai,
Waya je gunsa sai dai kai ,
A shimfidar kusanci aka kai
Shi ya je ya hau da takalminsa.

9. Annabi *Rabbana* ya ma baiwa,
Kyan suffa ka wuce kowa,
Sai di mutum yai ta dambarwa,
Ba wanda zai san kamaninsa.

10. Mai bushara gurin bayi,
Mai gargaxi wajen bayi,
Wayyo ni wayyo ni ya zan yi,
Kullum a raina tunaninsa.

11. Ni nai iyakar tunanina,
Na kasa gane Manzona
Na yi roqo ga Allahna,
Ko da a barci in ga siffarsa.

12. In yana zaune kyakkyawa
In ya miqe kyakkyawa,
Ga ka wanda ba ka inuwa,
Shin ya kake ne mijin Hafsa.

13. Annabi idan ya buxe bakinsa,
Akwai wushirya haqoransa
In zai magana mijin Hafsa,
Haske ke fita a bakinsa.

14. Kai ka zo mana da *alkhairi*,
Mun kasance cikin tsari,
Kan zuwan *Sayyadil Bashari*,
Kowa yana tafka shirmansa.

15. Da zuwanka Annabin Allah,
Sai Ma'aiki ya ce musu *lalah*,
A daina bautar wanin Allah,

Dukkan gumakansu ya rusa.

16. A bi ka a da ce Manzona,
A qi ka a ga fushin *Rabbana*,
Mai sanka zai shige *Janna,*
Wallahi Allah yana sansa.

17. Annabi kai ne amintance,
Siffarka ta wuce a kwantance,
Don ka fi mazaje ka fi mace,
Ka zarce Adam da 'ya'yansa.

18. Ni ina sanka Manzona,
Fiye da qaunar abokaina,
Da *ahalina* da dangina,
Na fifita son mijin Hafsa.

19. A nan zan taqaita waqena,
Wanda nai wa ma'aikina,
In an tambaye ka sunana,
Ka ce da su Sani sunansa.

20. Ka ce da su Sani sunana,
Abubakar ne mahaifina,
Allah ka yafe wa babana,
Laifin da yai duk girmansa.

21.'Yan'uwa masu sauraro,
Nan Kano nake a Hotoro,
In ka zo kad da ka ji tsoro,
Ka yi tambaya za ka ga gidansa.

Tamat

**WAQA TA HUXU**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
**'Ubangijin Halittu'**

**Amshi:** Ubangijin Halittu Allah ka La'anci Masu Kushe Annabina

1. *Bismillahi Rabbi*,
Allah ka haskaka *qalbi*,
Zan yi yabon *Habibi*,
Hasken Ubangijina.

2.Ya mai kashe mutane,
Kuma mai raya mutane,
Mai taimakon mutane,
Kai ne Ubangijina.

3. Allahu kai na roqa,
Tsira aminci ninka,
Gun shugaban ma'aika,
Adadin ya fuce sanina.

4. *Alai* haxa sahabbai,
Su suka xau takubbai,
Sun sare wasu kafirai,
Don kare Annabina.

5. Kuxin fetur aka qara,
Muka fito muna ta qara,
Muna ta tada qura,
Wai gwamnati tai varna.

6. Muka rinqa zanga-zanga,
Wasu na ta yaga riga,
Yau Annabi aka zaga,
Mai mu kai a zamanina.

7. Ni duk da ban da sanda,

Ban da bindiga da adda,
Shi ne na yo *qasida*,
Don waqe Annabina.

8. Ya Ubangijin Halittu,
Wasu kafirai vatattu,
Su ne sukai rubutu,
Don kushe Annabina.

9. Wasu kafiran mutane,
Wasu kafirai vatattu,
Wasu 'yan Amerika ne,
Suka shirya fim na varna.

10. Allahu ga ka ga su,
Ka san abin nufinsu,
Sharrin mayar shi kansu,
Da sukai wa Annabina.

11. Allah sa musu cuta,
Cutar da ba irinta,
Da kuturta da makanta,
Kuma ransu yai ta quna.

12. Wallahi kun yi hauka,
Haukar da ta fi hauka,
Allah ka sa su afka,
Wuta ya Ubangijina.

13. A wutar ka sa su maye,
Idansu ya yi hawaye,
Ga su banzaye wawaye,
Maqiyan Muhammadina.

14. In ban da ku qazamai,
Wa zai qi mai muqamai,
Wanda ya zo da komai,
Shi Rahamar Ubangijina.

15. Qaryarku 'yan ta'ada,
Ku ne ke ta fid da,

Kalamai har a jarida,
Don kushe Annabina.

16. Tun kafin mutursu,
Allah canza kalarsu,
A gaba ma a tsane su,
Su zanto munana.

17. Duk ni'imar da kai musu
Jin daxin da ka ba su,
Allah ka kwace musu
Tun da sun qi Annabina.

18. Kafin na je tsayawa,
Zan qara sallamawa,
Ga abin girmamawa,
Annabi Muhammadina.

19. Kai ne gagara gasa,
Lamarinka babu wasa,
Muhammadu mijin Hafsa,
Kai ne Rahamar Ubangijina.

20. Wataqil mai sauraro,
Ya buqaci wa ya tsaro,
Ni ne xan Hotoro,
Mawaqin Muhammadina.

21. Sani Abubakar ne,
Mai yabo ga Annabi ne,
A cikinsu qarami ne,
Mawaqan Muhammadina.

Tamat

**WAQA TA BIYAR**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
**Khairil Bariya**

**Amshi:***Sayyadil Wujudi* Sirri na Allah *Khairil Bariya*

1. Farko da sunansa mai bayar da kyauta,
Allah *Ganiyu* kai kaxai kake don ka wadata,
Kai ke da arzikin komai ka azurta,
Mun shaida Allah kai kai ne xaya.

2. Sarkin da bai da mata ko xa da jika.
Mu kai muke wa bauta da ka tsarkaka,
Mulkin mutum da Aljan duk na gareka,
Sarari da loko wani baya vuya.

3. Allah ka qara tsira da yawan aminci,
Ga *Sayyadil wara* mai tarin mutumci,
Shi ya rusa kafirai ya yaxa Musulunci,
Ya zo da gaskiya kuma ya rusa qarya.

4. Mata da 'ya'yansa *Rabbi* ka ba su yarda
Don matarbarsu ta fi ta kowa a tsada,
*Ahalin* gidan ma'aiki da xa ba su shaida,
Har T*abi'ina* kar ka bar su baya.

5. Sallama gare ka ya limamin hallitu,
Manzon Ubangiji baban Zahra Binta,
Kai ne ka zo da hasken shiriyar hallita,
Ka shirya duniya kan hanya xaya.

6. Kan take masu gasa da cikar isarka,
Ka rusa masu inkarin matsayinka,
Ko da Abu Jahil da yake nuna qinka,
A yau ka ga bayansa *Khairil Bariya*.

7. Shi wai ina Abu Lahabi xan asara,

Yau ka ga bayansa ba shi ba gadara,
A gaban *tabbat yada* sunan wa ka qara,
Shi ne Abi lahabi jagora a qarya.

8. Ya sansanin sanin soyayyar *Ilahu*,
Ya martabar ibada ka zarce Shehu,
Aikin ka ne ya shafe na Isa Masihu,
Daga kanka an gama ba qarni a baya.

9. Xan Amina da Abdu tsatsan Hashimawa,
Ka sha gaban hallita har Annabawa,
Kai ne ka zo da doka mai ba da sha'awa,
Kai ne kamanci mai rusa qarya.

10. Annabi Muhammadu dole a sallama ma,
Domin Ubangijina ya ba ka girma
Komai yana qasanka kai ne a sama,
Daga kanka an gama ba wani a baya.

11. Ya Manzan Allah dole a girmamaka,
Domin Ubangijina ya xaukaka,
Allahu ne ya haxa sunansa da naka,
Ga sunan Allah ga na *Khairil Bariya*.

12. Waye mala'iku ke inuwa gare shi,
Domin su kare zafin rana gare shi,
Waya kira wata ya zo har gaban shi,
Amsar bayanin *Khairir Bariya*.

13. Waye idan mutum bai yi riqo da shi ba,
To rayuwarsa ba za ta yi amfani ba,
Jin qan Ubangiji ba zai tava samu ba,
Sai kai Muhammadu *Khairil Bariya*.

14. Ya mai kyautar ban mamaki ga bayi,
Kyautar da babu tsoron talauci idan zai yi,
Ni kyautar da nake so ta ganin Nabiyi,
Ka yarda na ganka da idaniya.

15. Ya mai Abubakar mai Umar *Imami,*
Ya mai Aliyu ya mai Usman *karimi*,

Ya wanda ambato nai sai da *takarimi*,
Annabi Muhammadu *Khairil Bariya*.

16. Tilas na gai da limamin jarumawa,
Duk jarumi ba zai kai ka ba ka fi kowa,
Duk qarfin arne kai ke sa shi kuwa,
A gaishe ka Annabi *Khairil Bariya*.

Tamat

**WAQA TA SHIDA**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
**'Kai Nake Qauna'**

**Amshi:** Ya Rasulullah Kai nake so kai Nake Qauna

1. Dukkanin mai son aikinsa,
Aikinsa yai kyau shawara gunsa,
Sai ya sa Allah a lamuransa,
Tun da shi ke mulki na ko'ina.

2. *Bismillah Rabbi* Allahna,
Na kira sunanka Sarkina,
Kai nake yi wa duk ladubana,
Godiya nai gunka Allahna.

3. *Assalatu ma'assalamullah*,
*Rabbana* qarawa *Nurullah*,
*Alihi* da *Sahabu ibadullah*,
Ka haxa har da shehunai guna.

4. Allah yarda da mataye,
'Ya'yan Manzo da su tagwaye,
Jikokin Xaha sun fi ko waye,
Ke da isa gun Habibina.

5. Yardarka haxa da Shaikh Tijjani,
Har da Abdulqadiri Atjilani,
Na sa Inyasi *Gausi* na zamani,
Shehu Burhama ina qauna.

6. Gaisuwa zan yi wa manyan nan.
Wanda ake kira sahabban nan,
*Khulafa'urrashidi*nan nan,
Sun kashe *Kuffaru* mai varna.

7. Ya Abubakari a gai da ka,

Don Hadisi ne ya nuna ka,
Da xa Manzo bayan mai Makka,
Kai za a saka *Imamina.*

8. Umarul Faruk ina sanka,
Na jiyon qissar adalcinka,
Ya kamata a ce in wasa ka,
Tun da kai mulkin da ba varna.

9. Sannu mai haquri da kunyar nan,
Sayyadina Usmanun nan,
Sirikin Manzo Habibun nan,
Gun Allah wanda na fi qauna.

10. *Karamallah* ya *Waliyullah*,
Ya Aliyu ya *Wajiyullah*,
Gai da kai dodon *Aduwullah*,
Kai kake yi wa kafirai varna.

11. Ya yi kiransa zuwa sama ne,
Don ya nuna masa aya ne,
Irin bautar da Mala'iku ne,
Ke yi gun Sarki na *Ilahuna.*

12. Yabon Manzo a yau zan je,
Bege nasa za na je a guje,
Rabbana lamintamin na je,
Nai ta rera yabo ga *Imamina.*

13. Ya gano *Aljanna* tabbas ce,
An ni'imtar *Aljannahaqqu* ce,
Wanda ya yi aiki da ya dace,
A ciki zai je ya yi zazzauna.

14. An nuna mai wuta ga ta,
Ya gani har an ka fassarta,
Wanda za a saka cikinta,
Idan ya zam aikinsa yai varna.

15. Ya fitar da ruwa a yatsunsa,
Xaha ba famfo ba ne gunsa,

Ba mita babu dam a jikinsa,
Isarsa ka kawai a gun Sarkina.

16. Duk halitta wa aka ba wannan,
Annabawa da *Mussalan* nan,
Duk ciki nasu babu mai wannan,
Sai xan Abdullah da Amina.

17. Kai kamarka ba za a samu ba,
Matsayinka ba za a qara ba,
Kai kaxai ne Annabi babba,
Jagora kuma *Miftahul Janna*.

18. Wai ina mai san *Rasulullah*,
Na ce musu *La'ilaha 'illallah*,
Sai ya ce Manzo *Rasulullah,*
Ladansa yana wurin Allah.

19. Sai mai son Manzo muke nema,
Wanda ke qinai muke qyama,
Tun a nan duniya yake rama,
Kan ya je shi wuta a qoqqona.

20. Tsarkakkake mai cikar tsafta,
Hali nasa babu mugunta,
Kai nake wa yabo na nanata,
Qaunarka ta cikan raina.

21. Ni a nan ne zana taqaita,
Ko in ce nan Sani zan huta,
A yabon Manzo da na rubuta,
Na karanta don bayyana qauna.

Tamat

**WAQA TA BAKWAI**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**

**'Abin Koyi'**

**Amshi:** Abin so abin Koyi Muhammadu Rasulillah

1. A gun Malamai na ji wani bayani,
Suka ce ayyuka ai ba sa muni,
Idan an kira *Arrahamani*,
To don haka ni ma Sani na sanya*Bismillah*.

2. Da sunanka Allah zana fara,
Nake addu'ar ka daxan basira,
Na shiryo yabon Manzo na rera,
Allah gareka nake nema ka qaran yawan falala.

3. Allah dukkan arziki na nan gareka,
Kana ba da kyauta ba a ba ka,
Don haka na yi sujjada gareka,
Daxa min basira zan yabon Annabin Allah.

4. Da tsiranka da aminci *Karimu,*
Ka qara wa jagoran cikinmu,
Wanda ka bai wa Kur'anin *Karimu*,
Ka zave shi a halitta ya zam Annabi Allah.

5.*Aminci* haxa *ahalin* gidansa,
Da mata dan 'ya'yan gidansa,
Haxa Shabbansa masu hidima gurinsa,
Ko'ina suna bisa don qaunarsu gun Annabin Allah.

6. *Imamul imamul Mursalina*,
*Karimi* abin ko yi gurina,
Babu tamkarka mai Makka mai Madina,
*Sayyadul Mursalina Rasulillah* Ahmad mijin Ramla.

7. Biyayya ga Annabi wajibi ce,

Idan ka bi Annabi za ka dace,
Domin na ji har Allah ya ce
Muslumi mu bi Allah a bi Xaha Manzo Rasulillah.
8. Idan ka bi Annabi ka yi *mubai'a*,
A nan Lahira ka tafka sa'a,
Domin za ka sadu da masu xa'a,
Su ne Sahabbai Shahidai har da duk *Auliya'ullah*.

9. Dukkan xan'adam da akwai gwaninsa,
Amma nawa gwani shi ne ba kamarsa,
Muhammad Rasulu na san ba kamarsa,
Ka faxa ka qara *Habibi* ya fi komai a gun Allah.

10. Bara in faxa maka don ka gane,
Ka sani a komai ma'aiki shugaba ne,
Babu tamkarsa bai da kwatan-kwacinsa,
Haqiqa *Imami* ya fi komai da a gun Allah.

11. Muhammadu mafi darajar cikinmu,
Muhammadu mafi kyawun cikinmu,
Muhammadu mafi taqawar cikinmu,
Annabi muhammadu ne rahama halittu *Rasullah.*

12. Mafi martaba ga kyan xabi'a,
Kusanci ga Allah bai da sa'a,
Wajabci gare mu mu yi masa xa'a,
Dukkan wanda ya qi Muhammadu zai sha baqar wahala.

13. Da qaunarka bayi ke rabauta,
Saboda kai ne rahamar halitta,
Gare ka Allah zai ba da tuta,
*Sahibul Liwa'il Hamdu* Muhammad *Rasulullah*.

14. Dukkan wanda yak koma ga Allah,
A zuciya tasa bason Rasula,
A nan za ya san ya tarki matsala,
Za ya sha azabar Allah taqin Annabin Allah.

15. Allah na son mai son Annabi,
Masoyin ma'aiki bai da aibi,

A gurin Allah don son *Habibi*,
*Ilahi* daxa mana son *Karimi* mijin Ramla.

16. Mafi halitta kyawu da tsafta,
Mafi halitta kirki da kyauta,
Mafi halitta *taqawa* da vauta,
Dukkan ibada ko yi ake yi da Abdullah.

17. Tamat a nan nake nufin na huta,
A yan baitukan da na yo na furta,
Na bege ga jagoran halitta,
*Ilahi* ka karvi yabon da nai wa *Rasulillah.*

18. Sunan mai yin wannan qasida,
Sani Abubakari mai qasida,
Mai son ya cika da kalmar Shahada,
Xan Hotoron da Kawo masoyin *Rasulillah.*

Tamat

**WAQA TA TAKWAS**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
***'Waqar Isra'i'***

**Amshi**: Ba Wata Soyayya Mai Tsarki sai Wacce Allahna ya ke yi wa
Ma'aiki shi ne Dalilin *Isra'i* sai Sallah

1.*Arrahamani Rahim Lamyalid*kai ba ka haifa ba,
Sannan ba mata a gareka Allah balle ka yi uba,
Allah ba ka da kishiya ko qani fa ni na dudduba,
Ba farkon Allah Ahadin gwani Sarki Allah.

2. Qara salatinka ya *Rabbi* ba ma yankewa,
Gun babban bawa Muhammadu Sarkin kyawawa,
Vauta gun Allah wallahi shi yai koyawa,
Gai da mijin Aisha baba ga Zainab Sallalah.

3. Sa da sahabansa masu qauna ga yin ladabi,
Tsantsar koyi da shi wallahi sunnarsa suke bi,
Sun taimaka masa wajen yaxa addinin Rabba,
Sun ba da jininsu dukiyarsu domin bin Allah.

4. Soyayya tsantsa shi ne dalilin tafiyar *Isara'i,*
Sai karvo sallah shi ma dalilin tafiyar *Isara'i,*
Don duk Annabawa da Mirsalai ba wanda ya yi,
Sai dai Muhammadu cikakken masoyin gun Allah.

5. Shi *Isra'in* nan da Allah ya yi da Manzo ne,
Ai da jikinsa ne har ma da ransa ku gaggane,
Yai tafiya ta dare mai sauri domin masoyi ne,
Allah ne ya faxa ayar tana nan ba illah.

6. Zan dawo baya na fassara muku zancena,
Tsantsar soyayya dalili na farko zan zana,
An yi da Manzo ne *Isra'i* sha xaya dangina,
Shekara ta baqin ciki ake kiranta *ibadullah.*

7. Wannan shekarar Abu Xalibi ya mutu shi ma,
Sai kuma matarsa mai baiwa Nana Khadija ma,
Dukkansu biyu nan sun so shi Manzon alfarma,
Sai Rabbi ya xauke su manyan masoyan *Habibullah*.

8. Wannan dalili ma ya sanya an yi kiransa sama,
Domin rarrashinsa ga masoyi Manzon alfarma,
Sannan da nuna masa hallitu masu ibada ma,
Ko da mutun da Aljan ba sa yin bautar *Jallalah.*

9. Fifikon Manzo da dukkan *khalqi* za ku ji ma,
Annabi Musa ma magana ce yai da Allah ma,
Annabi Isa ko *ruhi* ne na Allah kuma dama,
Sai Annabi Ibrahim *Khalili* ne mai yin Sallah.

10. Duk *Mursalai* da Annabawa ba su kai shi ba,
Wannan soyayya dalili ce in kuka ma duba,
Tsantsar so ne Allah ya kai shi sama gaba,
Har qarshen-qarshen magayar tuqewa *Ibadullah.*

11. Dukkan Annabawa a qasa sukan yi *munajati*,
Ko dai mafarki ne ko wahayi mai daxin sauti,
Ba wanda a cikinsu ya qeta sama'u cikin sati,
Sai zavin Allah Muhammadu *Hamidu Sirril Jallalah*.

12. Zan dawo magana ta biyun fa ai *Isra'i* ne,
*Wal mi'irajin* tafiyar da Annabi yai yi ne,
Allah ya tabbatar tafiyar da bawansa *Sama'u* ne,
Don a cikin fa dare Manzo ya je gun Sarki *Jallalah*.

13. Shi *Isra'i* nan da Manzo Allah ya yi kuwa,
Da jikinsa ne da ransa mai kyawun nutsuwa,
Sannan a farke ne ba wai mafarki ne fa kuwa,
Fahimtar Ibn Abbas ni ma ita ce na xauka *Ibadullah*.

14.Ya je ya dawo shimfixar sa ma ba ta huce ba,
Domin har da xumi da take duk in an dudduba,
Gidan Umma ne Ummahani mai kyawun *haiba,*

Sai Jibrilu ya zo shi ya kwankwasa wa *Rasullalah*.

15. Sai Nana Faxima ta leqo dan ta ga ma waye,
Ta ga Jibrilu ne masoyin kaka da tagwaye,
Cikin tsafta da taguwar nan mai sawaye,
Sannan Manzonmu sai ya fito ya *Aminullah*.

16. Bayan ya hau ta *Baitil Muqasdas* can suka je,
Shi ne ya yi Sallah da Annabawa ma sun je,
Yai musu addu'a Manzo mai kyawun saje,
Sai suka tsallaka can *Sama'u* domin kiran Allah.

17. Ya tafi *Mi'iraji* Manzo na Xaha *Rasulullah*,
Ya qeta sama'u ta xaya har ta bakwai jimla,
Ya ga Mala'iku runduna ta Allah Sarki *Jalalla*,
Har da wasu Nabiyai na Allah kun ji *Siraxillah*.

18. Ga Annabi Adamu ga Musa har Ibrahim ma,
Annabi Yahaya sannan da Mala'iku su ma,
Ya yi musu Sallah ma *Rasulu* baba gun Umma,
Ya shiga *Aljanna* ya ga wuta Manzo *Shafi'ullah*.

19. Don in taqaita ma Jibrilu sai da ya tsaya ma
Ya ce wa *Rasulullah Habibullah* mafi girma,
Soyayyar Allah da kai Shafi'u masoyi ma,
Babu irin taka Balle gabanka *Habibu Aminullah.*

20. Manzo ya ga Allah wannan fahimta ina kanta,
Sun yi kusanci ma kusanci ba ya fa kwatanta,
Ya je *Al'arsh*i ya zauna baba a gun su Binta,
Sun yi dukkan sirri Manzo da Sarki Allah *Jallallah*.

21. Sai vangaren qarshe wato na karvo sallah ma,
Domin muhimmancin sallah a gurin Allah ma,
Sai da ya neme shi masoyi Manzon alfarma,
Shi ne ya girmama shi da sallah kun ji *Ibadullah*.

22. Domin girmanta Manzo *sama'u* ya karvo ta,
Sallah in ka duba sunan *Rasulu* aka rubuta,

Domin soyayya da Allahu ya ke yi fahimta,
Ya fifita shi sannan ba ya shi fa Xaha *Rasulullah*.

23. Wannan girma ne sallah kun ji fa abokaina,
Kar mi ta wasa da sallah kun ji fa masoyana,
Don ko can a lahira Muslim ma ba ya kuna,
Domin a jikinsa siffar jiki ce ta *Habibu Rasulullah*.

24. Wannan soyayya ita ce na ce mai tsarki ce,
Allah ya so shi ya girmama shi da ma zance,
Sannan ya gan shi kusanci ya wuce kwatance,
Nan ya tsarkake Allah inda ya ce *Attahiyatu Ibadullah*.

25. Ni ne Sanin xan Abubakar mai bin Allah,
Baba ga Usaini Hassan ga kuma Abdullah,
Hotoro gidana Walawai masoya *Rasulillah*,
Allah ka saka wa malam Abdullahi Yasayyadi jimla.

Tamat

**WAQA TA TARA**
**Marubuci Sani Abubakar Hotoro**
**“Mai Kur'ani”**

**Amshi:** Rasulu kai aka ba Qur’ani

1. *Bismilla* ni zan fara,
   Na yi kiran Sarki Allah *Rabbani*.

2. Da farko waqar nai *ta'awizi*,
   Ina neman tsarin Shaixani.

3. Sarkin da ba shi da xa ko,
   Mata balle ta haifi Usaini.

4. *Tabara* Allah shi ya kaxaita,
   Cikin *Zati* Allah *Rabbani*.

5. Sannan Allah shi ya kaxaita,
   Cikin siffar Allah *Rahmani*.

6. Wallahi Allah shi ya kaxaita,
   Cikin aiki Allah *Rabbani*.

7. Allah Salati har *Taslimi*,
   Qara gurin sirrin *Rabbani*.

8. Ma'ana Muhammadu *Rasulullahi*,
   Kakan gun Ahmad Tijjani.

9. Haxa matansa da 'ya'yansa,
   Da jikoki irin su Husaini.

10. Allah ka daxa min *ilhama*,
    Yau ma na sako wani launi.

11. Bege zan yi wa zavavvanka,
Maxaukaki *Sahibul Burhani*.

12. Wanda ka ba wa dukkan yardarka,
Ya xara komai ba ruxani.

13. Ba kokwanto ba jayayya,
Annabi ne *Sayyadil Saqalaini*.

14.*Assalamu'alaika* Muhammadu,
Ya Sirrin Allah *Rabbani*.

15. Kai aka ba ceto ga Sallah,
Ga *Kausara* kuma ga *Kur'ani*.

16. Dukkan halitta na bayanka,
Maza mata da su *Insu* da *Jinni*.

17. Annabi Musa shi aka bai wa,
*Attaura* na ji har a bayani.

18. Annabi Isa shi aka bai wa,
*Injila* na ji har a bayani.

19. Annabi Dauda shi aka bai wa,
*Zabbura* na ji har a bayani.

20. Amma Muhammadu *Rasulillahi*,
Ya zarce su an ba shi *Qur'ani.*

21. Kai ne dalilin duk *alkhairi,*
Duk ilimi na cikin *Qur'ani*.

22. Abin da zai zo da wanda ya fake,
Akwai bayaninsu a *Alkur'ani*.

23. Hani da umarni daga Allah,
An tattara a cikin *Qur'ani*.

24. Sakamakon daxi da azaba,

Akwai bayaninsu Qur'ani.

25.Duk ilimi Allah ya tare,
Ya dunqule su a *Alqur'ani*.

26. Allah don matsayin Manzanka,
Allah bar mu da *Alqur'ani*.

27. Allah don darajar Manzanka,
Ka da ka rabamu da *Alkur'ani*.

28. Tamat a nan ne zan dasa aya,
Cikin *qasidar* Mai Kur'ani.

29. Wanda ya shirya yabon da *qasida*,
Xa ga Abubakari ne Sani.

30. Ina Kano a garin Hotoro,
Gari na mahaddatan *Kur'ani*.

31. Gari na mahaddatan *kur'ani,*
Ga zikirin Allah *Rahamani.*

33. Allah saka wa 'iyayenmu,
Da malamai masu *Alkur'ani*.

Tamat